[04/03 13:39] MRS SADAUKI: *SHAUKIN SO*💘

```LoVe story```💟

By
Chamsiya Laouali Rabo
{MRS SADAUKI💫✍️}

*FCWA*☀️

---

Ina yi wa ɗaukacin musulmi Barka da sallah, Allah ya karɓi ibadunmu ya kuma gafarta mana kurakuranmu Amen !!!

Page 1-2

Sanyin la'asar ne ya sauka ya haɗe da sanyayyar iskar da ke kaɗawa, giza-gizai na gudu hadari sai gangamuwa yake yayinda garin sai ƙara lumshewa yake yana ƙara duhu.
Mutane sai harhaɗa kaya suke suna guduwa,abubuwan hawa na ta wucewa kowa na ƙoƙarin ƙarasawa gida kafin ruwa su sauko saɓanin malam Nur da ya ƙara gyara zama akan kujerarsa sai ci gaba da koyar da karatu yake ba tare da yayi la'akari da yadda Ɗalibai sai leƙen waje suke ta manyan tagogin ajin ba.

Cikin dadaɗar muryarsa yake rero ƙira'a mai shiga rai da ɓargon jiki amman sam Ɗaliban hankalinsu bai wajensa.
Lura da hakan yasa shi rufe Qur'anin yana fuskantar su "ku nutsu in kuna nutsuwa don babu wacce za ta fita sai ta biya min wannan shafin tom"ya faɗa yana tamke fuska tamau alamun babu wasa a ciki,sanin halin malam Nur yasa duk suka shiga hankalin su duk da ya kasance mai barkwanci amman wani sa'in ya kan rikiɗe ya koma miskilin malami ta yadda ko ƙwaƙwaran motsi mutum bai yi in yana cikin aji musamman lokacin karatu.

Karatu suka ci gaba da yi cikin nutsuwa suna koyon yanayin yadda duk yake lanƙwasa ƙira'arsa wanda hakan ba ƙaramin dadɗi yake wa malam Nur ba.
Tun da aka fara karatun yana lura da ita yadda ta takure wuri guda sai ƙanƙame jikinta take
```

alamun jin sanyi duk da tana cikin ƙaton hijabi.Zuciyarsa ce ta fara rawa,tausayinta ya tsargu a ransa cikin hikima ya sallami ɗalibai cike da murna suka fara fita aji duk yana kallonta har lokacin da ƙawarta Samira ta kama hannunta suka fice.

Lumshe ido yayi yana sauraren bugun zuciyarsa,tunda ya sanyo ƙafa makarantar nan ƴan mata suka fara rubibin shi daga masu nuna alamar suna son shi sai masu turo masa saƙo amman ita ko kallon shi bai dame ta ba.
Buɗe ido yayi jin ƙarar saukar ruwan,miƙewa yayi ya buɗe window yana leƙawa yayafi ne ake amman masu zowa da gudun nan.

Cikin zuciyar shi ya ke tambaya 'shin ko har ta kai gida?'dan ya ga alamu bata son sanyi sosai,huci ya sauke kafin ya ɗauki makulin motarsa ya fito.

Filin makarantar tsit yake dan dama duk sauran malumai sun daɗe da tashi ajinsa  ne wanda ya kasance ajin ƙarshe(na manya ga ba ɗaya)kawai ya tsayar da su.
Ƴar ƙaramar ƙofa yabi ya fita inda yayi parking ya nufa ya shige tare da yi ma motar key bai tsaya ko ina ba sai bakin tangamemen get ɗin gidansu ,horn yayi mai gadi ya buɗe ya shige.
Tun kafin ya shiga falon yake jin ƙarar sauti na tashi,cak ya tsaya yana kallon su yadda suke rawa tamkar ƴaƴan makaɗa sam ba su lura da shi ba sai sauka wayar caza suka ji ,ihu suka fara suna neman agaji amman ƙarar tv ta hana aji sai da yayi masu lilis sannan ya ƙyale su tare da kashe tv.Sai kuma a lokacin Maman ta sauko tana hararen su kafin ta tsayar da malam Nur da ke ƙoƙarin buɗe ɗakinsa"Ustaz sai yanzu ka dawo tun ɗazu nake ta tsimayen ganin ka"tsayawa yayi jin muryar mahaifiyarsa,gaishe ta yayi sannan ya ƙara da "eh Maman shigowata kenan kuma sai na tarar da waɗan can maras hankalin suna shaƙiyanci duk da sun san sun yi laifi na ƙin zuwa makaranta shine suka ƙara da wani laifin"ya ƙarashe maganar yana ƙyaci alamun jin zafi abun.

Inda suke a rakuɓe Maman ta kalla tace "ku tashi ku fice min da gani in ba shashanci ba ana ruwa zaku saka kiɗa maimakon karatun Alkur'ani,ai Ustaz in ka biye ta waɗannan sai su hauda maka hawan jini"tana gama rufe baki suka miƙe cikin azama suka shige ɗakinsu.

Ƙarasowa yayi kusa da mahaifiyar tasa yana kallon ƙullin maganin da ke hannunta,miƙa masa ta yi ya karɓa tare da dubanta yace "na me ne kuma wannan?"
"Cikin ruwan wanka za ka zuba shi sannan ka kaɗa cikin madara ka sha,dan Allah kar ka ce min a'a ko tambayata ba'asi"shiru yayi yana nazarin maganar kafin yace "toh maman in shaa Allah zan yi yadda kika ce"da murmushi Maman ta dafa kansa tace "Allah yayi maka albarka ya cika maka burinka na alkairi"da "Amen"ya amsa kafin ya wuce part ɗinsa ita kuma Maman ta shiga kitchen.

Sanin darajar mahaifiya da girman alƙawari shi yasa Ustaz yin amfani da maganin ba tare da ya san ko na mine ne ba,abinda ya sani dai uwa ba za ta taɓa cutar da Ɗanta ba.
Yana fitowa daga wanka ya saka doguwar jallabiya fara sol ya kunna ƙira'a a Sheikh Sudais yayinda kuma yake yin tasbihi da hannunsa,idonsa a lumshe suke yana jin sautin ƙira'ar na ratsa shi gefe guda kuma tunanin Nazifa ne maƙale a zuciyarsa sai dai da zarar ya fara sai ya yakice ta a rai kasancewar yau Litinin yana ɗauke da azumi a bakinsa.

Kiran sallah da wayarsa ta ɗauka ne ya sa shi saurin miƙewa ya ɗauro alwala ya fito falo inda kayan buɗa bakinsa ke jiran shi.Kamar kullum yau ma Maman ta ƙayata ɗan ƙaramin capet ɗin da yake zama lokacin shan ruwa da kayan ciye-ciye.
Zaunawa yayi akai tare da tanƙwashe ƙafafunsa addu'o'in  shi na yau da kullum ya fara kafin ya gabatar da buɗe bakin.
Sanyayar ajiyar zuciya yayi lokacin da ya kwankwaɗi jus ɗinsa na zoɓo wanda ya sha kayan haɗi,wani jus ɗin ya ƙara tsiyayawa a kofi ya ɗan saka maganin da maman ta basa ya motse sannan ya shanye.

Ruwan saman da ake ne suka ɗan tsagaita wanda ya bai wa musulmai maza fitowa yin Sallah magrib,duk da an yi ruwa masallacin cike yake da jama'a su Ustaz sune a sawun gaba kamar kullum.
Sai bayan an gama sallah ne ya gaida mahaifin nasa  wanda mafi akasari shi ke jan sallah magrib, isha'i da asubah.Cike da kulawa Baba ya amsa yana tambayar shi wunin ɗinsa"alhamdullah Baba ya gajiya ?"cewar malam Nur,a takaice Baba ya amsa mashi da "alhamdullah"kafin suke rankayowa gida.

Ko da suka zo gida sun tarar da Maman da ƴan matanta suna cin abinci,hararar su Nur yayi yana amsa barka da shan ruwan da Maman ke masa kafin ya wuce part ɗinsa.

Ƙaton hoton  ya ƙura ma ido yadda take murmushi gwanin kyau sai ta banbanta da sauran Ɗaliban da alamu ita bata ma san an ɗauki hoton ba,daidai fuskarta ya shafa ya na mai dafe saitin zuciyasa.

★
A ɓangaren Nazifa kuwa tun zuwanta gida ta duƙunƙune cikin bargo tana hawayen azaba

yayinda ƴan gidansu suka yi cirko-cirko suna jajanta ma juna game da ciwon Nazifa wanda sai gaba yake babu sauƙi.

Inna ce ta ƙarasa kusa da ita ta yaye bargon tana mai taɓa wuyanta,rau yake sai ɗan karen zafi kamar garwashi haƙoranta kuwa sai karkar suke suna gamuwa.Cikin tausayi Inna ta dubi yaya Ɗalhat tace "ko asibiti muke zuwa? Tunda maganin ya ƙi yi mata aiki" ajiyar zuciya ya sauke yace "toh Inna mu je can ɗin amman ba zuwan ba kar mu je su tsuIa mana kuɗi"murya na rawa Inna tace "a'a ai asibitin gwamnati za mu je tunda can kuɗin cirar takarda kawai za mu biya,je ka taro mana ɗan sahu "da sauri Ɗalhat ya fita ba jimawa sai ga shi ya dawo duk ya jiƙe da ruwa,kamar wata gawa haka ya naɗota cikin bargo tare da sungumarta ya shigar da ita adaidaita.Gaba ya shiga ita kuma Inna ta zauna baya tare da Nazifa ,CSI Ali Shaibu ɗan sahun ya kai su kamar yadda suka buƙata.

Adaidaitar na tsayawa Ɗalhat ya fito zai ɗaukar ta cikin murya maras lafiya tace "zan iya tafiya da kaina"taimaka mata yayi yana tattare bargon suka nufi ciki,Inna na ƙoƙarin kwance kuɗi ta sallami mai ɗan sahu yace ta bari godiya ta yi masa tana masu mara masu  Ɗalhat baya.

Inna na shiga ta tarar da Ɗalhat sai faman faɗa yake da wata nurse akan tace doli sai ya tafi ya karɓo takarda shi kuma yace ta dubata kafin ya dawo shine tace taƙi ta yi ɗin.
Cikin alamun a tausaya masu Inna tace "ƴata ki taimaka ki duba ta don haihuwar da iyayenki suka yi maki,mai rubuta takardar  kamar na ga ƙofar shi a rufe"a zafafe nurse ɗin tace "sai ku jira har ya dawo ko kuma ku canza asibiti...."Bashir ne yayi saurin katse ta wanda shi ma likita ne yace "haba Rakiya ba ki ganin halin da take ciki ne?Kuma dan tsufan wannan ai kin taimaka"ya ƙarashe maganar yana mai juyawa inda Ɗalhat ke tsaye yace "me ke damun ta?"cike da jin daɗin hallacin da yayi masu ya shiga yi masa bayani "eh to duk in an yi ruwa ne ko kuma lokacin sanyi sai jikinta ya rinƙa ciwo tana jin sanyi"kai Bashir ke ɗagawa kafin ya ɗibi jininta ya kai lab cikin ɗan lokaci ya dawo da fara takarda,sai da ya naɗe lemar (parapluie) sannan yayi mata allura.

Inna da Ɗalhat na gefe sai godiya suke zuba masa, murmushi kawai Bashir yayi yace "ba komiy ai yi wa kai ne".

Barci mai nauyi ta samu sai fitar da gumu take tana sauke ajiyar zuciya,gefen gado Inna ta zauna yayinda Ɗalhat ya bi bayan Bashir dan karɓo magani.

Sai bayan sallah isha'i suka dawo gida,cike da mamaki Jamila ƙanwarta ke kallonta ganin ta warke lokaci guda cikin kasa ɓoye mamakinta tace "anty kamar ba ke ce aka fita da ke a duƙunƙune ba ya jikin naki ?"

"Da sauƙi na ma warke yunwa nake ji me kika dafa?"
"Dafa duka ta shinkafa"ta bata amsa ta na mai ɗaukar kwano ta zubo mata,ba wani ci ta yi sosai ba ta tashi ta yi alwala da ruwan zafi ta gabatar da sallah da ake binta.

Lamo ta yi kan sallaya fuskar malam Nur na yi mata gizo, murmushi ta yi tuna lokacin da ya lura da ba cikin hayyacinta take ba duk sai ya ruɗe "sai yaushe zaka furta ne?"ba ta san a bayyane ta yi maganar ba sai jin Jamila tace "mi za'a furta?"yi ta yi kamar ba ta ji ta ba ta tashi ta haye katifar da suke kwana ta cigaba da tunanin malam Nur har barci ya ɗauke ta.

Ƙarfe bakwai cicif a makaranta tayi ma malam Nur,tun kafin ya ƙaraso ajin yake jin sautin muryarta sai karatu take cikin nutsuwa tare da ba ko wane harafi haƙinsa.
Bakin window ya tsaya yana ƙare mata kallo,sanye take da hijab da sket na uniforme ɗin makaranta hannunta riƙe da al'ƙur'ani amman ta rufe shi alamu hadda ce take.Idonta a lumshe suke yayinda ɗan ƙaramin bakinta wanda ya sha janbaki sai motsawa yake yana fitar da dadaɗan amo na muryarta.

A hankali ta buɗe su kuma,ido biyu suka yi a tare zukatansu suka buga dam,cikin i'ina tace "as..salamu aleyka yaa mu'alim"sai da ya ƙarasa shigowa cikin ajin sannan ya amsa sallama yana mai tambayar ta "ba ki jin tsoro ne kullum ke kike fara zuwa makaranta ina ɗayar take?"wani daɗi Nazifa ta ji kafin tace "ta na gida sai zuwa ƙarfe takwas take zuwa"
"Ke kuma ba ki iya jiranta ko?"ɗan ɗagowa ta yi ta kalle shi tace "um..ai saboda na yi hadda ne nake zuwa da wuri"jinjina kai yayi ya karɓu alƙur'anin hannunta ya fara yi mata tambayoyi,sai ya jawo Aya yace ta ci gaba ko kuma ya tambaye ta cikin wace sura ce ita kuma ta na basa amsa.Sosai duka zukatan biyu suke jin daɗin wannan kusancin a haka har mutane suka fara taruwa sai dai babu wanda ya shigo aji sai leƙen su da ake wasu na gulmar dama soyayya suke.

Lokacin shiga aji yayi kowa ya shiga,nan Nazifa ta ji ta a takure ganin rabin ɗalibain ajin sai harararta ake yawancinsu duk masu son malam Nur ne.

"Ke miye haka?dan Allah ki saki jikinki duk kin wani takure kawai dan surutun mutane ba komai ba ne ke cindu sai baƙin cikin ganin kin samu abinda suke so shekara da shekaru"cewar Samira murmushi kawai Nazifa ta yi ba tare da tace komi ba domin tun ba yau ba ta fahimci ɗin suna son junansu ba tare da su sun sani ba,tun ba ta yarda da zancen Samira har ta yarda da lalle tana son Malam Nur.

Duk karatun da ake masu na yau sam ba ta fahimta  don rabin hankalinta yana can duniyar tunani,ƴar ƙarar rawar da aka kaɗa alamun lokacin shan iska yayi ne yasa ɗaliban fara fita dan karyawa,"Malama ki tashi mu tafi ko yau ba ki cin komai ?"ta tsinkayo murya Samira cikin masifa, murmushin da ya zame mata jiki ta yi tana mai miƙewa har sun kai bakin ƙofa suka ji malam Nur yace "Naziiii"cak ta tsaya zuciyarta ta shiga lugude kallon Samira ta yi da ido ,ita kuma ta yi mata alama da ta tafi tare da ɗaga mata gira kafin take ficewa.

A hankali ta dawo kamar wacce ƙwai ya fashe ma a ciki har ta zo gaban teburinsa  inda yake zaune a kujera ya ɗora hannuwansa akan table ɗin mai ɗauke da littafai.

"Ga ni mu'alim"ta faɗa kamar za ta yi kuka,bai ce mata komyi ba sai ma ƙoƙarin ciro wani littafi yake.
Turo baki ta yi gaba tana jin haushin shanyata da yayi har ta fara tunanin ko dai ba kiranta ba ne yayi sai kuma ta ji yana cewa "ya kamata ki ƙara da karatun wasu littattafai dIn ilimi yawa ne da shi ga waɗannan ki je da su gida ki yi nazari gobe za mu fara su"amsa ta yi ta juya za ta tafi yace "am...ban gama ba"tsayawa ta yi, jin bai ce komai yasa ta ɗago kanta karaf suka haɗa ido wani irin lantarki mai game da shock suka ji a tare da sauri ta mayar da kanta ƙasa.Murmushi yayi yace "ki na iya tafiya"kamar mai jira ta juya da sauri ta fara tafiya kamar wadda aka yi ma dabaibayi..........
[10/03 14:46] MRS SADAUKI: *SHAUKIN SO*💘

```LoVe story```💟

By
Chamsiya Laouali Rabo
{MRS SADAUKI💫✍️}

*FCWA*☀️

---

age 3-4

Tun daga nesa Samira ke ƙare mata kallo har ta ƙaraso,dungure mata kai ta yi tace "ƴar sa ido kallo me ne kike yi min?"dariya ta yi tace "to Naziiii ni kam mi zan kalla a nan,kawai na ga yau duk a takure kike kamar wata kaza da ƙwai ya fashewa a ciki haka kike tafiya tsaya ki ga na gwada miki ma.Kin ga yadda kike tafiya"Samira ta faɗa tana kwaikwayon tafiyar Nazifa "ke dai
```

kika sani uwar sa ido"shine abin da ta ce.

"Babu wani sa ido sai gaskiya,wai me ne yace miki?"ajiyar zuciya ta sauke ta gwada mata litattafan da ya bata "na mi ne ?"

"Karatu za mu rinƙa yi"jan baki Samira ta yi tace "sabon kiciyi..."wani dundu Nazifa ta kai mata a baya cikin jin haushin furucin tace "Noori ɗin ne kike ce ma kiciyi?"amsa ta bata da "eh ɗin in ba kiciyi ba me ne na wani kame-kame ai sai ya fito fili yace maki yana son ki ba ya fake da koyar da ke ba"kamar daga sama suka tsinkayo murya malam Nur yana cewa "in kun gama gulmata sai ku shiga aji"da mugun tsoro duk suka juyo sai dai tuni ya wuce sai bayansa suka hango.

Sai da Nazifa ta sayi taiba suka wuce aji,a gaggauce ta shanye taibar ta ɗauki ruwa tana sha ita kuma Samira sai aukin kallonta take.

"Lafiya ko na sauya maki ne?"Nazifa ta tambaya "a'a ko ɗaya kawai na ga kina shirin zautar da malaminmu ne,har fah zai shigo ko da ya ga ki na cin abinci ya koma na san jira yake har ki gama"waro ido Nazifa ta yi sai kuma ta ƙyale ganin malam Jabeer ya shigo aji da alamu kuma shi zai masu karatu.

Rubutu ya fara a allo sannan ya juyo ya fara tambayoyin akan karatun da ya gabata su kuma ɗaliban na bashi amsa,cike da ƙwarewa ya shiga yi masu bayani muhimmancin amana da gaskiya suna tsaka da karatu malam Nur ya shigo ya zauna shi ma ya na sauraren jawabin malam Jabeer.

Ko da aka tashi tsayar da ita yayi ya ɗan mata tambayoyi bisa karatun da aka yi inda ba ta gane ba ya sake yi mata bayani har ta fahimta daga nan ya fara jan ta da hira har yake tambayar mene ne ya sameta jiya nan ta faɗa masa tana fama da sikila ne cikin tausayi yace "me yasa ba ki je asibiti ba?"

"Mun je mana har suka bani magani"
"Wace asibiti kuka je?"ya tambaye ta "CSI Ali Shaibu"ta basa amsa "ki rasa asibitin da za ki je sai wannan?"ɗan kallon shi ta yi a raunace sai kuma ta mayar da kanta ƙasa tana wasa da yatsun hannunta,wani gwabron numfashi ya sauke da ya tuna ba kowa ne ke da halin zuwa asibitin kuɗi ba.

"Ina ne gidanku?" ya tambaye ta yana mai tsare ta da idanu,ba ta yi zaton haka ba amma har ƙasan ranta ta ji tambayar " nan ne kusa ba nisa wajen gidan Alhaji mai tumaki"ta basa amsa

"To daga nan ina za ayi aje?"
"Ai makwabtanmu ne daga gidansa sai namu"kai ya jinjina kafin yace "ok wuce ki tafi Samira na jiran ki Allah kauwo afuwa"da "Amen "ta amsa kafin su fito tare.

Turus suka yi ganin Samira da malam Jabeer sai hirar su suke cikin kwanciyar hankali,"ya dai kun gama karatun?"cewar Samira tana kallon su "a'a ba mu gama ba"Nazifa ta bata amsa tana hararenta.
Dariya malam Jabeer yayi yace "haba abun har da baƙar magana?"

"Eh ai ku kuka fara"malam Nur ya basa amsa nan dai suka yi sallama suka yo gida.

Tun daga wannan lokacin wata shaƙuwa mai game da ƙauna ta shiga tsakanin malam Nur da Nazifa,Samira kuma da malam Jabeer.Wannan alaƙa ita ta ƙara danƙon abotar Nazifa da Samira sai ya zamana ko a gida kullum suna tare don Nazifa ba ta da waya da ta Samira ce take waya ita da malam Nur,babu yadda bai yi da ita ba akan ya saya mata waya amma fafur ta ƙi don ta san Ɗalhat zai iya dukan ta.

Cikin canjin da ya samu na nishaɗi ya kalli mahaifiyar tasa yace "Maman ki shirya kin kusa samun ƴa "yayi maganar yana mai sunne kai alamun jin kunya,cike da murna Maman tace "kaiiii haba?Masha Allah yaushe za a kawo min ita na gan ta?"ƙeya ya ɗan sosai gafin yace "nan ba da jimawa ba ke dai ki taya ni da addu'a"da sauri Maman tace "ai kullum cikin yin ta muke sai dai mu ƙara".

Tsuki Sappa ta ja tana zumɓuro baki gaba tace "haba Mama sai kace dai an yi maki  albishirin kujerar Makka sai wani daɗi kike ji mtwsss"baki buɗe Maman ke kallonta kafin tace "yanzu Sappa wannan ba abun murna ba ne? Tun yaushe nake jiran wannan ranar ta zo kuma shikenan ba zan yi murna ba?"ƙara turo baki Sappa ta yi tace "to ai sai ki bari ki ga yarinyar wa

ya sani ma ko ƴar talakawa ce..."wata irin tsawa ya daka mata jin ta taɓa martaba ruhinsa,da sauri Sappa ta miƙe ta nufi ɗaki don ta san ba ƙaramin aikinsa ba ne ya ƙara naɗa mata kashi dama har yanzu ba ta warke da bugun da yayi masu ita da Balkis ba.

Haƙuri Maman ta shiga ba shi tana cewa "dan Allah ka barta ƙurciya ce"

Zaunawa yayi yace "ba wata ƙurciya iskanci ne kawai haka ranar nan ta yi min wata banza wasiƙa ko yaushe aka haife ta ma da har za ta fara zancen soyayya"

"Soyayya???ita da wa?"Maman ta tambaya shiru yayi jin yayi suɓutar baki dan ko kaɗan bai so Maman ta gane da Sappa na sonsa,ganin ta ƙure shi da ido tana jiran amsa ya miƙe ya shiga wayar ƙarya.

Jikin Maman ne yayi sanyi ‘kar dai a ce Sappa son Ustaz take? Shine ta kasa faɗa min ta je ta faɗa masa’Mama ke maganar zuciya kafin ta miƙe ta nufi ɗakinsu Balkis,kwance ta tarar da ita tana kuka "ashhha! Yanzu Sappa kuka ne kike dama?me yasa tun farko ba ki gaya min kina son shi ba shine za ki wani shige ɗaki kina kuka?Maza tashi ki goge hawayenki gida ba ta ƙoshi ba ai ba za a baiwa dawa ba"cikin jin daɗi Sappa ta yi saurin miƙewa tana murna ta shiga toilet.

***Yamai

Wata tsohuwa ce zaune bisa tabarma sai mulmula dawo (fura) take gefe guda kuma wani ɗan yaro ne da ba zai wuce shekara shidda zuwa bakwai ba sai tankaɗa gari yake yana barbaɗa ma furar da take dunƙulewa ƴan mili-mili daidai na dala biyae.
Cikin gajiya da aikin yace "Kaka ki tashi mu tafi in mun je can sai ki ƙarasa mulmulewa"cike da kulawa ƴar tsohuwar tace "ah Tujani saurin me kake haka ne? Ka fi kowa sanin duk lokacin da za mu kaiwa gida dole a jira mu don furata ta tafi ta kowa duk kasuwar garin nan,ungo je ka karɓo ƙanƙara "ta basa ƙaton tarmus amsa yayi ya fice da gudu ba jimawa ya dawo ya tarar har ta jera kayan tallar.

Ɗan bokiti da nonon shanu ya ɗauka yayin da Kaka ta ɗauki ƙatuwar ƙwarya dawonta ta aza a kai,tarmus ɗin ƙanƙara kuma suka yi kama-kama.
Har sai da suka kai bakin ƙofa Kaka tace "mun tafi sai mun dawo"ƴar ƙwalla baƙin ciki Saude ta goge sannan tace "Allah ya tsare ya bada kasuwa, *Tajdeen* ka kula da kanka banda yawo"tana gama faɗi ta ɗauki *Haleematu* ta ja hannun *Ismaël* suka shige ɗaki.

Wata uwar ashar Kaka ta aika mata tace "yau na ga ƴar baƙin ciki ni da jikana ba ni da ikon tafiya talla da shi? To ta Allah ba taki ba mai farar ƙafa tun da Haliru ya auro ki ya tsiyace abincin da zaku ci ma sai na je na nemo maku dan talauci amman da yake butulu ce ke shine kike jin haushi don Tijani na taya ni talla..."cikin gajiya Tajdeen yace "Kaka mu tafi kika tsaya sai surutu kike sai codtumer ɗinmu sun yi fushi sun fasa saye"dariya Kaka ta yi tace "mu je ɗan jikallena ai uwar taku ce ta fiya mugunta"cikin jin haushi yace "ban so kar ki sake zagin Anya kin ga ba ta yi maki komai ba"

"To ni mz na yi mata da take hassadata?"

"Ita ba hassadar ki take ba kawai ba ta so ina zuwa talla so take na yi karatu na zama likita"ƙyaci Kaka ta yi suka ci gaba da tafiya har suka iso kasuwa dama babu wani nisa.

Tun kafin su zauna costomer suka fara zuwa,cikin ɗan ƙanƙanen lokaci Kaka ta fara ciniki dan har ta kusa sayarwa sai habaici take yi ma sauran ƴan fura-fura sanin hali yasa babu wacce ta tankata.

Wani mai mota ne ya parker kusan kullum sai ya zo sayen fura wani bi anan ake dama masa ya sha wata rana kuma ya tafi da kayarsa.
Washe baki Kaka ta yi tana amsa sallamar da yayi dan ba ƙaramin burge ta mutumen yake ba saboda in ya sayi fura sai yace ta riƙe canji ta sayawa jikanta wani abu.Shi kansa Tajdeen sosai yake son mutumen wanda yace sunan shi Omar.

2000 ya bada yace a dama masa fura  asa madara da suga,fura Kaka ta shiga damawa yayin da Tajdeen ya tafi sawo madara da suga.Bayan ta gama ta miƙa ma Tajdeen ya kai masa cikin mota,ɗaya gefen ya buɗe masa sannan ya karɓi roba da aka zuba furar.
Ƙatuwar wayarsa ya ba Tajdeen yana game sai dariya yake,sai da ya sha ya ƙoshi ya bashi sauran ya shanye.

Yamma lis su Kaka suka shigo,sannu da zuwa Baffa yayi mata ta amsa tana mai cewa "yawwa ga cefanen gobe nan shinkafa da wake za ayi mana da rana da dare kuma ayi tuwon laushi, tunda ni ke kawo cefane ai sai abinda nake so"Baffa dai bai ce komai ba sai ƙwala wa Saude kira da yayi.

"Sannu da zuwa"Saude ta faɗa tana mai sunkuyar da kai "riƙe abarki bayan kin gama ci min mutumci ɗazu shine yanzu kike wani duƙe kai dan munafurci to ban so" kallon Kaka Baffa yayi yace "haba mama gaishe ki ne fah ta yi ai sai ki amsa kafin ki ɗora da faɗan"

"Na ƙi na amsa ɗin ina ce saboda Tijani ta yi min rashin kunya "cewar Kaka tana hararen Saude,gefen Tajdeen ta zauna ta shiga duba kayan wasar da Omar ya saya masa"Tijani wannan karon dai babu wanda zaka bai wa kayanka don ba zan bari ka rarraba su ga waɗanda uwarsu sam ba ta da mutumci"

Ɓata rai Tajdeen yayi yace "ai dai ƙannaina ne kuma nace maki ki bar zagin Anya (uwa) ban so"yadda yayi kicin-kicin da fuska yasa Kaka dungure masa kai tace "na ji ɗan gaban goshi uwar taka ce sai da haka".

Washe gari ta kama Monday kuma rana ce ta komawa school,tun asubah farin Anya ta yi ma Tajdeen wanka dan yau ne za a rubuta sunansa cikin jerin ɗalibai.
Murna fal ransa ganin an saka masa
sabbin kaya kuma za a kai shi makaranta,duban mahaifiyarsayayi wacce ita ma kallo guda za ka yi mata ka gane tana farin cikin haka a zuciyarta kuma murna take Tajdeen zai rabu da talla zai fara karatu

Kaka ce ta leƙo tana goge ƙwalla tace "dama ni tun tuni na san kin shanye Baffan yara,dan tsabar makirci shine kika saka shi ɗaki kika kitsa masa a kai Tijani makaranta dan baƙin ciki yiiii"Kaka ta ƙarashe tana rusa kuka da sauri Baffa ya shigo kafin ya kai da magana Kaka tace "in dai na isa da kai kar ka saki ka kai Tijani makaranta a bari har wata shekara duka-duka nawa yake?"da "toh" Baffa ya amsa yana ficewa daga gidan rai jagule dan sam mahaifiyarsa ba ta gyara masa kullum sai ta yi masa katsalandan cikin lamurran iyalansa.

Hannun Tajdeen Kaka ta ja suka nufi ɗakinta nan ta yi ta kwantar masa da hankali har da bashi

kuɗi abu ga yaro dandanan ya manta da wani son zuwa makaranta.

Lokacin zuwa talla na yi Kaka ta ɗauki ƙwarya dawo Tajdeen bokin nono kamar kullum suka nufi kasuwa.
Can nesa da inda Kaka ke saida fura Omar yayi parking ya fito waya maƙale da kunnensa ya jingina a jikin mota,da hannu yayi ma Tajdeen alama ya zo wanda tun tsayawar motar ya ƙure shi da ido da sauri ya miƙe ya nufe shi da murna.
Kuɗin furar da zai sha ya bashi da gudu ya kai ma Kaka nan ta bashi kuɗi ya sawo madara.
Ganin ya tafi yasa Omar shigewa mota yabi bayan shi, Tajdeen na tsaka da tafiya yaji oder tsayawa yayi da nufin mai motar ya wuce sai ya ga Omar ne.Seat ɗin gaba ya buɗe masa ya shige yana murna shi kuma Omar ya danna ma mota huta ya fara gudu babu ƙaƙautawa............
[10/03 15:05] MRS SADAUKI: *SHAUKIN SO*💘

```LoVe story```💟

By
Chamsiya Laouali Rabo
{MRS SADAUKI💫✍️}

*FCWA*☀️

---

Page 5-6

Cikin gajiya da gudun da suke Tajdeen ya dube shi yace "Uncle wai ina ne za mu je? Ka ga fah mu na wuce shaguna(kanti)inda ake sayar da madara"murmushi Omar yayi yace "kar ka damu wannan tafi ko wace kyau kuma ina son sawowa dayawa ne ta yadda kai ma kullum za ka rinƙa shan guda biyar a wuni ko ba ka so?"baki Tajdeen ya washe cike da murna yace "ina so mana amman ita Kaka ba za ka saya mata ba?"
"Zan saya mata mana har da duk ƴan gidanku"ya baa amsa,shiru Tajdeen yayi yana kallon hanya yadda garin Niamey ya tsaru kai kace ƙasar waje ne.
Barci ne ya kwashe Tajdeen tun yana sa ran tsayawa har ya gaji yayi lamo,yafi minti talatin yana barci sannan ya farka amman abun mamaki sai ya ga har yanzu motar gudu take kuma sun baro cikin gari har sun shigo daji.
Cikin alamun tsoro ya kalli Omar yayi narai-narai da ido yace "ka mayar da ni wurin Kaka "wani
```

banzan kallo Omar ya watsa masa wanda ya sa shi fashewa da kuka.Bai hana shi ba hakan yasa ya cigaba da rera shi yana kiran sunan Kaka,wata uwar tsawa ya daka ma shi yace "yi min shiru ko na jefar da kai waje Zaki ya cinyen naman jikinka"tsit Tajdeen yayi ya haɗiye sauran kukan sai hawaye kawai ke masa zuba.
Ana kiran sallah la'asar suka shiga Dosso,a wani ɗan ƙaramin gida yayi horn aka buɗe mashi.Hannun Tajdeen ya ja suka nufi ciki bayan ya parker mota,a falo suka zauna bayan wani lokaci sai ga wani Alhaji ya fito.Gaishe shi yayi cikin ladabi ya amsa yana kallon Tajdeen wanda idon shi suka ɗan faɗa saboda doguwar tafiya da suka yi.
"Mi sunan ka?"shine abinda alhajin ya tambaya,shiru yayi ya ƙi bashi amsa dan izuwa yanzu duk da ya ke yaro ya san ba sayen madara ba ne ya kawo su nan.

Wanka Omar ya shiga yayi kafin a gabatar ma shi da abinci,cikin plate ya zuba ma Tajdeen ya karɓa ya fara ci dan yunwa ya ke ji sosai.
Bayan sun gama ne ya karɓi saƙo gun alhajin sannan ya ja hannun Tajdeen suka nufi inda ya ajiye mota,titi ya hau nan ma ya shiga ba mota huta bai tsaya ba sai da dare yayi ya fiddo abinci suka ci suka kwana a cikin motar da gari ya waye kuma suka cigaba da tafiya.
Daidai maraba da baƙi ta maradi suka tsaya ya buga waya ba jimawa wani ya zo ya karɓi motar da suka tawo da ita,taxi ya tara aka ida shigowa da su cikin gari daga nan suka nufi tashar mota.

Motoci duk sun cika,har zai juya yaji wani mutum na waya yana cewa Jos zai tafi ai da sauri ya ƙarasa gun shi ya nemi alfarma in babu damuwa su tafi tare in ya so shi zai bada na mai,ba tare da wata matsala ba mutumen ya yarda.
Ƙatuwar mota ce irin wanda ake ma lodi,kujerar kusa da driver ya zauna tare da ɗora Tajdeen saman cinyar shi.
Sai da suka kwan suka wuni amman ko ƙamshi Jos ba su ji ba,ɓangare guda kuma har an saba tsakanin Omar da Jean wanda ya kasance bagwari.

Suna tsaka da tafiya Tajdeen ya aza kuka yunwa ya ke ji,Omar ne ya sauka nemo mashi abinci sai aka yi rashin sa'a a yayi hatsari bisa hanya.Tun Jean yana jira har ya fidda tsammani ,kuka Tajdeen ya fashe da shi yana cewa "dan Allah ka kai ni wurin Kaka ni ban son nan"cikin gurbataciyar Hausar shi yace "wacece Kaka?ko wancan da ya tafi?"kai Tajdeen ya girgiza mashi ya shiga yi mashi bayani,zufa ce ta karye ma Jean dan ko babu shakka ya gano sato shi ne Omar yayi.
Cikin son kwantar mashi da hankali ya bashi biscuit da yi mashi alƙawarin zai kai shi wajen Kaka,cike da murna Tajdeen ya fara cin biscuit ɗin shi kuma Jean ya cigaba da tuƙi har suka isa Jos.

Wani tangamemen gida suka tsaya,tun shigowar shi mutanen gidan uwanda duk maza ne suka fito ko wane murmushi kan fuskar shi.
Tsaye Tajdeen yayi ya na kallon jama'ar uwanda duk kusan kamar su guda haka ma tsayi,hannun shi Jean ya kama suka ƙarasa.
Fuskar shi dattijon  cikin su ya shafa yana mai ɗan rage tsayin shi yace "ina ka samo wannan kyakyawan?"ya faɗa yana kallon Jean a nan tsaye yayi masu bayani,cike da tausayin Tajdeen duk suka shiga taɓa kan shi suna mashi murmushi "mi sunan ka ?"dattijon ya tambaya lokacin da suke shigowa babban falon gidan "Tajdeen"ya ba shi amsa "to daga yau za mu dinga kiran ka da Deen kaji ɗan kyakyawan jikana"kai Tajdeen ya ɗaga yana murmushi wanda shi kan shi bai san na minene ba....

****Niamey

Wajen minti talatin Kaka na jiran Tajdeen shiru,inda Omar ya tsaya da mota ta kalla da niyyar yi mashi magana wayam babu shi babu motai maimakon hankalin Kaka ya tashi sai cewa tayi "ka ga ɗan albarka mai tunani ya ga Tijani ya daɗe shine ya bi min sawun shi"ta fada tana mai rufe furar da ta dama ma Omar murfi.Can wasu mitinan ta riƙe haɓa tace "yau ni na ga gantalale daga bin sawun yaro ba kai babu shi balle daɗa madarar"ta kusa da ita ce ta tambaya "ni kam Delu lafiya kike ta surutu ke ɗaya?"
"To ba doli nayi surutu ba tun ɗazu Tijani ya tafi sanye madara har yanzu bai dawo ba kuma shi ma Umarun haka"ido ta fiddo waje tace "kar dai kice mai motar da ya ke zuwa nan sayan fura?"
"Eh shi fah,bari ki ga na tai na dubo su da kaina ƙila suna can shago(kanti)suna sayen kayan maƙulashe sun bar ni nan da tashi zuwan kan fura"cewar Kaka tana mai tashi ta tafi gun mai madarar da kullum Tajdeen ke sawowa,ba ta jima ba ta dawo hankali tashe tana gugar ƙwalla da haɓar zane "ka rufa min asiri Umaru ka dawo min da jikana,oh waini ni Delu"kafin wani lokaci wurin kancame kowa sai tofa albarkacin bakin shi ya ke dayawan mutane gani suke son banzar Kaka ne ya jawo haka yayinda Ɗan Ladi ke ta ƙara maimaitawa ya ga lokacin da Omar ya saka Tajdeen a mota ya wuce a guje.

Shaƙe shi Kaka tayi tace sai ya fito mata da jika ai da shi aka gama baki,dakyal aka taɓe shi ga hannunta.Zaman ƴan bori tayi ta fasa ihu "wayooo ni Delu mi zan ce ma Haliru in na koma gida?ubangi ma'aikin Allah ya tsine ma Umaru Allah gama ka da bala'in duniya, innalillahi ileyhi raji'un jama'a ku cece ni ku karɓo min jikana"sosai Kaka ke kuka,ganin haka aka tsayar da mai taxi aka sakata tare da kayan sana'ar ta sai wata da ta shiga dan kaita.

A tsakar gida suka tarar da Anya hannunta dafe a saitin zuciya,Haleematu na kuka amman ta kasa ɗaukar ta saboda lugude da faɗuwa da gabanta ya ke.Tun kafin su shigo kukan Kaka yayi

masu sallama,da azama ta miƙe ta nufi waje kiciɓis suka yi da Kaka wace ake kokawa saka ta gida amman fafur tace ba zata shiga ba doli sai da Tujani.

"Ina Tajdeen?"Anya ta tambaya murya na rawa zuciyarta na tsinkewa,"ya tafi da Tujanina ya tsere da shi"Kaka ta faɗa cikin kuka kafin su an kare sai ji suka Anya ta yanke jiki ta faɗi.

Kukan Kaka ne ya ƙaru tana mai kwance kwagirin ƙugunta ta fiddo wayata tana cewa "na shiga uku ungo kira min Haliru"mai taxi ya amsa ya shiga répertoire nan ya danna ma Baffa kira.Ba jimawa sai gashi cikin tashin hankali,ciciɓar Anya yayi ya saka a taxi suka nufi asibiti Kaka kuwa sai kuka ta ke har roƙon likita tayi ya bata gado yayi mata allura barci ko taji sanyi a ranta.

Sai da Anya ta sha ƙarin ruwa sosai kafin a samu ta farka,hawaye ne ke zuba kan fuskarta tana jin abun kamar cikin mafarki .Tun tafiyar su kasuwa take jin faɗuwar gaba ashe iftila'in da zai faɗa mata ne,a hankali ta fara motsa baki "innalillahi wa'inna ileyhi raji'un allahuma ajirni fee musibati wa'akhlifni khairun minha"sai ta rumtse ido tana mai cigaba da yi mashi addu'a a zuci ta na mai roƙon Allah kar ya ba shi ikon cutar da Tajdeen....

***Maradi

Kwance take bisa darduma hannunta riƙe da carbi tana ja,a zahiri tasbihi take amman a zuci tunanin malam Nur ne fal ranta.
Sallama wani yaro yayi yace "wani yace a kirawo mashi Nazifa"ras gabanta ya faɗi kafin tace wani abu Inna tace "je kace ga ta nan zuwa"kafin ta kalli Nazifa wadda ta taushi zaune "ki tashi mana ki ga ko wanene" "toh Inna "ta faɗa tana mai miƙewa ta saka takalmi.

A can ƙarƙashin wata itaciya ta hango shi,sanye ya ke da wani farin yadi ya taje sumar kan shi sai walƙiya ya ke baƙin gilashi ne a idon shi.Sai da tayi wata sanyayar ajiyar zuciya kafin ta ƙarasa gun shi bakinta ɗauke da sallama.
"Tare da sahibata abun alfaharina"shine malam Nur yace fuska ta rufe da hijab alamun jin kunya kafin tace "ya gida ina Maman da su Balkis"kwaɓe fuska malam Nur yayi yace "shine ni ba za a tambaye ni ya nike ba?toh duka lafiyar mu lau"dariya Nazifa tayi tace "laaa to kai ba ga ka a gaba na ba?hum to naji ya kake ?"bai bata amsa ba sai kallon ta da ya tsaya yi hakan yasa ta sunne kai ta fara wasa da yatsun hannunta, murmushi yayi dan kunyar ta na ɗaya da abinda

yasa ya ke sonta "ya dai babyn Nur?"ba tare da ta ɗago ba tace "daidai" "ok shine kuma kika ƙyale ni"yadda yayi maganar a shagwaɓe yasa tayi saurin ɗagowa ta dube shi "kuma ni za'a ayi ma shagwaɓa?🤔"tsayuwar shi ya gyara tare da cewa "eh mana in ban yi maki ba wa zan yi ma?"tana shirin magana yaya Ɗalhat ya karyo kwana layin wanda ƙarar tsohon Babur ɗinsa shi ne ya shaida mata da zuwan shi yadda malam Nur ya ga ta firgita ne yasa shi kallon Ɗalhat wanda ya ajiye mashin a ƙofar gida ya doso inda su ke.

"Keee!wuce maza gida,kai kuma wa ya baka izinin zuwa da har za ka wani parker mota kana wanke ƙawanta da ƙarya salon ka yaudare ta"shine abinda Ɗalhat ya faɗa cikin ɗaga murya tun kafin ya iso inda su ke.Cikin rawar murya Nazifa tace "yaya Ɗal..."wata uwar tsawa ya daka mata tare da nuna mata gida da gudu ta ruga ta na mai fashewa da kuka .........
[11/03 11:32] MRS SADAUKI: *SHAUƘIN SO*💘

```LoVe story```💟

By
Chamsiya Laouali Rabo
{MRS SADAUKI💫✍️}

*FCWA*☀️

---

Page 7-8

"Assalamu alaikum"malam NUR yace wa Ɗalhat yana mai miƙa masa hannu alamun suyi musabaha wani
banzan kallo yayi ma shi tare da ɗaga ma shi hannu yace "bari abarka abinda zan faɗa maka ka fita hanyar ƙawanta,kar na koma sake ganin ka nan"murmushi malam Nur yayi "babban yaya kar ka yi min haka mana ai duk wanda yace ya na son naka ya gama maka komai a duniya"ya faɗa yana ɗan jan gemu,taɓe baki Ɗalhat yayi ya kuma cewa "Ni ba zaka yaudare ni da salon ustanzanci ba haka kuma ba zan bari ka yaudari ƙanwata ba in dagaske kake sonta ai sai ka turo magabatan ka"yana gama faɗar haka ya juya ya shige gida ba tare da ya tsaya jin ta bakin malam Nur ba.

Tsakar gida ya tarar da ita kwance tana kuka gefen ta kuma Inna na rarrashin ta,da sauri Inna ta miƙe tana kallon Ɗalhat wanda sai kumbura ya ke yana batsewa "Inna miyasa za ba ki barin ta
```

fita zance?yanzu sabida Allah salon a rinƙa yi da ni ana cewa ba mu bata tarbiyya ba ido na ganin ido ta fita zance duk wanda ya wuce yana kallon ta kuma abun takaici wai Ɗan masu kuɗi..."

Saurin katse shi Inna ta yi da "in ban barta yin zance ba kai zaka auren ta?nace kai za ta aura ko kuwa ba ka ga girma take ba?shi wanda ka kora ɗin ka san wane ne? malaminsu ne na makaranta  wanda ta ke faɗa ma saboda karatun da ya ware ya ke koya mata na musamman sauran ɗaliban ke jin haushin ta,ina ce kai ma da kanka har dadɗi ka ji  ganin tana ta samun ilimi ko?"wani huci ya furzar yace "Inna ki yi haƙuri sam ban yi tunanin shi ne ba dan a yadda na gan shi bai yi kama da malamin makaranta ba,amman in shaa Allah ba zan sake korar shi ba in ya zo"ɗagowa Nazifa ta yi fuska shaɓe-shaɓe da hawaye ta kalli yayan na ta tace "da gaske ya Ɗalhat?"kai ya jinjina mata,cike da murna ta tashi ta wanke fuskarta ta nufi gidan su Samira.

Gidan babu kowa sai Samira zaune kan kujera tana wankin kaya gefe guda kuma wayarta  na fidda sautin waƙa.Sallama Nazifa ta yi kafin Samira ta kai ga amsa mata ta kuma cewa "Allah ya shirye ki ke yanzu waƙa ce kike sauraro ko kunya ba ki ji matar malam guda?"sheƙeƙe Samira ta ɗago tana kallonta tace "to sannu ustaziya miye na jin kunya daga sauraren waƙa sai ka ce wata ta gamtsi wadda ba ta kamata ba " "waƙa dai sunanta waƙa malama dama bege kika saurara da ya fi wannan shirmen"ruwan wankin ta watsa mata a fuska tace "wallahi ke ce shirme ba ni ba"dariya Nazifa ta yi  "kan ki dai ake ji"ta faɗa tana ɗaukar waya ta loda lambar malam Nur amman a kashe.
Cikin sanyi jiki ta labarta ma Samira abinda ya faru "to miye na damuwa tunda yanzu ya Ɗalhat ɗin ya amince ya dinga zuwa?"

"Samira ba za ki gane ba ne ta yaya kamilin mutum kamar malam Nur a jefe shi da mugayen kalamai? Ni wallahi in da na san gidansu da na tafi na bashi haƙuri"cike da mamaki Samira ke dubanta tace "haƙuri?eh lalle yanzu na yarda da maganar ɗalibai da su ke cewa kin fi son shi fiye da yadda shi ya ke son ki,wannan rawar kai har ina?yanzu ke sabida Allah sai ki je gidan na su dagaske?"kai ta ɗaga mata alamun eh, baki Samira ta ja tace "to ADS ne gidansu kuma duk ɗan adaidaita sawun da kika ce ma ya kai ki gidan Ali Ɗan Masani zai kai ki"dafe ƙirji Nazifa ta yi tace "ki na nufin  ɗan Alhaji Ali Ɗan Masani ne?"tsuki Samira ta yi tace "sai ki yi,ni ma jiya naji malam Jabeer na yi ma shi kirari"jikin Nazifa ne yayi sanyi dan duk yadda take zaton malam Nur na da kuɗi ba ta zata jinin Alhaji Ali ba ne "gaskiyar yaya Ɗalhat,ni yanzu mi ma zai yi da ni ƴar talakawa u
wanda abincin da za su ci ma ya na yi masu wuya wata rana?"
"To shine mi dan ya na Ɗan masu kuɗi ke kina ƴar talakawa?ina ce dai akwai ƴaƴan masu kuɗin dayawa a makaranta amman ya nace sai ke ko?"

"Samira ina jin tsoron kar danginsa su ƙi karɓata,na san malam Nur ba dan wani abu ya ke sona ba in ma akwai bai wuce ilimi shi ma Allah ne ya bani" "hum!su kuma su suka ba kan su kuɗin ko?Nazifa ya kamata fah ki nutsu ki gane da tallaka da mai kuɗi duk Allah yayi su kuma shi kaɗai ya san manufar yin haka,dan Allah ya baka arziki ba ya na nufin ya fi son ka da kowa ba ne in kuma yayi ka talaka ba wai dan bai sonka ba ne a'a hakan dai ya ga yafi dacewa da rayuwar ka"wani lumfashi Nazifa ta sauke tace "na sani amman abinda nake nufi ni ba class ɗinsa ba ce ya fi ƙarfina"

Cikin jin haushi Samira tace "kawai ki ce dama ba ki son shi tun farko amman zancen wani ba ajin ki ba ne bai ma taso ba,kyawu ma na banza kin fi shi kuɗi kawai zai gwada maki su kuma ba komi ba ne face dauɗar duniya in baka kashe su ba ka mutu ka bar su"

"Tabbas haka ne Allah sa dai mu dace"cewar Nazifa ta na mai shiga galerie inda hotunan malam Nur su ke,da "Amen"Samira ta amsa mata kafin ta miƙe ta fara shanya kayanta...

A ɓangaren malam Nur dakyar ya kawo kansa gida dan baƙin ciki da tiririn da zuciyarsa ke yi masa,tun da ya ke ba'a taɓa yi masa cin fuska ba sai yau.
Ya na isa gida direct part ɗin shi ya wuce ba tare da yayi la'akari da Baba wanda ya ke zaune a falo yana duba wasu littattafai.

Toilet ya shiga ya sakar ma kansa ruwa,a ƙasan zuciyarsa kuwa "innalillahi wa'inna ileyhi raji'un"kawai ya ke nanatawa har ya fara jin sauƙin abun.

Cikin kayan ƴan balo (ƙwallo)ya shirya ya feshe jikinsa da turare sannan ya ɗauko system ɗinsa ya kunna, hotunan ta ne ya ke kallo wasu ta na dariya wasu ta shagwaɓe fuska .
Bai san lokacin da murmushi ya kubce ma shi ba da ya zo inda ta washe baki tana dariya kyawawan haƙoranta fari tas waɗanda suka samu ƙawanyar wushirya,sai dimple (point beauté) ɗin ta mai ƙara mata kyau da ya lotsa.Ya shagala sosai da kallon hoton hakan yasa bai ji shigowar Baban nasa ba,sai jin ya dafa kafaɗarsa a razane ya ɗago ya sauke idonsa kan fuskar mahaifinsa wanda shi kuma ya ke kallon hoton Nazifa wanda ke bisa system.

Miƙewa yayi ya na ɗan sosa kai yace "um...Baba ina wuni?"murmushi Baba yayi ba tare da ya amsa gaisuwar da yayi ma shi ba yace "wacece wannan?"i'ina malam Nur ya fara

"dama...dama ita ce wadda nake gaya ma Maman ina so"wani murmushin Baba ya sake yi yace "shine tace ba ta sonka wanda hakan yasa ka shigo gida rai ɓace ba tare da ka gaishe ni ba ka wuce ɗaki sannan ina ta yi ma sallama ba ka ji ba?"

Kai malam Nur ya sunne yace "ba wai cewa ta yi ba ta sona ba" "to mine ne?"

"Yayanta ne yace min wai wani in dagaske na ke in turo magabatana dan shi bai barin ƙanwarsa na zance "

"To shine mi? Ai hakan ne daidai ka bani address ɗin gidan za mu je in shaa Allah ai mu dama maganar auren mu ke so"tsabar jin daɗi Ustaz bai san lokacin da ya rungume Baba ba.

Ƙarfe goman dare Maman ce a ɗaki sai saffa da marwa take ,ta rasa sukuni tun lokacin da Sappa ta shaida mata tana son Nur.
Wani gwabron numfashi ta sauke kafin ta nufi part ɗin Baba,a zaune ta tarar da shi bisa tapis ya na tasbihi da yatsun hannunsa.Bayan ta gaishe shi ya amsa ya zuba mata ido ya na kallo duk wunin yau yanzu kawai ya ganta sam babu walwala a tare da ita a kwana biyun nan yana lura da ita.
Gyaran murya yayi hakan ya sa ta ɗago suka haɗa ido,kamar daga bisa ta ji yace "mi ke tafe da ke ?Na ga da magana a bakinki"gyara zama ta yi tace "eh dama akan maganar auren yaran nan ce, Ustaz da Sappa shine nace bari na same ka na nemi alfarma ayi bikin ɗaya rana da na wacan ɗayar da ya zaɓa amman dan Allah kar kace ba ka yarda ba dan wlh Sappa na matuƙar son Ustaz wanda har son yayi mata mugun illa yanzu haka kullum sai an yi mata ƙarin ruwa"Maman ta ƙarashe maganar ta na sakin kuka .

Sororo Baba yayi yana kallonta,sam abun ya zo ma shi banbarakwai, amman shi kansa shaida ne yadda akan ciwon Sappa wanda kullum ƙaruwa ya ke.Nisawa yayi yace "ba damuwa zan yi wa shi Nur ɗin magana" cike da jin daɗi Maman ta shiga yi ma Baba godiya sai kace ba mijinta ba ne.

Washe gari zuwa 12 na rana sai ga valises (akwatina)kala biyun da Baba yasa a kawo ana shigowa da su,a falo aka ajiye su.Cike da murna Maman ta shiga buɗa akwatinan,kaya ne na azo a gani a cicike "Maman akwatinan ɗin wane ne?"cewar Balkis wadda fitowar ta kenan daga ɗaki "na matan yayanki ne ɗaya na Sappa ,Seat ɗayan kuma na ɗaya amaryar"cike da murna Balkis ta fara tsalle kafin kuma ta ruga zuwa ɗaki sai ga shi sun fito ita da Sappa wacce duk ta rame,a bayyane ta nuna farin cikinta gabanin ta sunkuyar da kai jin Maman na cewa "wane kika ɗauka kalar zai ba koko jajayen?"ba ta ce komai ba sai Balkis da tace "Maman bari mu duba wanda kayan ciki suka fi kyau sai anty Sappa ta ɗauka"

"Duk kayan kala ɗaya ne ai"cewar Maman murmushi kan fuskarta.

Malam Nur kuwa ya na can maƙale da waya shi da sahibar shi ya na shaida mata cikin satinan za'a kawo komai su yi aurensu su huta,kwaramniya da ihun Balkis ya fito da shi falo turus yayi jin zancen da ake wai har da Sappa zai aure.

Ransa ne ya ɓace fuskar ta yi kicin-kicin jijiyoyin kansa duk suka fito,cikin furzar numfashi yace "wace Sappai ?"ba Sappa da ke kusa da shi ba hatta Baba da shigowar shi kenan sai da ya razana,cikin tashin hankali ya ƙaraso tsakiyar falon ya durƙusa saman ƙafafun shi tare da game hannuwa yace "dan Allah Maman kar ki min haka wlh ni a matsayin ƙanwa na ɗauketa kuma ni banda tsarin zama da mata biyu Nazi ita ce ruhina,rayuwata da komai naw...."ƙarar faɗuwar Sappa ne ya hana shi ƙarasawa da sauri duk suka nufi gun ta inda ta faɗi a sume........
[11/03 12:08] MRS SADAUKI: *SHAUKIN SO*💘

```LoVe story```💟

By
Chamsiya Laouali Rabo
{MRS SADAUKI💫✍️}

*FCWA*☀️

---

Page 9-10

Ruwa masu sanyi Maman ta zuba ma Sappa nan ta shiga sauke ajiyar zuciya,bakinta ɗauke da sunan Nur.Baba, Maman da Balkis dukansu suka juyo suna kallonsa yadda ya nuna halin ko a jikinsa,hawaye Maman ta goge tana mai ci gaba kallon shi cikin ido hakan yasa ya ƙarasa cikin cool voice yace "Sappaaa..."ƙyalewa yayi ya ja dogon numfashi sannan ya cigaba da cewa "ki yi haƙuri kin ji?in shaa Allah ni da ke mutu ka raba" Sappa da ke kwance cikin ruwa da sauri ta buɗe idonta tarau kan kyakkyawar fuskar Ustaz wacce take sharrr saboda ambaton Allah.Kai ya jinjina mata ganin ta yi masa ƙuri ta na son gasgatawa,ido ta lumshe tana jin wani sanyi na
```

ratsa gangar jikinta ba ta san lokacin da murmushi ya suɓuce mata ba.
Kanta Maman ta shafa tace "Balkis ja ta ku tafi ɗaki ta canza kaya"da "toh Maman"ta amsa ta na mai taimaka ma Sappa ta miƙe a kunyace.

Ustaz kuwa gidansu malam Jabeer ya wuce ya na jin zuciyarsa babu daɗi ,a ƙofar gida ya zauna yana jiran fitowar shi.Seat ɗin mai zaman banza malam ya zauna yana mai gyara hullarsa yace "ya dai NazNur ka kira ni na zo kuma ka wani duƙe kai ko sallamar da na yi ba ka amsa min ba"ajiyar zuciya malam Nur ya sauke kafin ya ɗago fuskarsa ya kalli malam Jabeer "subahanallahi mi ya sami idon naka suka yi ja haka?"cikin ɓacin rai ya ba shi amsa da "sun ƙaƙaba min auren Sappa Jabeer yanzu mi zan ce ma Nazi ?da wane ido zan kalleta na gaya mata su biyu zan aura?"

Zama malam Jabeer ya gyara yace "ban gane ba yi min dalla-dalla"nan malam Nur ya bashi labarin komai da ya faru ya ɗora da faɗin "ka san dama ta sha gaya min ta na sona to ban zata rashin kunyarta  ba har ta kai haka shine ta yi min gami da iyayena su kuma suka yanke hukunci ba tare da neman shawarata ba"

Jinjina kai malam Jabeer yayi kafin yace "to shi aure lokaci ne kuma matar mutum kabarinsa,yanzu yadda za ayi ka bari har sai an sa date ɗin bikinku sannan ka gaya ma Nazifa" "Ka na ganin hakan shine mafita?" "Eh tabbas"nan dai malam Jabeer ya cigaba da kwantar ma abokin nasq da hankali tare da nuna masa mahimmancin yi wa iyaye biyayya ba dan bai sani ba sai dan ƙara yi ma shi tuni su ma sunada haƙi kansa.

Cikin sati guda kacal Baba yasa aka yi bincike dangane da tarbiyyar Nazifa inda ta samu kyakkyawar shaida hakan yasa ba ayi ƙasa da gwiwa ba aka kai lefe tare da tsayar da rana aure nan da wata biyu.

Mahaifiyar Sappa ba ƙaramin daɗi ta ji ba ganin zumuncinsu zai ƙara ƙarko ita da ƴar uwarta,Sappa kuwa tun da aka kawo lefen ta ƙara ɗaukar son duniya ta ɗorawa Ustaz dan yanzu ƙawayenta  SapNur su ke kiranta.

Tun wayewar safiya yau take yawan jin faɗuwar gaba,ko dan za ta je gaishe da iyayen Nur ne

oho.A haka dai Samira ta tsantsara mata lalle ta yi wanka sannan ta shafa mata hoda,za ta yi mata kwalliya irin ta zamani tace ba ta so.
Wani rantsantsen less  ta saka mai ratsin ja,hijabi da kalmi da jaka ta fitar jajaye  hakan ba ƙaramin fiddo ta kayan su kayi ba.
"Masha Allah"shine abinda Inna ta faɗa Rakiya da Samira kuwa sai kallonta su ke yadda ta fito sak amarya.Hotuna Samira ta fara ɗaukar ta a wayar da malam Nur ya saya mata kafin ta fito waje inda Ustaz ke jiran ta.
Sai da suka gaisa da Samira kafin su wuce gidan Maman,a falo duk suka tarar da ƴan gidan ana zaman jiran Nazifa.Malam Nur ne yayi sallama yana gaba ta na biye da shi a baya,a ƙasa ta zube tana mai kwasar gaisuwa cikin sakin fuska Maman ke amsawa kafin Balkis tace "ina wuni anty amarya"ɗagowa Nazifa ta yi ta kalli inda ta ji murya ta sakar mata murmushi sannan ta amsa akan idonta Balkis ke zungurar Sappa wacce sai cika take ta na batsewa,dakyar tace "sannu"shi ma don ta ga irin kallon da Ustaz ke jifarta da shi ne,gaban Nazifa ne ya faɗi cikin sanyi da ta ji duk jikinta ya ɗauka ta amsa ma Sappa kafin su tsaya ƴar kallon-kallon.Wata irin muguwar tsana ce Nazifa ta hango cikin idon Sappa,cikin zuciyata kuma take tambayar kanta 'to ita kuma wannan wace ce?mi nayi mata ne daga gani na take hararena? ...'ba ta tsinke da lamarin Sappa ba sai da ta ji ta ja tsuki ƙasa-ƙasa tare da cewa "baƙauya kawai"kallon Sappa Maman ta yi dan ta ji sarai abinda tace.

"Sappa tashi ki ɗauko ma antynki ruwa mana,kun wani sa ta a gaba ku na kallo haka ake tarban baƙi?"Maman ta faɗa cikin bada umarni,gunguni Sappa ta tafi ta na yi ta shiga kitchen Balkis ta bi bayanta.
"Anty Sappa mi za ki yi da ruwan pampo ?ba dai amayar ce za ki kai ma ba?"Balkis ta faɗa lokacin da ta shigo ta tarar da Sappa na zuba ruwan pampo cikin moɗar ƙarfe,yatsina fuska tayi tace "eh mana ai su ta saba sha a gidansu ko ba ki ga ƴar talakawa ba ce"cikin rashin jin daɗin zancenta Balkis tace "a haka kuma Ustaz ke son abar shi"ta na gama faɗi ta ɗauki jus ɗin da ita ta haɗa da kanta ta fita,ƙanƙara ta zuba cikin kofi sannan ta tsiyaya lemun ta miƙa ma Nazifa sannan ta ajiye sauran kusa da ita ko da buƙatar in ta ƙara.

"Na gode"Nazifa ta faɗa tana mai yin Bismillah ta ɗan kurɓi lemun cike da kunya, Ustaz na kallonta ya na jin son ta na ƙara ratsa shi ya lura a takure take hakan yasa ta kasa cin fruits ɗin da Balkis ta kawo daga baya.

Zamewa yayi daga bisa salon ya zauna ƙasan capet,trayn ya jawo gabansa ya ɗauki ayaba ya ɓare tare da nufar bakinta "buɗe bakinki na ciyar da ke tunda kunya kike ji"ɗagowa ta yi ta kalle shi sannan ta juya inda Balkis ke zauna Maman kuwa tuni ta bar gun, ɗan turo baki ta yi tare da buɗe shi za ta yi magana kawai ya tura mata ayabar a baki ba ta da wani zaɓi hakan yasa ta ɗan guntsira tana murmushi.Taratseeee kofin glas ɗin da ke hannun Sappa ya sulɓe,dukkansu kallonta suka yi banda Nazifa da ta sunne kai zuciyarta na bugawa das-das.

Wata uwar tsawa Ustaz ya daka mata "keee!wane irin hauka ne wannan?so kike ki firgita min mata ko miye ?maza ɗauko tsintsiya ki kwashe shi sannan ki goge wurin"wasu zafafan hawaye suka karye  ma Sappa ta ɗauko salade de fruits ne dan ta nuna ma Nazifa isa da su sun san yadda ake shan shi kuma sun saba sai ga shi kogo ya juye da mujiya.Sanin halinsa ya sa ta yi saurin tattare glas ɗin da ya fafashe ta kwashe sannan ta goge wajen tsaf,cikin kuka ta nufi part ɗinsu.

Ajiyar zuciya Balkis ta sauke kafin tace "Allah yaye maki wannan baƙin halin"kusa da Nazifa ta zauna tace "antynmu dan Allah ki yi haƙuri ki ci duk wannan abun saboda ke fah na yi shi"ta faɗa tana mai sake jawo wani tray mai ɗauke da abinci,saving nata yi amman fafur Nazifa tace sai dai Balkis ta sa hannu su ci tare.
Kallon malam Nur Balkis ta yi sai ya jinjina mata kai hakan ya sa suka fara cin abinci shi kuma ya nufi ɗakin Baba,bai fito ba sai da ya kwatanci sun kamalla sannan suka fito shi da Baba.Gaishe shi ta yi tamkar uban da ya haife ta cikin kulawa Baba ke amsawa ya na tambayar ta ƴan gida da kuma karatu.

Har Nazifa ta tashi tafiya amman Sappa ba ta sake fitowa ba,goma ta arziki Maman da Baba su ka yi mata Ita kuwa sai zuba godiya take.Kafin Nur ya sauke ta gida sai da ya biya Kalla Transa Mall yayi mata sayayya ƴan abubuwan da ba za a rasa ba.

Ganin irin hidimar da aka yiwa Nazifa ya sa Inna jin sanyi a ranta da tunanin ko ba ta da rai Nazifa ba za tayi kukan maraici ba dan a yadda Nazifa ta tsaya ta na yabon Maman da Balkis abun sai Masha Allah.
Samira da Rakiya sai buɗa kayan su ke suna fesa turarurukan,bayan sun gama gani ne ta ba kowa rabon shi Inna dai sabulu kawai ta amsa ta ajiye ma Ɗalhat.
"Tashi ki raka ni gida zan wuce"Samira ta faɗa ta na mai ɗaukar ledar kayanta,hijab Nazifa ta saka suka kamo hanya a nan ne Nazifa ta shiga ba Samira almarar Sappa ta ƙare da cewa "wlh har cikin raina nake jin tsoron ta dan da alamu irin mugun kallon nan da take min ba ƙaramar tsanata take ji ba"

Numfashi Samira ta ja tace "to Allah kyauta sauƙin ta dai ba ƙanwar malam Nur ba ce da kin shiga uku kin san ƴan uwan miji in ba su son ka akwai matsala"

"Eh haka ne sosai, amman dai su na da alaƙa dan da alamu a gidan take zaune inda ma na ji sauƙin abun da yake tana tsoron Noori"cewar Nazifa ta na mai tsayawa dan sun ɗan yi nisa da gidansu alamu kuma sun nuna daga nan za su rabuwa,sallama su ka yi kowa ya tafi gida.

Da dadare bayan sallah isha'i malam Nur ya kirata a waya suka sha hira su ta soyayya wacce rabin ta duk akan yadda bikinsu zai kasance ne da irin rayuwa da za suyi bayan aure.
Har sun yi sallama Nazifa ta yi saurin tsayar da shi tace "um..Ni kam Noori wannan wace ce wadda na gani gidanku?"duk da ya gane wadda take nufi amman ya basar yace "wace fah daga ciki?"fuska ta ɓata kamar ya na ganinta tace "ba Balkis ba ɗayar"
"Wai Sappa kike nufi?" "Um ita"ta ba shi amsa "kishiyarki ce"ya samu bakinsada furtawa,shiru ta yi kamar ba ta ji ba sai da ya sake maimaita mata daga ƙarshe yace zai ƙara yi mata bayani daga baya ya kashe wayar.A daren ranar nan juyi Nazifa ta aniya yi ba ta rumtsa ba,kalmar kishiyarta ce ta tsaya mata a rai.

Washe gari ta kama asabar ranar zuwa makaranta tun bayan kawo kuɗin aurenta ba ta sake zuwa ba sai yau da malam Nur ya bata umarnin zuwa.
Lati ta yi yau kasancewar ta yi ranar tashi,tun da ta shigo ƴan ajin ake kallonta ana ƙus-ƙus-ƙus ita dai ba ta kula su ba gefen Samira ta zauna babu jimawa malam ya shigo.
Har zai fara karatu wata tace "malam yau ba a bulalar lati ne ?"duk ɗaliban kallonta su ka yi,malam ya so yayi kamar bai ji ta ba amman kar ace yayi son kai saboda Nazifa ta zo late kuma ya san saboda a ga yadda zai yi ne suka kitsa haka.

"Duk wacce ta san ta zo lati ta tashi tsaye"shine abinda malam Nur yace yana mai buɗe coffre ya ɗauko dorinarsa,Allah ya isa suka fara jama Rabi'at kafin su fara miƙewa tsaye.

"Dan Allah ki tashi ki ba mara Ɗa kunya saboda ke ne suka tuna ma malam zancen bulalar lati amman an fi sati rabon da ayi ta"cewar Samira ta na mai jimƙe hannun Nazifa , murmushi ta sakar ma ƙawarta ta kafin ta mike tsaye.

Bulala goma-goma malam Nur ya shiga zabga ma Ɗaliban har ya zo kan Nazifa,daure zuciya yayi ya shiga tsula mata bulala duk in ya shauɗa sai ta rumtse ido dan zafi har aka gama mata.

Zaunawa suka yi suna jinyar jikinsu dan duk juriyarka in malam Nur ya zane ka sai ka ji jiki,karatu suka fara yi kamar kullum har lokacin shan iska yayi.

"Naziii..."shine abinda malam Nur ya faɗa ganin ta nufi ƙofar fita,dawowa ta yi tana turo baki.Ajiyar zuciya ya sauke tare da furzar da huci yace "sorry"ɗagowa tayi tace "da aka yi mi fah " "da dorina ta zane ki"baki ta sake turowa tace "ai kai ka sanya ta"ta a idasa maganar kamar za tayi kuka "nooo!kar ki yi kuka zan ko hukunta ta dan ba za ta sake kwana duniya ba ƙonata zan yi cikin wuta tunda har ta taɓa fatar amarya Nur"dariya Nazifa ta yi har da ƙyarƙyatawa nan dai

su ka fara karatun litattafai kamar kullum.

Bayan an dawo daga shan iska maimakon a cigaba da karatu sai malam Nur ya ɗauki rigar rashin mutumci ya saka,nan ya shiga yi ma ɗaliban da suka sa ya ɗaki Nazifa masifa inda ya ke cewa "ku a tunaninku har za ku iya yi ma malam Nur wani ƙulli wanda ba zai gane ba? Ribar mi kuka ci da na daki Naziii?ke kuma da kika fi su fitsara sai suka turo ki ki min tuni da bulalar lati ko?"cikin son kare kai suka fara rantse-rantse shi kuma ya katse su da cewa "mi yasa kwanakin baya baku tunan min ba sai na yau? Duk ƙiyayar da kuke nuna mata na sani ba tun yau ba dan haka zan ba kowacen ku hutun sati guda duk wacce ta san da sa hannunta ciki ta tashi ta fita"ya na gama rufe baki munafukan duk suka fita waje.

Wannan abun da malam Nur yayi shi ya wanke zuciyar Nazifa da duk wani ƙunci har ta mance da maganar wata Sappa.

Haka rayuwa ta cigaba da tafiya har aka zo yau saura kwana biyu biki,duk ɓangaren uku shirye-shirye kawai su ke Sappa ta koma gidansu tun tuni mahaifiyarta sai ƙara gyara ɗiyarta take.Inna ma ba a barta a baya ba sosai ta ke kula da Nazifa wanda hakan ya sa ta ƙara haske ta yi wani fresh sai ƙyalli take da santsi.

Darul Mar'a malam Nur ya biya kuɗi tun daga gyaran jiki,farce,gashi da lalle,sosai ta yi kyau kana ganinta ka ga cikakkiyar amarya ƙawayenta sai ɗaukar ta hoto suke.

Ranar ɗaurin aure duban jama'a suka shaida auren Nuradeen Ali Ɗan Masani da Nazifa Sa'id Lawan da kuma Sappa Hamisu Kabeer,mutane da dama sai mamaki su ke jin mutum guda ya auri mata biyu duk ɗaya rana.Ɗalhat da shi ya bayar da auren ƙanwarsa sosai ya girgiza jin ba ita ɗaya ba ce,a zuci ya ke tunani "ƙila shiyasa Inna tace min zan ji wani a wajen ɗaurin auren amman kar na tada hankalina,to ko shine abinda malam Nur ya zo ya gaya ma Inna a jiya?"ganin dai bai dai amsar tambayar ya ƙarasa wajen baƙinsa su ka nufi gida kasancewar ɗaurin auren masallaci ne.

Sosai Nazifa ke kuka wanda ta rasa na miye na farin ciki ko akasin haka,yau dai ta zama NazNur.......

Please share
[11/03 12:31] MRS SADAUKI: *SHAUKIN SO*💘

```LoVe story```💟

By
Chamsiya Laouali Rabo
{MRS SADAUKI💫✍️}

*FCWA*☀️

---

Page 11-12

An yi walimar biki ta kowanne bangare,zuwa dare kuma aka miƙa su gidan mijinsu.
Danƙareren gida ne na musamman mai part biyu,ko wace ciki uku da falo ne aka yi mata.
Nazifa banda kuka babu abinda take ta wani riƙe Samira tace babu inda za ta,a na haka sai ga sallamar ango da malam Jabeer.
"Yawwa ga angonki nan ai yanzu sai ki sake ni"cewar Samira ta na kallon nata sahibin,sallama suka yi masu da fatan alkairi na farin ciki mai ɗorewa kafin su wuce.

Murmushi mai ɗan sauti malam Nur yayi wanda har sai da ta ji shi cikin ƙahon zuciyarta,mayafin da ta luluɓe ya ɗan ɗage nan kyakkyawar fuskarta ta bayyana wacce ta yi shaɓe-shaɓe da hawaye,wani murmushin ya ƙara yi yana jin wani irin SHAUƘIN SO na ɗibarsa .

"Amincin Allah ya tabbata ga Shalele ƴar gatan malam Nur, Mama su Ayman da Laila"Nazifa dai tun da ya fara magana ba ta ɗago ba sai da ya zo ƙarshen maganar ne ta yi saurin rufe fuska tana dariya.

"Tashi ki yi alwala ki rama sallah da ba ki yi ba,ina zuwa"ya faɗa tare da fita ita kuma ta miƙe ta shiga toilet ta ɗauro alwala ta gabatar da sallah magrib da isha'i wanda ba ta samu ta yi ba saboda ɗawaniya biki.

Malam Nur ledodin da suka bari a falo ya ɗauki biyu ya fita zuwa ɓangaren Sappa wacce ta cika ta yi fam kamar za ta fashe dan tun lokacin da suka shigo shi da malam Jabeer akan idonta.
```

Tura ƙofa yayi tare da yin sallama,can tsakiyar gado ya tsinkayota ta sha kwalliya kamar wata aljana.Ido cikin ido su ke kallon juna,babu abinda malam Nur ya tsana irin wannan kwalliyar mai sauya wa mutum kamanni,baki ta turo ganin yayi tsaye bakin ƙofa bai zo gun ta ba.
"Wa'aleykum salam"ta faɗa cikin jin haushi taɓe baki malam Nur yayi kafin ya ajiye mata ledar gasasar kaza da ta fruits da jus,yace "sai da safe in Allah ya tashe mu ki zo ki kulle ƙofa"wani irin dirowa Sappa ta yi daga kan gado ta na mai cewa "kai kuma ina za ka je?"banza yayi da ita ya fice.
Zuciyarta na zafi ta je ta rufe ƙofa ta dawo ta haɗe kai da gwiwa tana rusar kuka.

Malam Nur sai da yayi wanka a ɗakinsa tare da alwala sannan ya tafi gun amarya,a zaune ya tarar da ita tana ƙare ma ɗakin kallo ba laifi Inna ta fidda kuɗi an yi mata katakai masu kyau daidai ƙarfinsu.Gyaran murya yayi ta juyo ta na kallon shi sai kuma ta maida kai ƙasa tana wasa da zoben hannunta,"amarsu a tashi mu yi sallah godiya ko?"ya faɗa lokacin da ya zo dab da ita,miƙewa ta yi ta shimfiɗa wani tapis daga gaban nata malam Nur ya hau ya ja su sallah suna gamawa su kayi ƴan ciye-ciye kafin su gabatar da sunnah Manzon Rahaman.

Asubah farin Nazifa ta farka,cike da jarumta ta miƙe ta faɗa toilet ta haɗa ruwan ɗumi ta yi wanka game da alwala.
Har sai da ta gama raka'atil fajir sannan malam Nur ya farka,shi ya canza zanen gado ya wanke a injin wanki sannan yayi wanka ya zura jallabiya zuwa masjid.

Sai da rana ta fito wantsar sannan malam Nur ya dawo gida dan wannan sabonsa ne duk bayan sallah asubah masallaci yake zaunawa yayi ta azkar.Har zai shiga ɗaki sai kuma ya ji motsinta a kitchen,a hankali ya ɗaga ƙafar shi zuwa can kitchen ɗin ya jingina da bango ya na kallonta ta na zuba ruwan zafi a Flask,ba ta san da zuwan shi ba sai ji tayi yayi huging nata yana murmushi mai sauti "Barka da asuba!"ta faɗa a kunyace lokacin da ya juyota suna facing juna, hanci ta ya ja kafin yace "Barka da asuba wa?haka ake gaishe da miji ko ɗan sunan nan na masoya ba za'a saka ba"malam Nur ya faɗa yana mai zuba mata ido,turo baki ta yi tace "to ka sake ni sai na faɗa"waro ido yayi yace "au!sai na sake ki zaki faɗa?to bari ki gani"dariya ta yi jin ya sungumeta kamar wata baby,kan bed ya direta ya lulubeta da blanket  "yi kwana kwanta ki huta"ya faɗa yana mai dadaɓata tare da hura mata iska a fuska,lumshe ido ta yi tana jin soyayyar mijinta na ratsata kafin wani lokaci har barci ya ɗauke ta.Murmushi malam Nur yayi ya shiga wanka ya fito ya shirya cikin wata rantsatsiya gizner H color,zaman hullar kan shi ya gyara ya ɗaura agogo a tsintsiyar hannunsa na dama tare da fesa turare ya nufi part ɗin Sappa.

A zaune ya tarar da ita a man falo,sanye da kayen barci tana kallon tv ta saka tray fruits a gaba tana ci.Wani irin miƙewa tayi tana kallon sanyin idanunta wanda ke sheƙin amarci,ba tare da ta

amsa sallamar da yayi mata ta faɗa a jikinsa ta saki kuka.Duk ƙoƙarin hanata da malam Nur yayi bai sa ta dakata ba,da sauri ya ɗagota yana cewa "lafiyar ki kuwa Sappa?mi ya ke damun ki?yanzu a hakan ne kike zaune tsirara?"saurin sakin shi ta yi ta zuba masa ido cikin raunin murya tace "yaya Nur mi yasa baka sona?mine ne wanda ake so ga ɗiya mace wanda ni ba ni da?ko ban cancanta ka so ni ba ne?"kawar da kai malam Nur yayi gefe yace "tafi ki suturta jikinki sannan ki zo mu yi magana"yadda yayi magana yasa ta jawo wata doguwar rigar abaya ta hauda saman kayan barcin ta na mai zaunawa ƙasa kusan ƙafafunsa.

Huci ya furzar yace "Sappa ina son ki bani hankalinki nan ki nutsu ki fahimce ni, muddin ki na son samun soyayya ta doli ne ki bi Naziii sau da ƙafa ban so ki yi wani abu wanda ranta zai ɓace, ki zauna da ita lafiya ki ɗauke ta matsayin yayarki in kin yi haka ina mai tabbatar maki zaki samu soyayya Nuradeen akasin haka kuma hummm kin san sauran"tun da ya fara magana ta buɗe ƙofofin kunnuwanta tana sauraren shi daki-daki,wasu hawayen takaici ne suka zubo mata amman ta danne zuciyata tace "in shaa Allah zan yi in dai ka so ni" dangwala mata yayi da yatsa yace "good girl"kafin ya ke miƙewa yace "na tafi sai na dawo ki kula da kan ki"amsa masa ta yi da "a dawo lafiya"tana jin daɗin kalmar ta kula da kanta da ya faɗa.

Nazifa kuwa sosai ta sha barci ba ta tashi ba sai da shabiyun rana ta gota shi ma kiran Inna ne ya tashe ta,bayan sun gaisa Inna tace " ki bani hankalinki nan Nazifa ina so ki saurare ni da kunnuwan basira"da "toh Inna"ta amsa ta na mai yin zauna.
Nasiha Inna ta fara yi mata ta ɗora da cewa "Nazifa ina so ki ɗauki ƙaddara a duk yadda ta zo maki,wani abu ba zai taɓa samun bawa ba face dama ya na rubuce a cikin allon ƙaddararsa,sau tari abubuwa su kan zo mana ba tare da mun shirya zuwan su ba ko kuma ba yadda mu ka tsara su ba,da haka nake cewa ki zama mai biyayya tare da duban uzirin mijinki.Tun kafin aurenku Nuradeen ya same ni da maganar iyayensa za su gama shi aure da ƴar uwarsa kuma bai da wani zaɓi sai na yi masu biyayya,ya faɗa min ne saboda ya kasa tunkarar ki dazancen gudun kar hankalinki ya tashi ba dan ya na tsoronki ba sai dan gudun ɓacin ran masoyi.Yanzu haka kishiyarki na nan cikin gidan da kike kawai dai an raba ɓangarorin ne,ki riƙe ta amana ki zauna da ita da zuciya guda kar na ji kar na gani kin yi wani abu na cutarwa"tunda Inna ta ambaci kalmar kishiya ta ji kamar an buga mata guduma amman kuma sauran kalaman sun ɗaure mata jijiyoyi,hawaye ta goge tace "toh Inna in shaa Allah zan kasance mace ta gari" "Allah maki albarka ya kuma baki ikon yin haka"cewar Inna sannan tayi mata sallama.

Jiki ba ƙwari Nazifa ta shiga ta yi wanka tare da simple kwalliya ta saka riga da zane na atamfa,kitchen ta nufa ta haɗa tea ta sha sannan taci sauran kaza jiya.Tv ta kunna ta zauna ta na duba Channel sai ta. ji ana bubuga ƙofa,izinin shigowa ta bada aka turo ƙofar tare da yin sallama.

Amsawa ta yi tana mai kallon Sappa wacce kallo guda za ka yi mata ka gane amarya ce,gaban Nazifa ne ya bada ras dan ko babu tantama wannan ce kishiyarta .Wurin zama ta bata,zaunawa Sappa ta yi ta na cewa "ina kwana anty amarya"amsawa Nazifa ta yi cikin sakin fuska kafin ta bata ruwa.

Tv su ke kallo lokaci zuwa lokaci suna ɗan taɓa hira kafin daga ƙarshe Sappa ta yi mata sallama ta koma ɓangarenta,Nazifa kuwa Samira ta kira suka sha hira daga ƙarshe Samira tace tana nan tafe....

***JOS

Wanka Vani ta yi ma Tajdeen ta saka masa kayan da mijinta Jean ya sawo,sosai Tajdeen yayi kyau ya fito asalin bafulataninsa.Cikin jin daɗin sabin kayan da ta saka ma shi yace "na gode tanti"da sauri Vani tace "no daga yau da Mom za ka rinƙa kira na kaji ko?"kai Tajdeen ya ɗaga yace "toh Mom"kan shi ta shafa ta na jin son ɗan har ƙasan ran ta,Jean da ke gefe ya na kallon su yace "toh ni kuma da mi za'a kira ni ?"kallon Vani Tajdeen yayi alamun ya na son jin amsa daga gareta "Dad ɗinka ne dan haka shi ma daga yau Dad za ka kira shi ka ji ko?"kai Tajdeen ya jinjina alamun toh.

Hotuna Mom ta fara ɗaukar shi wasu ya na tsaye wasu kuma zaune kafin ta jawo shi su fara selfie suna dariya inda a ƙarshe Dad ya shigo suka rinƙa ɗauka tare gwanin sha'awa.
Wasap Mom ta shiga ta saka hoton da suka saka Tajdeen a tsakiya kan profil (dp)sauran kuma ta zaɓi masu kyau ta saka a status,inda ya ke shi ɗaya ta rubuta ```My son Deen``` a sama.

Cikin zumuɗi irin na wanda bai taɓa samun haihuwa ba suka kamo hannun Tajdeen zuwa babban falon gidan,a zaune suka tarar da Raj,Ranvir,Rahul da kuma Père (père na nufin father)wato dattijon.
Dukan su da murmushi su ke kallon Den in ka fidda Raj wanda tun zuwan Tajdeen ya ji ya tsane shi har ƙasan ransa.

Hannuwa Père /father ya buɗe yace ma Deen ya tawo,cikin rashin sabon haka Tajdeen ya shige jikin tsohon.Kansa  ya rinƙa shafawa yana sa mashi albarka kafin yace "ya kamata ku tashi mu ɗan zaga gari ta yadda jikallena zai saki jikin shi"dariya dukan su suka yi dan sun san halin Père da son yara dan dai ma Allah ya jarabi babban yayan nasu Jean da rashin haihuwa kuma shi kaɗai ne mai mata sai Raj wanda ake shirin aurensa.

Cikin gari suka shiga suna zagawa Tajdeen kuwa ya ware ido sai kallon abubuwan mamaki ya ke yadda mutanen garin ke rayuwa irin ta turawa,mata na saka sutura wacce ita da babu kusan ɗaya yayinda mazan garin su ka ɗauki shan giya da sauran kayan maye kamar ado.
Sai da Père ya ga alamun kamar Deen ya gaji sannan suka koma gida,Mom kuwa ta ja hannun Ɗanta suka wuce part ɗinta ta sake yi masa wanka tana cikin shafa mashi mai Dad ya shigo dariya yayi mata yace "abun nema ya samu ko?to a rage yi mashi wanka kar mura ta kama shi"dariya ta yi tare da rufe ido alamun jin kunya kafin ta buɗe akwati ta zaɓo mashi wasu kayan......

Please share
[14/03 16:00] MRS SADAUKI: *SHAUKIN SO*💘

```LoVe story```💟

By
Chamsiya Laouali Rabo
{MRS SADAUKI💫✍️}

*FCWA*☀️

---

Page 13-14

Rayuwa mai daɗi Tajdeen ke fuskanta,ya ci abinda yake so ya kwanta wuri lafiyaye babu abinda ya fi yi masa daɗi irin kayan jikin da ake saya masa tsadadi.
Soyayya da Vani da mijinta suke nuna masa ko ɗan cikinsu sai haka amman duk da hakan Tajdeen bai sa ya mance Anya da Kaka ba dan kusan kullum sai yayi ma Mom hirar su,ita kuwa ta yi ta dariya jin shirmen da Kaka ke yi.

Cike da kulawa take shirya Tajdeen cikin uniform ɗin makarantar da zai fara zuwa yau, murmushi ta yi bayan ta gama shirya shi tace "iyeee ɗan Mom ka ga yadda uniform ɗin nan ta yi maka kyau kuwa? Zo mu je ka duba madubi ka gani"kusan ƙaton madubin suka isa nan kyakkyawar fuskarsa siririya irin ta Fulani ta bayyana,sai sumar kansa wadda ta ɗan toho ita ma sai ƙyallin take.
```

"Na yi kyau Mom"Tajdeen ya faɗa ya na taɓa hannuwa alamun jin daɗi,jan shi ta yi zuwa waje inda Dad ke zaman jiran su.
Mota ya shiga yana ɗaga ma Mom hannu yayinda Dad ya figeta zuwa waje.

Sun yi ƴar tafiya mai ɗan nisa kafin su ke tsayawa gaban ƙaton get ɗin école/school ɗin,hannun shi Dad ya kama ya kai shi har cikin class ya zaunar da shi sai da lokacin fara karatu ya kusa sannan Dad ya bashi kuɗi ya juya zai komawa ai kam Tajdeen yace bai san wannan ba.

Cikin shagwaɓar da ya ya koya tun farko zuwan shi cikin ahalin ya riƙe Dad yace "Please Dad kar ka tafi ka bar ni ban san kowa ba tsoro nake ji"rage tsawo Dad yayi cikin sigar rarrashi yace "ka zauna yanzu zan dawo ɗaukar ka da zarar kun gama karatu"kafaɗa Tajdeen ya maƙe yana mai shigewa jikin Dad,wani ɗan yaro ne daidai sa'ar shi ya taso daga inda yake ya kama hannun Tajdeen yace "Friend zo mu tafi ka ƙyale Dady"kallon Dad Tajdeen yayi ya jinjina masa kai alamun su tafi kafin ya shafa kansu yana mai tambayar yaron sunan shi "Junior"ya ba shi amsa,bye-bye suka ma Dad kafin suke zaunawa saman table Junior na yi ma Tajdeen hira har Madam ɗin da za ta koya masu ta shigo.

Karatu ta yi masu daidai yadda kwanyarsu za ta ɗauka,sosai kam suka gane dama sunayen abubuwa irin su dabbobi ,kujera,allon rubutu sune ta koya masu.

Lokacin shan iska na yi duk yaran suka nufi restaurant nan kowa ya shiga sayen abinda yake so.Tajdeen na cin biscuit ya dubi Junior yace "mi yasa duk ƴan garin nan fatar ku iri ɗaya ce tunda na zo ban ga baƙar fata ba,kuma na ji kuna Yaren Hausa?"amsa Junior ya bashi da "eh mu ba African people ba ne asalin ƴan Indonesiya ne yaƙi ne ya shigo damu ƙasashen baƙar fata" "minene Indonesiya?"Tajdeen ya sake tambayar shi"da hannu Junior yayi mashi alama da oho kafin yace "ni ma ban sani ba na dai ji Mama na faɗa ne".Kallon students ɗin Tajdeen ya shiga yi kamar mai son tantance wani abu zuwa can ya nisa yace "toh mi yasa ba'a sallah nan garin?"kallon ban gane ba Junior yayi ma shi hakan yasa Tajdeen miƙewa ya fara gwada mashi yana Allahu Akbar sai yayi ruku'u,dariya Junior yayi yace "minene kuma wannan?"tsayawa Tajdeen yayi yace "ita ce sallah a gida na ga Anya da Kakata suna yi kuma friday muna zuwa masallacin juma'a mu yi ibada da bautar Ubangiji"da sauri Junior yace "oh yanzu na gane nan kuma duk saturday ne muna zuwa gidan bautar Ubangij,tashi mu shiga aji lokacin komawa yayi"nan suka miƙe suka shiga Madam ta cigaba koyar da su har sai ƙarfe ɗaya ta yi sannan aka tashe su.

Tajdeen na ganin Dad ya ruga ya rungume shi cike da murna "ina abokin ka?"Dad ya tambaye shi "yanzu Mamarsa ta zo ta tafi da shi" "ok!to ya karatu ka na dai ganewa ko?"Dad ya faɗa yana jan shi zuwa mota,"eh sosai ma"nan Tajdeen ya shiga karanto ma Dad abinda aka koya masu inda bai yi daidai ba sai Dad ya gyara ma shi har suka iso gida.A zaune father yake yana duba jarida sai ji yayi Tajdeen ya faɗa jikinsa yana ihu, rungume shi  yayi yana jin son jikan nasa

yace "i miss You Deen shine ka tafi makaranta ba ka je ka yi min sallama ba ko?"zaman shi ya gyara kan cinyar father yace "ai lokacin kana bacci kuma Mom tace ka sha magani ne na barka ka huta"dogon hancin shi ya ja yace "haka ne maza tashi ka cire uniform ka zo ka ci abinci sannan ni ma ka koya min karatun da aka yi maku"da "toh"ya amsa ya nufi ɗakin Mom da gudu jaka a hannu yace "Mom na dawooo"rungume shi ta yi sannan ta cire masa uniform ta yi masa wanka ta saka masa kayan shan iska.Abinci ta fara bashi a baki sai da ya ƙoshi sannan ta fara mashi tambayoyi kan karatu.

Haka rayuwa ta cigaba da tafiya kullum Dad ke kai Tajdeen school in lokacin tashi yayi kuma ya ɗauko shi yayinda Mom ita ke koyar da shi lesson.
Kasancewar Tajdeen mai kaifin ƙwaƙwalwa tun dama can farko hakan yasa karatu bai bashi wuya dan yana fahimta sosai,a gida kuma kullum SHENNEL ɗin turanci da French ya ke kallo wannan ya ƙarfafa ma karatunsa inda a ƙarshen shekara ya zo na ɗaya cikin ajinsu.

Hutun shekara wato vacances da suka shiga shi ya ba Tajdeen damar zama kullum a gidan wannan lokacin ne kuma ya ƙara fahimta lalle Raj na baƙin cikin ganin shi a gidan hakan yasa bai sakewa a duk lokacin da Raj ke  wurin.

Shirye-shiryen bikin Raj bai ɗauki lokaci ba aka yi biki inda suka tare a gidan father ,tun shigowar Avani ba su taɓa shiri da Vani ba wato Mom duk dan saboda Tajdeen a cewar Raj father ya ɗauki soyayyya ya ɗorawa Deen yanzu ko sun haifi yara ba su da wani gurbi sosai cikin zuciyarsa,da yake ita ma Avani sokuwa ce sai tabi ra'ayin mijinta.

Tajdeen na da shekara goma sha biyu ya samu matsalar memory sakamakon dukan kawo wuƙar da Avani ta yi masa tana ta buga kansa ga katanga ita niyyata ta kashe shi kowa ya huta dan shekara cikin ta uku kenan da auren su har yanzu ba ta samu ciki ba.
Duka ahalin gidan tsaye suka yi cirko-cirko tsakiyar asibiti tunda Dr yace Tajdeen ya samu matsalar memory ba su tsaya jin ƙarin bayani ba duk suka ruɗe.
Dad ne ya shigo da mota a tsiyace ko wani ƙwaƙwaren parking bai yi ba ya fito,"mi ya samu Deen ɗin?"shine tambayar da yayi yana kallon Mom cikin kuka ta fara yi mashi bayani "mu na can gidan bauta ne sai Avani ta kira tace Deen ya faɗo daga sama ya mutu sai..sai...."kuka ne ya ƙwace mata jijigata yayi cikin tashin hankali yace "sai mi?"ganin ba za ta yi magana ba ne Rahul yace "sai muka dawo gida shine muka tarar da shi cikin jini,sai muka kawo shi asibiti nan Dr ya tabbatar ma mu da ransa matsalar memory ce ya samu"da sauri Dad ya dafe saitin zuciyarsa wace ke bugawa da ƙarfi tun lokacin da aka kira shi aka shaida masa.

Riƙe shi Rahul yayi yana ƙarƙafa masa gwiwa na su gode ma Allah tunda da ransa kuma kar su fidda ran zai samu sauƙi.Ihu suka ji game da kuka Tajdeen na kiran sunan Mom ,da sauri suka nufi room ɗin da aka kwantar da shi.
Ƙoƙarin tashi yake amman ya kasa,an naɗe kansa da bandeji sai ƙarin ruwan da aka maƙala masa a hannu.Rungume shi Mom ta yi tana hawaye tare shafar kansa,cikin kuka yace "Mom mi na yi ma Mom ƙarama..."kasa ƙarasawa yayi ya dafe kai  sakamakon wani irin sarawa da yayi mashi,jini ne ya shiga ɓulɓulo masa ta hanci daidai nan kuma Dr ya shigo ya nemi alfarmar su bashi wuri ya duba shi.Waje suka fito suka tsaya bakin ƙafo,kujera father ya samu ya zauna dan wani irin jiri ne ke ɗibar shi.Can wajen kamar rabin sa'a Dr ya fito murmushi kan fuskar shi yace "madallah an yi sa'a bai rasa memrynsa duka ba zai iya tuna wasu abubuwa waɗanda suka wuce kamar na 2ans/years  haka,sannan za'a sallame shi nan da 3days tunda jinin da ya toshe wani ɓangare na ƙwalwar shi ya samu ya fito sai dai wanda ba'a rasa ba"Dr ya faɗa yana mai miƙa ma Ranvir takarda da za'a sawo magani dan ya ga shine kawai ke da nutsuwa,"zamu iya shiga yanzu?"Dad ya tambaya kamar zai yi kuka "eh toh amman da dai kun bar shi ya huta"kai kawai Dad ya ɗaga gabanin ya kalli Rahul yace "ka ɗauki father ka mayar da shi gida zuwa gobe sai ku dawo"kai Rahul ya jinjina tare da cewa "Tom. amman in ana buƙatar wani abu fah?bari na kai shi sai na dawo" "kar ka damu ga Ranvir nan ai".
Miƙewa father yayi tsaye sannan yace "Vani wuce mu tafi tare sai ki girka abinda zaku ci ki tawo da shi"ya na gama faɗar haka yayi gaba,ba dan Mom ta so ba tabi bayan shi ya rage daga Dad sai Ranvir a asibiti.

Wani gigitacen mari ne ya kifa mata wanda sai ta ga gilmawar wasu taurari kafin ta dawo daidai ta kuma jin wani,cikin ɗaga murya ya ke mata masifa akan bugun Tajdeen da ta yi.Ya daga hannu zai sake kwaɗa mata wani marin father yace "ya isa haka Rajjj!"saurin juyowa suka yi dan ba su san da shigowar su father ba sai jin murya shi da suka yi.
Takowa yayi har tsakiyar falon ya nuna Raj da yatsa yace "duk laifinka ne da ace baka nuna ma Tajdeen tsana ba da matarka ba ta yi kuskuren taɓa lafiyar shi ba,amman ba komi duniya ce"ya faɗa yana mai wucewa part ɗinsa Rahul ya take masa baya.
Kallon ido cikin ido Mom ta yi ma Avani ta goge ƴar ƙwallar da ta ciko idonta sannan ta wuce kitchen,tsaye ta yi ta rasa mi ke mata daɗi ashe bugun Deen Avani tayi shine ta yi mata ƙarya tace faɗowa yayi a zuci tace 'kenan shine binda Deen ke son faɗa min?'......

****Maraɗi

Sai bayan sallah Zuhur malam Nur ya shigo gida, kyakkyawar tarba ya samu gun amaryasa Nazifa.Bayan sun gama cin abinci ne suka fara ɗan taɓa hira da Samira wacce ta zo ta taya ƙawarta aiki,kallon malam Nur Nazifa ta yi tace "ɗazu anty Sappa ta shigo nan"dariya yaƙe yayi

ya na jin zuciyarsa na bugawa "toh Masha Allah mi ta kawo maki?" "hira mana dan ta jima nan kafin ta koma part ɗinta" "to yayi kyau"shine abinda malam Nur ya faɗa "ya kamata ka tashi ka dubo ta tunda ka shigo baka leƙa ba"cewar Nazifa ta na mai komawa kusa da Samira ,ba tare da yace komi ba ya miƙe ya nufi part ɗin Sappa can ƙasar zuciyarsa kuma ya na jin daɗin zuwan  da ta kai ma sahibarsa.

A zaune ya tarar da ita ta na kallo tana ganin shi ta miƙe tana mai mashi barka da zuwa,amsawa yayi yana mai tambayar ta yadda ta wuni  ta amsa mashi da alhamdullah.
Ruwa masu sanyi ta ba shi kafin tace "ko na zuba maka abinci ?yanzu anty Nazifa ta aiko min shi"cike da jin daɗin haka ya sakar mata murmushi yace "no na ƙoshi sai dai zuwa an jima"baki ta turo tace "da fah an yi sallah la'asar ƴan damu za su zo gidan zai cika da jama'a ina zan ganka balle na baka abinci" "toh sai ki aje har baƙin su tafi,yanzu dai miƙo min télé commande/remote"miƙa mashi ta yi ta zauna kusan ƙafafunsa tana kallon yadda ya ke binciko tashoshi.

Zuwa bayan la'asar aka fara gudanar da Damu kamar yadda al'adar Maraɗi take a duk sadda aka kai amarya ga washegari ƴan uwa da abokan arziki sukan taru gidan amarya danginta su bayar da kyaututtuka ga dangin ango.
Bayan an gama gudanar da bikin Damun,dangin Sappa suka rakota har ɗakin Nazifa suka damƙata amana tare da yi masu nasiha.
Malam Nur ma da ya zo haka ya tara su ya gindiya masu sharaɗan zama gidansa tare da doguwar nasiha mai ratsa jiki.

Sai da malam Nur yayi sati guda cur a ɗakin Nazifa sannan ya koma ɓangaren Sappa ita ma yayi sati guda,daga nan suka yi rabon kwana biyu-biyu.
Tun daga lokacin bikinsu babu abinda ya haɗa su na rashin jituwa, Sappa na bin Nazifa sau da ƙafa wannan yasa ta ciri tuta gun malam Nur har ya faɗa cikin kogon sonta ba tare da ya sani ba.

Tun safiyar yau Nazifa ta tashi da wata irin kasala da zazzaɓi,tun tana daurewa har ta kasa hakan yasa ta nufi part ɗin Sappa.Ƙwanƙwasa ƙofa ta yi amman ba'a amsa ba hakan yasa ta cigaba da bugawa da ɗan ƙarfi,jin an buɗe ƙofar yasa tayi saurin ɗago kanta Sappa ce sanye da rigar bacci iya cinya.Hamma ta yi ta kalli Nazifa ta yamutsa fuska tace "yaaa lafiya irin wannan dukan ƙofa?"
"Banda lafiya ne"Nazifa ta bata amsa kamar za ta yi kuka "to sai aka yi yaya? Ni na ɗora maki ciwon ne da za ki wani kwaso jiki ki zo gaya min?"da mugun mamaki Nazifa ke kallonta kafin tace "ki kira min shi ya kai ni asibiti"kallon baki da hankali Sappa ta watsa mata tace "barci yake

kuma saboda wata banza ba zan tada mijina ba"gammm ta rufe ƙofa ta bar Nazifa sake da baki.

Ganin tsayuwar ba ta yi mata yasa ta koma ɗaki,kuɗi ta zuba a jaka ta kulle ɗaki ta nufi bakin titi.Ba jimawa ta samu abun hawa asibiti Agaji ta tafi bayan ta ga likita yayi mata tambayoyi,nan yayi ƴan rubuce-rubuce ya bata takarda ta sawo alluran da za'a yi mata ta dawo .
Allura ruwa ya saka mata dandanan barci ya ɗauke ta ,ko da ta farka ƙarin ruwan ya ci rabi.Text ta yi ma Samira ba jimawa sai ga ta tazo, result ɗin likitan ya shigo ya bata tare da yi mata congratulations.
Cike da murna Samira ke karanta farar takardar da sakamakon ya nuna Nazifa na ɗauke da ciki na tsawon wata biyu.......

Please share
[21/05 11:57] MRS SADAUKI: *SHAUKIN SO*💘

```LoVe story```💟

By
Chamsiya Laouali Rabo
{MRS SADAUKI💫✍️}

*FCWA*☀️

___________________________

Page 15-16

Cike da mamakin ganin ta kulle part ɗinta malam Nur ya ciro waya ya danna mata kira,bugu biyu aka ɗaga tare da yin sallama amsawa yayi yace "ina kuma kika tafi na ga ƙofar gidanki a rufe?"
"Ina asibiti"ta bashi amsa "asibiti? Shine ba ki kira ni na zo na kai ki ba ? Shine kika fita ba da izinina ba saboda kin isa da kanki ko mi?"a yadda yake maganar za ka gane cikin zafin rai ne ya ke yinta hakan yasa Nazifa ta sanyaya murya tace "babyn ka ne ya matsa min tun safe nake jin kasala ga kuma zazzaɓi shine na zo asibiti sai kuma aka tabbatar min da zaman shi"wata sanyayar ajiyar zuciya ya sauke a ɗan bayaninta ya gane so take tace masa ta na ɗauke da ciki
```

"to kuma Naziii shine ba zaki kira ni mu je tare ba?"murmushi ta yi jin ya sauko daga dokin zuciya tace "dan kar na shiga haƙin ƴar uwata ne shi yasa,ya ne kun tashi lafiya ina amarya?"bai amsa gaisuwar ba sai tambayar ta asibitin da ta je yayi,tana gaya masa ba'a fi minti goma ba sai gashi ya zo baki buɗe yana fara'a kamar gonar auduga.

Gaisawa da Samira yayi nan ta shiga zolayar shi kai kace ba malaminta ba ne, fuskar Nazifa ya shafa ya na jin wani farin ciki na luluɓe shi.
"Mu ga cikin?"ya faɗa can ƙasan maƙoshi ta yadda ita kaɗai za ta ji,kallon shi ta yi ta turo baki tare da yi masa alama Samira fah na nan.Inda Samira ke zaune ya waiga sai ya ga hankalinta sam ba ya gare su waya take dannawa hakan yasa ya ɗan ɗaga rigar Nazifa ya shafi mararta yace "ya aka yi ban gan shi ba?"sake da baki Nazifa ta kalle shi tace "wai mi ba dai cikin ba?"gira ya ɗaga mata yace "eh mana"dariya ta shiga yi kafin ta tsagaita tace "duka wata biyu ne fah,kuma har kake tunanin ya fito?"
"To sai yaushe kenan?"kafin ta bashi amsa kira ya shigo wayarsa ɗagawa yayi bakinsa da sallama sai dai bai kai ƙarshenta ba ya yanke sakamakon jin kukan Maman.

Fita yayi waje yana mai tambayar lafiya "Alhaji ne ba lafiya sai suratai yake dan Allah ko mi kake ka tawo,ciwon na shi sai tsananta ya ke"Maman ta faɗa cikin kuka

"innalillahi wa'inna ileyhi raji'un"shine kawai abinda malam ya faɗa ya kashe wayar .Komawa ciki yayi ya shaida ma Nazifa Baba ne bai jin daɗin jikinsa ,nan yayi mata sallama tare da ba ta kuɗi in buƙatar hakan ta taso.

"Dan Allah Alhaji ka bar min maganar wasiya nan ai ciwo ba mutuwa ba ne,in ka mutu ka bar ni ina zan sa raina?"Maman ke faɗar haka tana kuka gefenta Balkis ce ita ma tana rera nata.Sallama yayi basu amsa ba,cikin halin kaɗuwa ya nufi mahaifin nasa wanda ke kwance tsakiyar falo sai hawaye yake zubarwa.
Kansa malam Nur ya tallabo ya ɗora saman cinyarsa yana goge hawayen da ke zuba kan fuskarsa ,cikin rawar murya yace "Baba mine ne na kuka maimakon addu'a? Ka yi shiru ka bar zubar hawaye in shaa Allah za ka samu sauƙi yanzu nan zan kai ka asibiti"kai Baba ya girgiza yace "Nuradeen ciwona ba na asibiti ba ne,abu guda ke damun raina tun shekaru ashirin da suka wuce shi nake ma kuka domin ban san mi zance ma ubangijina ba duk da dai ba yin kaina ba ne "cikin sigar rarrashi malam Nur yace "No Baba zafin ciwo ne ni na san babu wani abu da za ka aikata marar kyau da har Ubangij zai hukunta ka,ka bari kawai na kai ka asibiti"murmushin takaici Baba yayi yace "miyasa ba zaku fahimce ni ba?zuciyata ciwo take min saboda nauyin abinda nake ɓoyewa ku bar ni dan Allah na faɗa maku ko zan ji sanyi"
"Minene kake ɓoyewa Baba wanda har mu ba mu san shi?"
"Wata babba ƙaddara ce da ta taɓa abkuwa gare ni, Allah ya jarabce ni da son yin mata biyu

amman mahaifiyarku ta hana duk lokacin da na yi yunƙurin ƙara aure sai ta rogaza shi abun takaici kuma ita ta kasa kula da ni kuma ta hana ni auro wadda za ta ɗebe min kewa.Da ƙarfi da yaji ta sa na lizimci yin azumi dan kauce ma hanyar ɓata da farko na samu sassauci sai kuma daga ƙarshe Rahanatu ta shigo rayuwata lokacin da na fara kasuwanci Kano-Kano ina saro kaya.Tun farko da aure nake sonta amman ganin hakan ba zai samu ba sai sheɗan ya buga min ganga na bi ruɗinsa ita ma da yake tana sona sai ta biye min wajen aikata kuskuren da har ƙarshen rayuwata ba zan daina nadama ba.Ɓullowar cikin Rahinatu shi ya fargar damu cewa saɓon Allah ne mu ke aikatawa mafi muni,kafin muyi tunanin zubar da cikin mahaifanta tuni sun san da zaman cikin kawai sai suka kira ni da zancen doli sai na auri Rahinatu ko kuma su maka ni kotu banda wani zaɓi na amince ta na haihuwa aka ɗaura mamu aure..."wata irin shaƙa Maman ta yi ma Baba tana cewa "au mi?aure fa kace?ai gwara na kashe ka da na ida jin wannan mummunan labarin"

Dakyar malam Nur ya ƙwaci Baba nan ya shiga tari ya kuma ɗora da faɗin "ai duk laifinki ne ko ma minene ke kika jawo Allah ya shaida ban aure ki ba sai dan ina son ki kuma ki haifa min ƴaƴa amma kika biye ma ra'ayinki na yara uku kawai za ki haifa duk gudun kar ki tsufa,saɓanin Rahinatu da ta haifa min yara ɗaiɗaya har bakwai kuma duk maza"wani irin ihu Maman ta yi jin abinda Baba ke faɗa,ririƙeta Balkis ta yi yayinda malam Nur ya ciciɓi Baba ya nufi waje sakamakon jini da ya fara amayarwa .

CLINIC HAMDALLAH tafi kusa da gidansu hakan yasa ya nufi can,taimakon gaggawa suka shiga baiwa Baba cikin ikon Allah jinin ya bar zubowa.Oxygen aka maƙala masa sannan suka fito da shi ɗakin hutu,cike da tausayin mahaifin nasa ya zauna gefen gado tare da kamo hannunsa ya jimƙe.Zantukan Baba ne suka shiga yi masa kai komo cikin kwanya, tabbas dattin Zina ba zai taɓa gogewa ba ko da kuwa ka tuba akwai wannan tabon amman wani sa'in babu yadda mutum zai yi da zanen ƙaddara doli sai haƙuri da roƙon Allah yafiya da kuma tsari.

Wasa-wasa sai da aka yi ma Baba ƙarin ruwa wajen sau bakwai a ranar,tun malam Nur na tsimayen farkawara har ya fidda rai.
Ya na dawowa daga sallah magrib ya tisa Baba gaba yana kallo,wata ƙwalla ce ta zubo masa wadda ya kasa tantance ta mi cece,ta tausayin Baba?ko kuwa ta farin ciki ce jin ya nada wasu ƙannai bayan Balkis?.Motsi Baba ya fara yi da hannu gabanin ya buɗe ido,kusa da shi Nur ya matsa suna kallon juna.
Cikin murya ta maras lafiya Baba yace "ka yafe min Nuradeen mahaifinku bai so ya kasance mazinaci ba,na bar maku mummunan tabon da zai rinƙa bibiyar zuri'arku har ƙarshen duniya sai dai ka sani ba yin kaina ba ne wlh rabon a yi ne , Allah na gani tun ina ɗan saurayina ban yi ta ba sai bayan na mallaki hankalin kaina..."ƙyalewa Baba yayi tare da rumtse ido jin saukar hawayen malam Nur kan fuskarsa.

"Na sani Baba ni shaida ne a kan halayenka,kullum ka kasance mai min gargaɗi daga sharrin Zina tun kafin na san mi kalmar take nufi har ya kai na santa.A kullum a ko da yaushe ina alfahari da kai a matsayin mahaifi ka bani tarbiyya ta gari duk da tarin dukiyar da kake da a kullum kana nusar da ni dogaro da Kai yafi zaman jira,ka nuna min dukiya ba komi ba ce fa ce dauɗar duniya..."da sauri Baba ya lalubo hannun malam Nur yace "tabbas dukiya ba komi ba ce dan ba komi take saya ba,akwai kuma ranar da ba tada amfani ga mai ita ka ɗauki darasi a kaina milliards nawa ke a kwai cikin asusun bankina amman gani a kwance rai hannun Allah kuma na san ba za ta tsinana min komi ba nan da ɗan lokaci zan barta na koma ga mahallacina"kai malam Nur ya girgiza yace "no Baba ba za ka mutu  ka bar ni ba ka fi kowa sanin ina sonka fiye da komi, Please ka bar maganar mutuwa na gaya maka zafin ciwo ne kuma in shaa Allah za ka samu lafiya"

Wani murmushi Baba yayi yace "Allah bai barin wani dan wani ya ji daɗi Nuradeen,ka riƙe ƴan uwanka ka zamo masu BANGO(MRS SADAUKI )sannan kafin ku raba gado ina so ku baiwa Suleyman gida guda da wani kaso na kuɗi duk da ya na shege jinina,ka ce ma Mamarka ina sonta har kullum ta kula min da Balkis kar ka aurar da ita da mutumen banza,ina sonk...."tari ne yaci ƙarfin Baba yayinda na'urar da ke manne da bango ta fara ƙara tiii-tiii jan layi na fitowa,cikin azama malam Nur ya tallabo kan Baba yana mai maimata masa kalmar shahada shi kuma ya na biyawa daidai nan likitoci suka shigo suka tsaya wuri guda suna kallon danjar da ta nuna jan layi alamu rai yayi halinsa.

Ido malam Nur ya shafe ma Baba yana mai jan zane zai luluɓe shi likitocin suka ƙaraso,gefe ya zauna yana kallon sarautar Allah shikenan Baba ya rasu "innalillahi wa'inna ileyhi raji'un"shine kawai abinda ya ke maimaitawa.
Wayar ɗaya daga cikin likitocin ya ara dan tasa ta faɗi lokacin da ya ciciɓi Baba,malam Jabeer ya kira yana ɗagawa yace "ka zo ka same ni CLINIC HAMDALLAH Allah yayi ma Baba rasuwa"bai jira ta cewar shi ya kashe kiran.Ba'a ɗauki lokaci ba Malam Jabeer ya ƙaraso,ambulance aka saka gawa Baba aka kai shi babba asibiti ta Maradi,GIDAN GAWA(MRS SADAUKI) na sanyi aka shiga da shi aka laya shi kusa da gadajen matattu waɗanda wanda suka riga mu gidan gaskiya.

Malam Jabeer ke tuƙi yayinda malam Nur ke zaune kusa da shi ,ko gama parking bai yi ba mutane suka nufo motar dan duk illahirin unguwar ta ɗauka Alhaji Ali Ɗan Masani wanda  kuma shi ne Liman bai da lafiya.Jiki ba ƙwari malam Nur ya fito nan aka fara tambayar shi ya mai jiki "ciwo ya warke"shine kawai abinda ya faɗa nan wuri ya ɗauki kabbara.

Ya na shiga cikin gida ya ci karo da Maman wacce kabbara mutane  ce yasa ta saurin fitowa,ba

ta samu damar tambayar malam Nur ba ya wuce ta ko kallonta bai yi ba Malam Jabeer ne ya sanar da ita rasuwar Baba.

Tun cikin dare malam Nur ya shiga shaida ma ƴan uwa na nesa da na kusa rasuwar Baba,wasu tun lokacin suka ƙaraso ba'a ɗauki lokaci ba gidan ya cika da ƴan gaisuwa.
Miss call ɗin mutane ya shiga dubawa rabin su duk na Nazifa ne, text yayi ma Sappa ta zo gida ba jimawa kuwa ta zo nan ta tarar da tashin hankali,bai cikin nutsuwarsa hakan yasa malam Jabeer kai shi gida.
Kwance ya tarar da Nazifa tana kwana ledar magani kusa da ita,ɗaukar ta yayi ya maida ta bedroom sannan ya shiga wanka.Sallah isha'i ya gabatar sannan ya dawo falo ya fara karatun alƙur'ani,ya jima sosai yana karatun sannan ya koma jan casbi.Ranar nan yadda ya ga rana haka ya ga dare ko kaɗan kwana bai gigin zuwa wurin shi balle har ya sace shi,ya na nan har aka yi assalatu yayi alwala ya nufi masjid.Sai bayan ya dawo ya tada Nazifa tayi sallah,wanka yayi yace ta shirya za su fita.
A ƙofar gidansu ya sauke ta wanda aka share tass kamar ranar sallah, zuciyarta ce ta tsinke ta waigo ta kalle shi ido ya rumtse yace "fita ki shiga ciki"ba muso ta fita.

Malam Nur tare da wani ɗan uwan Baba su suka yi wankan gawa suka suturtata sannan suka yo gida da ita aka sallaceta sannan aka kai Baba gidansa na gaskiya.Motoci na dawowa malam Nur ya fito ya dubi ɗumbin jama'ar da suka zana'izanci gawar Baba,sai a lokacin ya ji wasu hawaye masu ɗumi kan kumcinsa.
Da sauri malam Jabeer ya riƙe shi ganin kamar zai faɗi,suna shirin shiga gida sai ga yaran Baba na Kano sun nufo malam Nur ashe tun da safe suka zo sam shi bai ma san da zuwan su ba,jiya dai ya shaida masu rasuwa mahaifinsu.
A tare suka shiga cikin gidan tun daga nesa Maman ta tsinkaye su, tabbas waɗannan sune ƴaƴan Rahinatu dan kamar su ɗaya da Nuradeen.Yunƙurawa ta yi za ta miƙe Ummu Sappa ta mayar da ita tana girgiza mata kai,kuka ne ya kubcewa Maman tana jin zuciyarta na suya.

Nuradeen kuwa shi da ƴan uwansa suka shige ɗaki suna rarrashin juna,malam Jabeer na basu haƙuri tare da  yi masu wa'azin mamaci addu'a ya ke buƙata.
Sun daɗe haka kafin su ba kansu haƙuri da juriya su koma waje suna karɓar gaisuwa.

Ranar sadakar uku Inna ta samu ta yi wa Maman gaisuwa da sauran jama'a kafin take komawa gida, Nazifa wuri guda ta samu ta takure dan bata san kowa ba saɓanin Sappa da ya ke gidansu.Duk lokacin da suka haɗa ido wani banzan kallo Sappa da ƴan uwanta ke jifarta da shi,ganin haka yasa Nazifa tafiyarta gida wanda hakan da ta yi ya tunzura Maman tana ta

zaginta a ƙarshe ma bayan mutane sun watse ta yi mata gami malam Nur,cikin son kare matarsa  yace "Maman kin san ba ta jin daɗin jikinta sakamakon juna biyun da take da"cikin masifa tace "gareta farau yin juna biyu?kawai ta raina mutane ne inda ubanta ne ya mutu ai da yanzu ka na can kana baƙar wahala da su"malam Nur dai bai ce komi ba ya ficewar shi.

40days Ago

Wani sabon gini aka ɗora cikin gidan malam Nur wanda bai wani ɗauki lokaci ba aka gama aka yi masa penti,cikin rana guda aka kwaso kayan Maman aka maido su ciki.
Cike da murna dawowar Maman gidansu Sappa ta shiga ta gaishe da Maman nan suka fara taɓa hira ita da Balkis wacce rabinta duk ɓata Nazifa ne take gun su.Duk hirar da su ke Maman na jin su da sauri ta ɗago tace "miiii?gori fah?"cike da jin daɗi Sappa tace "wlh Maman gori ta yi min tace wai ni juya ce ban iya komi ba sai dai na ci na kai masai"ƙyaci Maman ta yi tace "eh lalle ki ce yarinya ta girma ta isa yanka,yanzu har ta kalli tsabar idonki ta yi maki gori?"kai Sappa ta ɗaga tace "wlh Maman ba ki san ta raina mutane ba sai kin ga yadda take sa Ustaz aiki kamar Ɗan da ta haifa,jiya fah wankin kaya yayi mata"

Ƙirji Maman ta dafe tace "ke mi wanki?" jin sallamar malam Nur yasa Sappa ƙyalewa amsawa suka yi,ya shigo Nazifa na biye da shi a baya.Durƙusawa ta yi tace "ina wuni Maman da fatan kun zo lafiya?"sheƙeƙe Maman ta kalleta tace "mun zo lafiya?balaguro na yi?Ni da gidan Ɗana kike min wani sanu da zuwa?oh!nufinki na zo zan takura maki ko baki so zuwa na ba"cikin girgiza kai Nazifa tace "a'a Maman ba haka nake nufi ba,dama gaishe ki ne na zo na yi"
"To na gode madallah a tashi a tafi"miƙewa Nazifa ta yi tana kallon malam Nur wanda yayi sumen tsaye.........

Please share
[21/05 12:33] MRS SADAUKI: *SHAUKIN SO*💘

```LoVe story```💟

By
Chamsiya Laouali Rabo
{MRS SADAUKI💫✍️}
```

*FCWA*☀️

---

Page 17-18

Cikin rashin jin daɗin abinda Maman ta yi ma Nazifa malam ya juya zai bin bayanta Maman ta shiga taɓa hannuwa tana salati,tsayawa yayi ba tare da ya ƙara ko taku guda ba ne."A'a je ka,tafi bi bayanta sai ka tabbatar min kai mijin tace ne"cewar Maman dawowa yayi ya zauna,kallo guda yayi ma su Balkis suka miƙe suka bar wurin.Kafafun Maman ya dafa zuciyarsa na suya yace "kiyi haƙuri Maman sam hakan da kika yi bai dace ba,Naziii na bakin ƙoƙarinta wajen kauce duk wata husuma, na lura tun ranar sadakar uku ta Baba da kika ƙullice ta har yanzu baki sauko ba,a madadinta ina mai baki haƙuri..."saurin katse shi Maman tayi da cewa "ni ce mai tada husumar ko? Saboda matarka kake gaya min magana har da cewa na ƙullace ta?" "A'a Maman ba haka nake nufi ba wlh,kawai abinda kika mata ne yanzu bai dace ba a matsayinta na surukarki ni ina ganin da ni da ita ai duk ɗaya ne a gun ki"hannuwansa Maman ta jaye daga kan ƙafarta tace "ka tashi ka tafi kar jininka ya hau ka zage ni"da sauri Ustaz yace "subahanallahi zagi kuma Maman ?" "Eh mana tunda an taɓa ƴar gwal ba zagina ba ai ko dukana sai ka yi".

Murya malam Nur ya ƙara sanyayawa yace "Allah ya huci zuciyar Ummu Nur, Allah ya baki haƙuri zan fita malam Jabeer na kirana kin san Yau za'a kai kuɗin aurensa"yana gama faɗa ya miƙe tsaye Maman kuwa ta washe baki tana cewa "ah-ah Masha Allah ashe yarona an kusa zama manyan mutane?toh Allah sa dai ta kirki ce zai auro Allah kuma yasa alkairi alkairi"da "Amen"ya amsa yayi ficewar shi.

Sai bayan sun dawo daga kan kuɗin malam Jabeer ne ya shiga gun Nazifa,waya ya tarar da ita suna yi ita da Samira.Kashe kiran ta yi ta tarbi mijinta "har kun dawo?Masha Allah yau burin ƙawata ya cika malam Jabeer ya kai sadaki sai fatan kuma Allah ya nuna mana ranar biki"Nazifa ta faɗa murmushi kan fuskarta,shi ma murmushin yayi yace "shikenan sai mu huta da mita kullum sai yayi min hirarta sai kace gare su farau soyayya"

Dariya Nazi ta yi tace "ai bai kai nacinka ba ko ka manta lokacin da muna soyayya kullum ka na gidanmu kuma hirarka ba ta wuce NazNur"tunda ta fara magana ya tsaya yana kallonta kamar

yau ya fara ganinta,jin bai ce komi ba ta ɗan daki ƙirjinsa tace "ya dai?"numfashi ya sauke yace "ba komi kawai ina tunanin babyna ne,ko da wa zai kama cikin Ni da Ke?"
Dubansa ta yi tace "in namiji ne da kai zai yi kama in kuma mace ce da ni za ta yi kama" "na fi son ki haifi namiji Saboda buri biyu,na farko don na saka masa sunan Baba, na biyu kuma don na samu aboki"cikin rashin jin daɗin zaɓen da yayi na cewar ya fi son namiji tace "ka bar ma Allah zaɓi dai shi ya fi,in kuma na haifi mace sai yaya kenan?"miƙewa yayi tsaye yace "in shaa Allah namiji ma ne,sai da safe ki zo ki rufe ƙofa"ya faɗa yana mai ficewa saboda yau Sappa ce da girki.

★

Kicin-kicin ta yi da fuska kafin a shagwaɓe tace "yanzu saboda Allah SapNur sai yanzu za ka shigowa bayan ka san yau ni ce da girki shine ka tafi can ka yi zamannin ka?"sam malam Nur bai kulata ba sai ma dariyar sunan SapNur da yaji tace sai ya ji sam bai yi daɗi ba.Cikin jin haushi Sappa ta biyo shi ɗaki sai aka yi rashin sa'a har ya shiga wanka har za ta tafi kuma komi ta tuna sai ta dawo ta zauna.Bai jima ba ya fito ɗaure ta towel, jallabiya ya saka yayi Sallah raka'a biyu sannan ya fara tilawar alƙur'ani mai girma.
Wani maƙoƙon baƙin ciki ne ya tokare ma Sappa maƙoshi,cikin jin haushi ta ɗaga murya ta yadda zai jita tace "malam alhuduhudu ai ka dakata da karatun ka ji da lamurran matarka,koko har yanzu ilimin naka bai sanar da kai darajar mata a gun mijinta ba?"kamar zubar narkakar dalma haka malam Nur ya ji maganarta ,cak ya tsaya daga karatun da ya ke ya waigo inda take zaune ta hakimce bakin bed tana kalkaɗa ƙafa.Ido ya rumtse ya ci gaba da karatu ganin haka yasa Sappa yin tataki har inda ya ke ta tsaya masa a kai tace "da kai fah nike"yadda ta yi maganar tamkar uwarsa yasa ya harzuƙa ya miƙe ya kwaɗa mata mari tare da nunata da yatsa yace "ki shiga hankalinki tun kafin ki sa na aikata abinda ba ya cikin tsarin rayuwata,wlh in kika ci gaba da wannan shirmen zan maki ɗan banzan duka get out..."jiki na kyarma Sappa ta fita ba shiri,tana shiga ɗaki ta fashe da kuka tana cewa "na shiga uku ni Sappa wato duk yadda zan yi maka ban yi daidai ba na yi maka kissa da rangwaɗa ka wani share ni,na nuna maka fushina ka koro ni "taɓata ta ji an yi da sauri ta juyo suka haɗa ido,alama yayi mata da ta zo gare shi ba muso ta faɗa ƙirjinsa.Bayanta ya bubuga yace "toh ki yi shiru mana ba gani ba ko baki so na komawa ta ne?"kai ta girgiza yace "to na ji ba zan tafi ba amman ya kamata ki san yadda za ki rinƙa yi ma miji magana sannan ki rage saurin fushi duk abinda lalami da rarrashi bai bayar ba to tashin hankali ba zai saka shi ba"ajiyar zuciya ta sauke tace "toh"kulawa ta musamman suka shiga baiwa junan su tamkar ba yanzu suka yi faɗa ba,hakan kuma yana ɗaya daga cikin jajircewar malam Nur na kwatanta adalci tsakanin matansa ba tare da ya tauye haƙin ɗaya ba.

***JOS

Sosai jikin Tajdeen yayi sauƙi kasancewar ya na samun kulawa ta musamman daga iyayensa,tsakanin shi da Avani da Raj kuwa sai gaisuwa ita ma ba kullum ba .Duk da yanzu

Avani ta rage jin haushin Tajdeen sakamakon cikin da likita ya tabbatar mata da shi,da sannu ta fara jawo Tajdeen jikinta abun ka da yaro sai ya manta cutarwa da ta yi masa ya ke zuwa gun ta sai dai da zarar Raj ya shigo ya ke fitowa saboda kallon tsanar da ya ke jifar shi da kuma faɗan da ya ke ma Avani dan mi take bari ya na shigowa.

Cikin Avani na shiga wata tara da ƴan kwani ta haifo kyakyawar ƴarta mace mai kama da turawa,tun a ranar da aka haife ta aka yi mata laƙabi da *Mari* sai da aka ɗauki wata biyu sannan aka yi biki.
Tunda Mari ta zo duniya Tajdeen ya ɗauki son duniya ya ɗora mata,kullum ya na ɗauke da ita in kuma ya tafi makaranta bai da hira sai ta Mari dan wasu abokanansa  har zuwa su ke kawai dan su gan ta.

Zaune suke tsakiya falo ya sa Mari gaba sai wasa ya ke mata ita kuma tana wangale baki ta na masa dariya,kuka ta fara alamun ta gaji yunwa take ji hakan yasa Tajdeen ɗaukar ta ya nufi part ɗin Avani da ita ya na ɗan ririgata.
"Mi ka yi mata take kuka iyeee?"Raj ya tambaya kamar zai kashe Tajdeen,shiru yayi bai ce komi ba sai jikinsa da ya ɗau rawa dan har ga Allah tsoron Raj ya ke.Wani gigitacen mari Raj ya sauke ma Tajdeen wanda yayi sanadiyar ɗaukewar numfashinsa na wucen gadi,wata irin ƙara Tajdeen ya ƙwalla tare da sakin Mari bai shirya ba.A gudane ya nufo waje jini na yi masa zuba ta hanci,karo suka ci da Mom wadda ƙarar Tajdeen ta caki ƙahon zuciyarta ta nufi part ɗin Avani.Jikinta ya faɗa ya na kuka,saurin ɗago shi ta yi tana bubuga goshinsa dan tsayar da jinin amman abu ya cuttura.Ruwan sanyi father ya ɗauko tare da wanke masa fuskarsa nan jinin ya tsaya,father na shirin shiga part ɗin Avani dan zaƙulo Raj sai Dad ya riƙe shi ya girgiza mashi kai " ba komi ba ne ake ɗaukarwa mataki,Deen tamkar  Ɗa ya ke gun Raj ya na da incin hukunta shi ƙila laifi yayi masa"ya na faɗin haka ne tare da jawo hannun father zuwa kujerar zaman shi.Cike da jin haushi Mom ta harari Dad murmushi kawai yayi mata,lamo Tajdeen yayi yana shasheka kafin daga bisani barci ya ɗauke shi.

Washe gari bayan Dad ya sauke Tajdeen school sai ga shi da wasu takardu ya na yi ma father bayani,shi kuma huci  ya sauke yace "ban ƙi ta taka ba Jean amman ka na ganin shi Deen ya na son aikin soja?kuma mi zai hana ka bari har sai ya girma?"kai Dad ya girgiza yace "a'a father gwara ya tafi tun yanzu dan zai fi samun horo mai kyau kuma hankalinsa da namu zai fi kwanciya"
"To Allah ya taimaka ita Vani ɗin ta yarda?" "Ban kai ga gaya mata ba sai yanzu ".

Sosai Mom ta yi murna da maganar da Dad ya zo mata na tafiyar Deen makarantar horon soja,hakan ya sa Tajdeen na zuwa ta shaida masa nan ya hau kuka yace shi aikin likita ya ke so cikin rarrashi Mom tace "Ɗana Deen aikin soja da na likita duk ɗaya ne"cikin kuka yace "a'a Mom na yi ma...na yi alƙawari"sai kuma ya ƙyale ya na jin kan shi na sara masa sakamakon

wani abu da ya so ya tuno kuma ya kasa.Zuciyar Mom kuwa lugude ta shiga yi dan ita har ga Allah ba ta son ya na yi mata zancen Anya kuma babu shakka ta tabbata abinda ya ke son faɗa kenan,ɗaki ta kai shi ta ɓalli maganin shi ta ba shi dandanan barci ya ɗauke shi.
Da ya farka da maganar zuwan shi aikin soja ya tashi,cike da murna Mom ta rinƙa kwaɗaita masa aikin.
Farin cikin da ya ga ta na yi shi ya zame masa ƙwarin gwiwa,hakan ya sa ya ɗaura ɗamarar kasancewa kamar yadda su ke so.

Abu kamar wasa sai ga Tajdeen luntsum cikin makarantar yara ta sojoji wacce ke babbar jaha ta Abuja,sosai kasancewar shi a nan ta yi ma shi daɗi duk da baƙar azabar da ake gana masu amman samun abokan ƙwarai ya sa shi jin daɗin rayuwar,gefe guda kuma ya na jin kewar gida da soyayyar ƴar ƙanwarsa.
Kwance Tajdeen yayi bayan ya fito daga wanka,lumshe ido yayi gidan su na yi masa gizo bai ɗau wani lokaci ba barci ya ɗauke shi mai cike da mafarka iri-iri,duk cikin su guda ne ya tsaya masa ba wani mafarki ba ne yayi fa ce na yanzu girma ya zo masa alƙalami ya hau kansa.Kasancewar shi yaro shiyasa bai gane komi ba dan a lokacin shekarar sha biyu da wasu watanni za'a iya cewa yanzu cikin 13years ne yake,wani wankan ya sake yi ba wai na yadda addini ya sharanɗa ba a'a sai dan kawai wanke ƙazamtar jikinsa.Cikin wani irin yanayi na shiga sabon zangon rayuwa ya shirya tsaf ya nufi filin da ake buga wasa,tun kafin ya ƙaraso Irfan da Faruk suka yi masa alama.
Hannu ya basu suka gaisa sannan ya zauna suka cigaba da kallo,Irfan ne ya kalle shi yace "Deen sai na ga kamar yau ba ka cikin walwala why?"murmushi kawai yayi yace "ba komi"ba dan Irfan ya yarda ba ya ƙyale shi dan sam ba haka ya san Tajdeen ba.
Har aka gama ƙwallon Tajdeen bai ce ufan ba Irfan da Faruk kawai ke hira,tun su na tambayar shi lafiya har su ka ƙyale dan sun lura Deen irin mutanen nan ne masu zurfin ciki.

Ko da dare yayi bayan sun gama cin farar Macaroni da mai da maggi wata hira suka ɗora inda Tajdeen ya haye ɗan ƙaramin gadonsa ya faɗa tunanin yarinyar da ya gani cikin mafarki jefi-jefi kuma ya na sauraron hirar abokansa.

Yayi nisa a cikin tunani ya ji Faruk na cewa "Ni kam Tajdeen na tambaye ka"ba tare da ya juyo ba yace "um ina jin ka"
"Miyasa ba ka yin sallah ne kullum sai na ga ka yi wanka ka shafa mai?"ita ce tambayar da Faruk ya jefo ma shi,shiru yayi ya fara tunanin ina ya taɓa jin kalmar sallah da dai ya ji zai jawo ma kansa ciwon kai sai cewa yayi "minene sallah?"waro ido su kayi a tare suka ce "minene sallah kuma?"a yadda ya ji sun yi maganar cike da mamaki ya sa shi juyowa yace "eh mana ni ban san mi kuke zance ba"kallon-kallon suka fara yi kafin Irfan yace "ka na nufin kai ba Musulmi ne ba?"saƙe Tajdeen yayi zuwa can ya girgiza kai yace "Ni ban san komi Please telle me mi kuke son faɗa ne ?sai naji kamar na taɓa sanin wannan kalmar"cikin ɗan ilimin da su ke da

suka shiga yi ma Tajdeen bayani akan addinin Musulunci har sai da dare ya tsala sannan suka dakata tare da yi masa alƙawarin gobe sun ƙarasa mashi...

****Maradi

Rayuwar farin ciki Nazifa ke fuskanta gun mijinta inda kuma ɓangare guda ta ke fama da irin cin kashin da Maman ke yi mata,ƙiri-ƙiri Maman ke nuna banbanci tsakaninta da Sappa musamman yanzu da ita ma Sappai ke ɗauke da ciki sai ta yi ta ƙulla mata sharri iri-iri ita kuma Maman ba bincike ta hau Nazifa da faɗa tun malam Nur na tare mata har ya kai ya zuba ma sarautar Allah ido.

Yanzu abinda ya fi damun Nazifa shine wata sabuwar dokar da Maman ta kafa,in Nazifa za ta yi girki doli sai abinda Maman ta zaɓa haka kuma in za ta tafi unguwa doli sai da izininta ko da kuwa malam Nur ya yarje mata.

Duk wannan bai ishi Maman ba sai da ta ƙara mata da wata dokar na banda yawan baƙi a cewar ta suna zowa ne dan su zuga Nazifa,hatta da Rakiya ƙanwar Nazifa in ta zo Maman ta fara habaici kenan.A na haka har cikin Nazifa ya shiga watan haihuwa wanda yayi daidai da bikin malam Jabeer da Samira.

Tun satin bikin Nazifa ta fara sallar dare tana roƙon Allah ya sa Maman ta barta ta je bikin sai dai kash tana fitowa Maman tace "ina za ki Nazifa kika wani ci uban shiri ko haihuwa ce?"cikin faɗuwar gaba tace "Maman wajen bikin matar malam Jabeer kin san yau ne"baki Maman ta ja tace "eh lalle shine kike sauri zaki fice kafin na gan ki ko?"
"A'a Maman niyyata sai na shigo na shaida maki kafin na tafi"Nazifa ta faɗa muryata na rawa idonta na cikowa da ƙwalla "to ba za ki je ba,in kuma kin fita wlh akan aurenki"Maman na gama faɗa ta shige ɗaki ta bar Nazifa tsaye......

Domin shiga paid group 300 ne cakal via2670215530
ZULFAU YAHAYA
Ecobank DM +22795045822
[21/05 13:50] MRS SADAUKI: *SHAUKIN SO*💘

```LoVe story```💟

By
```

Chamsiya Laouali Rabo
{MRS SADAUKI💫✍️}

*FCWA*☀️

---

Page 19-20

Duƙewa Nazifa ta yi tana jin mararta na ƙullewa ga wani azababen ciwo da ya dirar mata lokaci guda,zaunawa ta yi dirshen ba tare da ta shirya hakan ba.Zufa ce ta karye mata,banda sunan Allah babu abinda take ambata jin ciwon sai gaba ya ke ƙugunta ma ya ɗauka.Tana nan zaune sai ga Balkis kamar an jefo ta,da sauri ta nufi Nazifa tana cewa "anty Nazifa lafiya kika yi zaune da ƙasa ai sai ki ɓata kayan jikinki"shiru Nazifa ta kasa cewa komi sai jakarta da ta miƙa ma Balkis "kira Nurrr" ta faɗa kamar ranta zai fita,wayar ta ciro daga jaka bugu biyu ya ɗauka "anty Nazifa ce ba lafiya ka tawo"shine abinda Balkis ta faɗa ba tare da ta ko amsa sallamar malam Nur ba.

Su na nan zauna Balkis sai faman jera mata sannu take sai ga malam Nur,ba tare da ya tsaya tambayar ta mi ke faruwa ba ya ja ta zuwa mota.
Gidan baya ya saka ta Balkis ita ma ta zagaya ta shiga ta ɗaya ɓangaren.
Su na zuwa asibiti aka tabbatar masu da haihuwa ce,gida malam Nur ya koma sai ga shi sun dawo shi da Maman kamin daga bisani ya kira Inna ya shaida mata.

Su na nan zaman jira sai ga yayar Inna,sama-sama suka gaisa da Maman bayan malam Nur ya gaisheta "Allah dai ya sauke ta lafiya"cewar Lami yayar Inna da "Amen "dukan su suka amsa.Sai da Nazifa ta kwashe wajen awa uku sannan Allah ya sauke ta lafiya,ta haifo kyakyawar ƴarta mace mai kama da ubanta.Cike da murna nurs ɗin ta fito ta shaida masu Nazifa ta haihu da sauri malam Nur ya tambayi abinda aka samu nurs ɗin tace "mace"a take fara'ar fuskar malam Nur ta ɗauke dan shi a tsarin shi ya fi son ya samu namiji daga farko.

Balkis kuwa har da tsalle jin sun samu baby girl,rashin jin daɗi malam Nur ya nuna ƙarara wanda har Maman ta lura da hakan.
Ganin hakan yasa ita ma ta ji sam ba ta son mace namiji take so dan burinta bai wuce a maido sunan Ali duniya ba wato marigayi mijinta.Lami kuwa ta na can inda nurs ke duba lafiyar baby,bayan sun gama bincike suka naɗota a zane suka ba ta.

Jiki sukuku Lami ta nufi su Maman dan ba ta san yadda za su ɗauki al'amarin da likitoci suka shaida mata ba,da sauri Balkis ta nufi Lami tana kallon babyn wadda kallo guda za kayi mata ka hango zallar kamarta da malam Nur.

Karɓar ta Maman ta yi tana kallon yarinyar kuma sai Allah ya jarabce ta da jin mugun sonta,kallon idon yarinya ta fara yi waɗanda su ke farare tass sai ɗan boule ɗin su wanda ya ke kamar h color dan bai da baƙi sosai.
Murya na rawa Lami tace "ikon Allah kenan!  Haka Allah ya nufa ta kasance a *makauniya* ,sai mu yi fatan Allah sa makantarta ita ce alheri gare...."da sauri malam Nur ya katse ta yace "Makauniya?kamar yaya?"kafin ya karɓi babyn daga hannun Maman ya ƙura mata ido, tabbas idonta sun nuna ko a kallo za ka gane.A razane malam Nur ya ɗago ya kalli Maman ya na cewa "Maman dagaske fah Makauniya ta haifa mini"ba Maman ba hatta likitocin da ke tsaye kusa da su sai da suka yi mamakin furucin malam Nur,ita kuwa Balkis fashewa ta yi da kuka tana girgiza ma ɗan uwan nata kai tace "sam ban tsammaci haka ba daga gare ka yaya Nur,ina imaninka ya tafi har kake faɗin haka?kar ka manta kai Malami ne ka san yadda Allah ya so ya ke yi ba wai neman shawara ba"masu raunin zuciya irin su Lami sai da suka goge ƙwalla jin bayanin ƙaramar yarinyar da ba tafi 18years ba amman babba mai hankali kuma malami ya kasa gane ƙaddarar Ubangijj zuwa ta ke ba tare da an shirya ba.

Maman ya miƙa ma babyn yana jin zuciyarsa na zafi,sam ya kasa ɗaukar lamarin ta yaya ɗiyarsa ta farin za ta kasance Makauniya?laifin mi yayi ma Ubangijinsa? Da wannan tunanin ya nufi ɗakin da ya ga an kai Nazifa ciki.A kwance ya tarar da ita hannunta sanye da ƙarin ruwa sai numfashi take saukewa akai-akai,ka na ganinta ka san ta sha wuya ba ƴar kaɗan ba.
Ido ya zuba mata yana jin zuciyarsa na bugawa yayinda ƙaunarta haɗi da SHAUKIN SOnta ke ninkuwa a ciki,ƙarasawa yayi ya tsaya kusan kanta yana kallon idonta da suke zubar da hawaye.Kamar daga bisa yaji tace "ba kayi murna ba saboda na haifi mace ko?duk lokacin da kace min  namiji kake so ina samun kaina da tsinkewar zuciya dan ban san abinda Allah za..."da sauri ya rufe mata baki ya shiga share mata hawayen tare da kwantar mata da hankali,bai bar wurin ba sai da ya tabbatar ta saki ranta.

Maman da Lami ne suka shigo,tashi ta yi ta karɓi yarinya da ta fara kuka Lami na gwada mata yadda za ta shayar da ita.Cike da kunya ta ke bata abincinta, Balkis kuwa na gefenta ta kasa ta tsare sai kallon babyn take "amsar ta ai ta ƙoshi"cewar Nazifa tana mai miƙa ma Balkis babyn,amsar ta ta yi tana dariya ta dawo ƙasa inda su Maman ke zaune bisa tabarma.

Malam Nur ne ya shigo bakinsa ɗauke da sallama, ledodin hannunsa ya ajiye ya na tambayar Nazifa jikinta,gefe ya zauna yana latsa waya sai shating ya ke hankalinsa kwance kafin kuma ya miƙe ya fita.Sosai Nazifa ta yi mamakin rashin ɗaukar baby amman sai ta bar shi akan ƙila bai iya ɗaukar jarirai ba ne.

Kwanan Nazifa ɗaya a asibiti aka sallamo ta,amman ko take Sappa ba ta zo ba.Ƴan uwa na nesa da na kusa kuwa suna ta tururuwa zuwa wajen barka,Samira dai ango Jabeer ya hana

yace sai ranar biki zai kawo ta.

Sha tara ta arziki Maman ta haɗa ma Nazifa ita da ɗiyarta,kayan jarirai kala-kala wasu ma sai ta shekara ba ta sa su ba.Wannan bajintar ba ƙaramin daɗi ta yi ma Nazifa ba dan ko ba komi hakan ya nuna ana son ɗiyarta.

Ranar suna yarinya ta ci sunan *Laila* ,malam Nur da Nazifa anko su ka yi na blue gizner. Nazifa na tsaka da cin biki sai ga Sappa kamar wadda aka yi ma doli ta shigo ɗakin,kwalin sabulu da kayan jarirai ta miƙa Samira ita ce kusa hakan yasa ta karɓa ta na godiya Nazifa kuwa cike da mamaki take kallon Sappa dan har ta mance da ita.
Juyar da kai ta yi gefe sai cika ta ke tana batsewa wanda ba komi ne ya jawo hakan ba sai kyautar gida sukutum da Maman ta bayar ga jikanyarta.

Malam Nur angon jego shi ma ya na can waje shi da abokansa suna taya shi murna,amsawa kawai ya ke dan babu yadda zai yi amman har ga Allah bai son yarinyar.
Kafin bayan sallah magrib kowa ya watse ya rage ƴan gidan,wanka Nazifa ta yi ta fito ta na shafa mai sai ga malam Nur.
Gaishe shi ta yi ya amsa kafin ya fara bincike "mi kake nema?"Nazifa ta tambaya shiru yayi bai tankata ba sai ci gaba yayi da abinda ya ke.

Cike da jin haushin share ta ɗin da yayi ta fito falo inda Lami ke yi ma baby Laila wanka sai ƙara take ta na kuka.Ka sa jurewa Nazifa ta yi tace "Inna Lami a barta haka nan tunda ba wata dauɗa gare ta ba"dariya Inna Lami ta yi tace "oh!Ni yaran yanzu babu ta ido ƙiri-ƙiri kuke nuna son ɗiya" "ba haka ba ne Inna Lami kawai na ga sai kuka ta ke ne ya kamata kuma a barta haka"cewar Nazifa ta na mai ɗauko ƙaramin towel wanda za a naɗe Laila,"ba wani son ɗiya ne mana,mu lokacin mu yaro ko wuta muka ga zai taɓa ba zamu janye shi ba saboda kunya amman ku da ya ke yaran zamani ne wankan ruwan zafi ma ba ku haƙuri ayi ma yaren ku"kai Nazifa ta sosa alamun jin kunya kafin ta ce "ruwan ne da zafi ko sirkawa bakwa yi"aza mata baby Laila ta yi kan towel ɗin da ta riƙe tun ɗazu tace "ke kike ganin zafin su amman ita daɗinsu ta ke ji saboda yanayin jikinta da ya ke da taushi balle ma yau da ta sha ɗauka jikinta yayi ciwo doli a gasa ta"Nazifa dai ba ta ce komi ba sai gashin Laila da ya kwanta luf ta ke shafawa.

Su na nan zaune malam Nur ya fito daga ƙurya ɗakin "ungo wannan ko buƙatar wani abu ta taso "malam Nur ya faɗa yana miƙa ma Nazifa kuɗi karɓa ta yi ta na kallon shi sai ya kuma cewa "eh gobe za ki koma gida shan kunu kamar yadda kuka buƙata,ban san lokacin da za ku tafi ba ƙila ina bacci sai ku shiga taxi"ya na gama faɗin haka ya fice.

Wani abu ne ya caki zuciyarta sam ta kasa yarda wannan malam Nur ɗinta ne,tunda ta haihu komi na shi ya canza.Jiki baƙwari ta miƙe ta nufi bedroom shimfiɗar da Laila ta yi ta koma can ƙarshen gado ta yi tagumi ta na tunanin rayuwa,ganin tunanin ba zai ɓarkata mata komi ba yasa ta miƙe ta ɗauro alwala ta fara jan casbi.

Washegari misalin ƙarfe goma na safiya Inna Lami ta taro mai taxi,kayan da za ta buƙata ne kawai za ta tafiya da su.Sallama su ka yi ma Maman sannan suka wuce gidan Inna,yaya Ɗalhat ne ya shigar masu da kayan ya kuma sallami mai taxi.

Cike da begen jikanyarta  Inna ta rungume ta dan rabonta da ita tun a asibiti,sosai yarinya ta ƙara yi mata kyau.
Yaya Ɗalhat ne ya matso yace "Inna kin kama ɗiya kin riƙe ba ki da niyya ba iyayenta"dariya ta yi tace "mi ake da kishiya,ɗiyar taku ma da ba wani kyau ne da ita ba sai dogon hanci kamar biro"dariya shi ma Ɗalhat yayi ya karɓe ta ya manna a ƙirji ya na jin son babyn,bisanin ya miƙa ma Rakiya wacce ke zumɓuro baki ta yi gajen haƙurin a bata.

Nazifa kuwa babu abinda ya dameta sai ɗumamen tuwon masara ta ke ciki ta na kallon diramar su.Sai yamma lisss Inna Lami ta tafi gidanta bayan ta karɓi sha tara ta arzikin da Nazifa ta yi mata.

Sosai Nazifa da ƴarta su ke samun kulawa wajen Inna da ya Ɗalhat da kuma Rakiya,dan kowa na iya ƙoƙarin shi wajen kyautata mata wannan ya sa damuwar Nazifa ta kawar duk da shi ma malam Nur ɗin na zuwa ganinta kusan kullum sai dai bai ɗaukar Laila,da ya ga Nazifa na damuwa da hakan ne ya ke shafa kanta duk in ya zo wani sa'in kuma yayi kissing nata a goshi ya ɗauki hotonta.

A kwana a tashi asarar mai rai,Nazifa ta yi arba'in har ta koma ɗakinta inda rainon Laila kwankwacakwam ya koma hannun Maman da Balkis,kullum tana part ɗin Maman sai dare kawai ake maido ta ko kuma in ta yi kuka.
Wannan abu shi yayi ma Sappa kaluluwa a zuciya ji take kamar ta jawo watan haihuwarta kusa ta haihu ko nan ta rage haushi da tunanin kuma Maman za ta so ɗanta fiye da na Nazifa.

Zaune take a falo Balkis na matsa mata ƙafafunta da suka kumbura,gefe kuma Maman ce ke ta faman koyawa Laila zama ta sakata tsakiyar ƙafafunta.
Lokaci zuwa lokaci Sappa ke kallon su 'Allah sa ta faɗi ta fashe baki da goshi 'hine abinda kawai take rayawa a zuciya.

Kamar daga sama kuwa sai jin kukan Laila ta yi ta faɗi ɗin kamar yadda ta so,da sauri maman ta cirota ta shiga ririgata amman ta ƙi yin shiru hakan yasa Maman tashi tsaye ta goyeta a baya ta shiga kewayen ɗaki.
Takaici,baƙin ciki da hassada su ne suka turnuƙe Sappa barin tausar Balkis ta yi ta nufi Maman tana yi ma Laila wasa daga goyen tsit ta ƙyale tana sauraren ɗan kacau-kacau da Balkis ke kaɗawa,tsabar baƙin ciki yasa Sappa sarƙewa da yawun bakinta ta shiga tari kamar ranta zai fita.

Harararta Maman ta yi tace "lafiyarki kuwa?minene kike ci wanda ya ƙware ki?"ƙyafƙyaf da ido Sappa ta yi ta turo baki cikin jin haushi,baki Maman ta taɓe tace "ki shiga hankalinki Sappa ba ruwana da sarkarci dan na ga har yanzu kin ƙi ki sauwa daga mugun halinki,jikanyar tawa ma banda iko na kula kawai dan ki na kishi da uwarta?"cikin jin haushi Sappa tace "toh wai ni mi na yi?ni ai ban faɗi haka ba" "to minene ya ƙware ki?in ba kin ji zafin hakan ba?ko ko kece ɗin a ban sani ba mai yin tarin baƙin ciki in kin ji haushin abu?"shiru Sappa ta yi dan sarai ta san da Maman ta yi mata farin sanin da ko uwar da ta haife ta albarka.

Ana cikin haka sai jin sallama su ka yi,malam Nur da ƴan uwansa maza bakwai sai mace datizuwa wanda ke nuni ƴaƴanta ne.Kicin-kicin Maman ta yi da fuska kamar ta ga mala'ikan mutuwa,gaisheta suka yi ta amsa da "lafiya"gabatar da su malam Nur yayi kafin daga bisani ya ƙara da cewa "wannan ce mahaifiyarsu kuma ba komi ne ya kawo su ba sai rabon gado"daram ƙirjin Maman ya buga sai ido da ta fiddo tana kallon samarin bakwai wanda su ke a jere ras gabanin ta kalli Nuradeen da Balkis ƴaƴanta biyu rak.....

My book is only 300 via
2670215530
ZULFAU YAHAYA
Ecobank DM +22795045822
[22/05 16:28] MRS SADAUKI: *SHAUKIN SO*💘

```LoVe story```💟

By
Chamsiya Laouali Rabo
{MRS SADAUKI💫✍️}

*FCWA*☀️
```

Page 21-22

Cikin dauriya Maman tace "to sai a ka yi yaya in za a yi rabon gado?"kallonta duk suka yi banda Rahinatu da ta sunne kai dan ita har ga Allah tsoron Maman ta ke.Ganin duk sun ƙyale Maman ta ci gaba da cewa "in rabon gado za a yi ai malumai ke yinsa ba wai tsakankanin magada ba,in banda masifa da zanzana irin ta tallaka duka-duka yaushe ne alhajin ya rasu da har za'a yi maganar rabon gado sai kace masu jiran mutuwar"cikin jin haushin wulaƙancin da ake yi masu Suleyman ya miƙe tsaye yace "ku tashi mu tafi tunda da alama wannan matar ba ta san arziki ba,kawai daga zuwa za ta wani rufe mu da masifa"baki buɗe Maman ke kallonsa kafin tace "ka ga masifa nan kusa da kai,uwar ka ita ce masifafa shege ɗan Zina kai miye naka cikin rabon gadon?in banda sa kai uku"duk miƙewa suka yi suka fice Rahinatu na matsar ƙwalla.
Kusa da Maman malam Nur ya matsa yace "haba Maman miye haka? ƴaƴan mijinki fah ƴaƴanki ne minene na tozarta su?"
"To Baba dake ni.Nace ka dake ni na taɓa ƙannan uwarka"cewar Maman tana juya masa baya,cike da tsoro malam ke kallonta dan abun Maman ya fara barin bashi mamaki sai dai tsoro.
"Allah ba ki haƙuri"ya faɗa ya na mai zaunawa ya fara kallon tv.

Maman kuwa ɗaki ta shige ta fara zagaye tana neman mafita dan tabbas Rahinatu sai ta fi ta samun kuɗi ita da ke da yara 6 kuma maza,yatsa ta cije tace "miyasa ma na biyewa ruɗin zuciya na yi ta shan magani dan kar na haihu mtsw..."haka dai ta yi ta saƙa da warwara har sai da kanta ya fara ciwo sannan ta kishingiɗa ta yi barci.

Washegari sai ga su Suleyman sun sake dawowa da maganar dai ta rabon gado,malam Nur shi kansa sun bashi haushi hakan yasa ya nemo malamai masu ilimi kamar yadda Shari'a ta zartar haka aka raba masu gado bayan an cika wasiya Baba an fidda ma Suleyman kaso daga ciki. Wannan rabon gadon sosai ya ɓata ran Maman ganin Rahinatu da ƴaƴanta sun ɗauki wajen kaso 85 cikin ɗari na dukiyar Alhaji ,tun tana masifa tana cewa an cuce su har ta kai ta kasa dangana ta fashe da kuka.
Sai da ta yi mai isarta sannan ta ƙyale,malam Nur da Balkis Maman suka ba duka kuɗin dan tun ba yau ba ta shaida masu kasuwanci za ta fara.

Haka rayuwa ta ci gaba da tafiya yau ƙunci gobe daɗi,Maman an fara kasuwanci sayar da kaya na Lome da kanta take zuwa dan sam ba ta da yarda.
Duk in ta tafi sai tayo ma jikokinta sayayya Laila da ƴan biyun Sappa wanda malam Nur ya

ɗauki son duniya ya ɗora masu .
"Maman wannan ai sun yi ma Amar da Anas yawa sai dai ko Laila tunda ita ta nada ƙiba"cewar Balkis wacce ke zaune tana duba kayan da Maman ta sawo,fizge kayan Sappa ta yi tace "ina Makauniya ina wannan kayan?ai na masu ido ne"da sauri Nazifa ta ɗago tana kallonta,murguɗa baki Sappa ta yi tace "eh ko ƙarya ce ba Makauniyar ba ce kike wani kallona kamar wacce ta yi maki ƙage"wasu hawaye ne suka zubo ma Nazifa a zuci take cewa 'kenan dagaske Makauniya ce?zargina ya tabbata' kallon Maman Nazifa ta yi wadda ita ma ƙwalla ta cika ma ido "ki yi haƙuri Nazifa ni nace kar a sanar da ke"cewar Maman tana kwashe kayan da aka baje a capet.
"Maman kenan ke kin san da haka?"Nazifa ta sake tambaya "eh kowa ma ya sani daga ke sai Sappa ne a baku sani ba,ita saboda irin wannan ranar yasa na hana a shaida mata ke kuma saboda kar ki tada hankalinki".
Ɗaukar Laila ta yi ta fita direct part ɗinta ta wuce,hawayen idonta ta goge sannan ta ƙura ma Laila ido wacce yanzu take wata na biyar da haihu.Da ɗan yatsar ta yi kamar za ta tsone idon Laila dan tabbatarwa amman ba ta ƙyafta ba, rungume ɗiyarta ta yi a ƙirji ta saki wani marayan kuka na tausayin kansu su biyun.
A fili ta furta "wannan dalilin ne Abbanki a bai son ki,shin kyautar Ubangijin ce yayi fatali da ita har ya ke ƙyanƙyamin ta?miye laifin ki a ciki dan kin fito Makauniya alhalin ba ke kika yi kan ki ba?shi malami bai yarda da ƙadara ba to ina ga jahili wanda bai san Allah ba?"ba ta san da shigowar shi ba sai ji ta yi ya daka mata tsawa yace "ya isa haka!ni namiji nake so shine kika tashi ki haifo min mace,macen ma Makauniya.Da wane kike so in ji rashin cikar burina koko ɗawainiya da ita?ita kanta mace rauni ce to yaya kike gani in ta kasance da naƙasa?"wasu hawayen baƙin ciki Nazifa ta goge tace "ai Nakasa ba kasawa ba ce nufi ne na Allah,kai da kuma ba ka da ita babu tabbacin haka za ka zauna har ƙarshen rayuwarka domin ba'a gama hallitar ɗan Adam ba har sai ya koma ga mahall...."wani gigitacen mari ya ɗauketa da shi tare da nuna mata yatsa yace "zo ki nakasa ni ƴar baƙin ciki, Makauniya dai ce ki riƙe abarki"ya na gama faɗa ya juya zai fita a fusace har ya kai bakin ƙofa ya ji tace "ai ba ita ta yi kanta ba"bai saurareta ba dai yayi gaba.

Cigaba ta yi da kuka tana yi ta na fyace majina,Laila kuwa sai wasa take da ƴan hannun mahaifiyarta da suke ƙara.Aje ta Nazifa ta yi ta shiga wanka,ta na fitowa ta saɓa ƴarta a baya ta goyeta.Hijab da jaka ta ɗauka ta rufe ɗaki tana shirin fita ta ji Maman na ƙwala mata kira ta window,kewayawa ta yi cikin ɗakin ta yi tsaye ta sunkuyar da kai ganin Maman na yi mata kallon mai saman ruwa.
"In dai kin san yaji ne za ki yi to ki kwance min jika dan ba da ita kika zo ba,ki barta a gidansu kafin ki tafi naku gidan.Gare ta farau makanta da har zaki ɗaga hankali in ke ma baki sonta sai ki bani na raineta,tunda ku Allah ya baku kun ce baku son kyautar wasu na can suna neman ko kuturwa ce Allah ya ba su"Maman ta faɗa da alamun faɗa-faɗa ,kukan da ta ke riƙewa ne ya kubce mata tace "Ni Maman ina son ƴata a yadda ta ke shi ne...shi ne dai a bai so "taɓe baki Maman tayi tace "to sai mi?ni ban ga abun damuwa ba tunda mu muna son abar mu,kin ga miƙo min ita tafi ki ɗora girki ki ci ki ƙoshi in kika biye ma namiji takaici ne zai kashe ki"kwance goyon Nazifa ta yi ta miƙawa Maman ,baiwar Allah Laila sai barcinta take.

Ɗaki Nazifa ta koma tana jin zuciyarta ta rage nauyi, zantukan Maman ne kawai ta yi zaune ta na tunawa ta na ɗan jin sauƙi.Tun daga wannan lokaci Nazifa da ƴarta ke fuskantar tsangwama gun malam Nur da Sappa yayinda Maman ta ke ƙarƙafa ma Nazifa gwiwa,tun lamarin na damunta har abun ya zame mata sabo.

Cikin shirin fita ta fito tana jaye da hannun Laila wacce yanzu ta ɗan girma tana cikin shekara ta biyar.Da shigar su part ɗin Maman Amar da Anas suka shiga yi ma Laila dariya su na tsokanar ta"ƴar makauniya..."cikin jin haushi Laila ta ƙwace hannunta daga na Nazifa ta nufi inda ta ke jin maganar su tana lalube,dariya suka sake yi tare da ci gaba da tsokanar ta suna guje-guje ita kuma tana bin duk inda taji motsin su.
"Miyasa ba ki jin magana ne Laila ba na ce ki bar kula su ba?"cewar Nazifa ta na kamo hannunta,hawaye na kawowa idonta tace "Ammy baki ji su ke tsokana ta ba?"kai Nazifa ta girgiza tace "to ai ƙannanki ne sai ki yi haƙuri,tawo mu tafi Maman na bedroom"tsuki Sappa ta yi wacce tun ɗazu ta ke zaune ƙasa da uban cikin ta ƙatoto haihuwa ko yau ko gobe tace "Allah kiyaye mu irin mu babu masakai,can ku ƙarata ke da makauniyar ki,Twins ku zo nan kar ku taɓa wacen abar ta liƙa maku nakasa"murmushin da yayi kuka ciwo Nazifa ta yi kafn ta wuce ɗakin Maman,ba'a jima ba sai ga su sun fito Maman na yi mata a dawo lafiya.A zaune ta tsinkayi malam Nur ya ɗora Twins a cinya ya na raba masu biscuit,har za su wuce Laila taji murya shi da sauri ta waiga tana ƙyafƙyaf da ido kamar mai gani tace "Abih..."ɗagowa malam Nur yayi kallo guda yayi masu ya maida hankalin shi gun Twins da suke mashi surutu ya na amsa masu.

Zuciya na yi mata zafi ta nufi bakin hanya ta samu abun hawa ya kaita gidan Samira wacce ake bikin haihuwar da ta yi ta biyu,abun biki kawai ta bada ta samu wuri ta rakuɓe.Shikenan yanzu ita da farin ciki sai dai ta gani gun wasu?haka dama maza su ke ba su da tabbas?miye laifin ta dan ta haifi makauniya? wannan ne tambayoyin da Nazifa ta yi ta yi har bikin ya watse ta dawo gida.

Cikin dare Sappa ta kasa bacci saboda naƙudar da ta tawo mata gadan-gadan,cikin tashin hankali malam Nur ya fito ya shiga ƙwanƙwasa ma Maman ƙofa kasancewar ba ta da nauyin bacci yasa ta ji bugun.
Ta na buɗewa ya shaida mata Sappa ce ke naƙuda da sauri ta koma ɗaki ta kimtsa suka nufi asibiti,Twins kuma aka bar su wajen Balkis.

Gari na wayewa Nazifa ta je gaishe da Maman Balkis ke faɗa mata Sappa na asibiti wajen haihuwa "Allah sauke ta lafiya"ta faɗa tare da komawa ciki ta fara girkin da za'a ta kai.
Ta na gama girki su ka shirya ita da Balkis da yara suka nufi asibiti,tun daga nesa su ke jin kukan Sappa sun tsaya tunanin room ɗin da take sai ga malam Nur ya fito fuskar shi a kumbure

idon shi sun yi ja alamun kuka ya yi.Ba su tsaya tambayar shi mi ke faruwa ba suka shiga ɗakin da ya fito,kwance suka tarar da Sappa sai fizge-fizge ta ke yayinda likitoci ke ƙoƙarin yi mata allura barci.

"Maman lafiya ko jaririn ne ya zo ba rai?"cewar Balkis,kai Maman ta girgiza ta yi masu nuni da ɗan ƙaramin gadon da aka shimfiɗe bbyn tace "a'a da ranta kawai dai da nakasa ne aka haife ta da shi"da sauri Balkis ta zaro ido tana ƙarasawa bakin gadon,wata kyakyawar baby girl ta yi tozali da ita mai hannu guda ɗayan kuma gundululu ne.
Tausayinta ne ya ratsa zuciyar imani ta Balkis hannu na rawa ta ɗauke ta,ɗaya daga cikin nurs ɗin tace wane suna za'a sa ga takardar babyn " *Jasmine* "Balkis ta faɗa a takaice tana miƙawa Nazifa babyn.A nan free page ya ida mai son ci gaba sai ya biya 300 via 2670215530 ZULFAU YAHAYA
Ecobank DM +22795045822

*Dama haka Allah ke ikonsa,in ka raina halittar wani kai ma sai ya jarabce ka ya ga ya za ka yi.Ga Sappa dai ita ma ta haifi mai nakasa ko ya za ta kaya? Shin za ta yarda ita ta haifi Babyn nan ko kuwa ? Mu haɗe a paid group*
[22/05 23:57] MRS SADAUKI: *SHAUKIN SO*💘

```LoVe story```💟

By
Chamsiya Laouali Rabo
{MRS SADAUKI💫✍️}

*FCWA*☀️

---

23-24

"Zan ci mutumcin ki wlh in ba ki karɓi yarinyar nan ba kika bata abincinta,uwar mi za kiyi da shi in ba ki shayar da ita ba?"Mamar Sappa ke faɗin haka tana mai miƙa mata babyn.Kai ta girgiza cikin kuka tace "wlh Umma tsoronta nake ji,ban iya ganin ta"
"To kin dai ji da kunnenki tun ɗazu yarinyar nan ke kuka ta bata nono ta ƙiya sai zam-zam kawai nake ɗura mata"cewar Maman ta na hararen Sappa wadda ta yi zaune kan gadon asibiti tana
```

rusar kuka.
Bisa cinyoyinta Umma ta aza mata Jasmine da ke ta kuka,rumtse ido Sappa ta yi ganin hannu guda kawai ya fito ta rigar gudan kuma sai shatin shi kawai ake gani.Karrr ƙafafunta suka fara zanzana suna rawa yayinda hawayen fuskarta suka ƙaru,wani wawan dundu Umma ta kai mata a baya tace "in dai baki shayar da ita ba Allah ya isa nonona da kika sha ban yafe ba"jin furucin mahaifiyarta  yasa doli ta fara baiwa Jasmine abincinta.
Ƙofa aka ture tare da yin sallama,Nazifa ce hannunta ɗauke da basket ɗin abinci.Gaishe da su Maman ta yi tare da tambayar Sappa ya jikinta amman ko kanzil ba ta ce mata ba,Maman tace "ina kika baro ita Laila ɗin?"  "Ta na can gida wajen Balkis tana koya mata karatu" "ah to yayi ai gwara ita Balkis ɗin ta koya mata tunda shi uban ya kasa kaita makaranta" murmushi kawai Nazifa ta yi tana kallon baby Jasmine da ke shan nono har yanzu kafin zuwa can ta saki alamun ta ƙoshi hakan yasa Sappa maida rigarta tana turo baki.Tashi Nazifa ta yi ta ɗauko ta murmushi kan fuskarta,gefen ƙyale ta sa ta goge mata baki.

Hararenta Sappa ta yi tace "munafuka wa ya sani ma ke kika yi min asiri na haifi wannan masak..."da sauri Umma ta buge mata baki tace "in na sake jin kin aibata yarinyar nan sai na yi mugun saɓa maki, banza daƙiƙiya da ba ta san abinda ta ke ba"mahaifiyar Sappai ke faɗin haka,ita dai Nazifa har ga Allah ta ke jin son Jasmine.
Abinci Maman ta zuba plate biyu ta miƙa ma Sappa guda su suka ci ɗayan,ba jimawa likita ya shigo ya basu takarda sallama.
Kaya suka fidda kafin Nazifa ta fita bakin ƙofa ta kirawo ɗan taxi,shi ya taimaka masu wajen sa kayan tare da faɗa masu kuɗin da za su biya.
Har ƙofar gida aka sauke su,da gudu Twins suka tawo gun Sappa tare da kama mata ƙafafu.Hannun su ta ja zuwa ciki,direct part ɗinta ta wuce alhalin part ɗin Maman aka ce za ta tsaya.

Cikin jimami Maman tace "ya kamata fa mu samu mafita kar jaririyar nan ta mutu,a bada kuɗi  a sayo madarar gwangwani a riƙa bata kina ga fah tun zuwan mu ta kama ƙofa ta rufe alamun ta bar mana  da ƴar"cikin takaici Umma ta kalli Maman tace "yanzu sabida Allah anty jaririya uwarta da ranta da lafiyarta sai a shiga bata madara?"Maman ta yi saurin cewa "eh mana in dai ba taimaka mata za muyi wajen kisan kai ba,wlh na fi ki sanin halin Sappa ke haihuwarta kawai kika yi tunda kika ji tace ba za ta shayar ɗin ba to haka maganar take ba canji.Balkis tashi ki tafi pharmaci ki sawo min madara "Maman ta faɗa ta na zuge zip ɗin bag ɗinta ta baiwa Balkis 5000.
Ruwan zafi Umma ta ɗora yayinda Maman tayi ma Jasmine wanka,ba jimawa sai ga Balkis ta dawo riƙe da ledar madara da biberon.

"Yauwa wanke biberon ɗin sai ki kaɗa na bata,baiwar Allah yunwa ta ke ji"cewar Maman, "toh"Balkis ta amsa ta nufi kitchen ba jimawa ta dawo da kaɗaɗar madara ta miƙawa Maman.Ana saka mata tétine ɗin ta kama ta shiga sha zut-zut,baiwar Allah sai da ta sha sosai sannan ta saki dandanan barci ya ɗauke ta.

A ɓangaren Sappa kuwa babu wanda ta gaya ma ta haihu,dan a cewar ta abun kunya ne a ce ta haifi nakasasa mai hannu guda.
Ita ke dafa ma kanta ruwan zafi tayi kuma wanka da kanta,tun da aka sako su daga asibiti ba ta ƙara sa su Maman a ido ba balle wata can Jasmine.Duk abinda ta ke buƙata malam Nur ta ke gayawa ya kawo mata,dan sam shi ma bai marhaba da haihu Jasmine duk da malam Jabeer na bakin ƙoƙarin shi wajen tunatar da shi amman fafur ya ƙi fahimta,a ƙarshe ma dai malam Jabeer ne yayi ma Jasmine huɗuba.

Sati na kewayowa aka yanka ma Jasmine ragon sunanta ba tare da yin biki ba, Sappa da malam Nur ko a kwalar rigarsu dan ba su san wainar da ake toyawa ma ba.
Da dare ya shiga part ɗin Nazifa sai ganinta yayi rungume da Jasmine tana bata madara gefenta kuma Laila ce zaune ta na cin abinci tana karatun da Balkis ta kowa mata.
Baki ya taɓe a zuci yace 'uwar masakai tunda ke kin ji kina iyawa ai sai kiyi'ƙarasowa yayi ya zauna ta ɗago ta kalle shi ba tare da tace komi ba.
Laila kuwa ido ta shiga juyawa tana ɗan buɗe ƙofofin hancinta tace "Abih...?Ammy Abih ya shigo nan?naji ƙamshinsa"ido malam Nur ya waro cikin suɓutar baki yace "toh mayya"Nazifa tace "Allah kiyaye ni ban haifi mayya ba"Laila kuwa tashi ta yi tana lalube tana cewa Abih,"kar ki taɓa ni"ya faɗa da sauri ganin ta zo dab da shi cikin rashin sa'a ta ɗora hannunta bisa farar shaddar shi,cike da murna ta ke furta "Abihhh"wata ɗunguza yayi mata yana mai tashi tsaye ya tattare gun da ya ɓace ya nufi toilet ya na banbamin bala'i.

Kuka Laila ta fashe da shi ta na kiran sunan mahaifiyarta,wani mashi ne ya caki zuciya Nazifa lokacin da ta ɗago Laila ta ga goshinta yayi ƙululu sakamakon bugewa da tayi da ƙafar kujera.
Tun daga wannan ranar Nazifa ke kafa-kafa da Laila da zarar ta ji muryar malam Nur ta na son zuwa sai ta riƙe ƴarta,shi kam ba ƙaramin daɗi ya ke mashi ba dan a ganin kiran sunan shi ma da Laila ke yi takura ce.Gefe guda kuma sosai ya ke tattalin Twins da saya masu duk abinda su ke so,a duk lokacin da babu school kuwa da su ya ke tafiya makaranta.

Karamci da Nazifa ta yi na ɗaukar Jasmine yasa ta ciri tuta a zuciyar Maman da umma,wanda kuma hakan ya fara damun Sappa sai ta fara kula ƴar makauniya ta na janta a jiki wani sa'in har part ɗinta ta ke kwana.A tunanin Maman Sappa tayi hankali ne yasa take son maida alkairi da alkairi ga Nazifa ba su san cewa aiki ne ta ke sa Laila ba ,ba tare da tayi la'akari da ƙaramtar ta ba.

Lokacin da Laila ta shiga 10years zallar kyawunta da kamalarta suka fito wanda ba komi ya ƙawata ta ba sai tarin ilimin da ta ke samu gun mahaifiyarta da kuma amarya Balkis.Cike da jin daɗi da annushuwa Maman ke kallonta tace "yanzu dagaske Lailana kin hardace alƙur'ani hizib

sittin?"kai Laila ta ɗaga tana murmushin da ke fito da zallar kyawunta "gaya min duk abinda kike so ni kuma nayi alƙawarin zan yi maki shi"cewar Maman,shiru Laila tayi zuwa can tace "ina so nima idona ya buɗe na rinƙa gani kamar kowa kin ga shikenan Twins ba za su sake tsokanata ba"kamar daga sama amsar ta zowa Maman,wasu hawaye ne suka zubowa Maman cikin dauriya tace "in shaa Allah zan yiwa Abihn ki magana ya shirya mana visa mu tafi ƙasar waje ayi maki gyaran ido"rungume ta Laila tayi cikin farin ciki.

Cikin satin da bai wuce biyu ba Maman suka fara shirye-shiryen fita ƙasar waje bayan ta sa malam Nur ya je Bank ya ciri duka kuɗin account ɗin da suka yi saura dan tun auren Balkis aka bata gadonta cikin su aka yi mata sayayya sauran ta baiwa mijinta kasancewar shi tallaka ne.

Cike da mamaki malam Nur ke kallon Maman yace "yanzu Maman saboda kawai a buɗe ma Laila ido zaki sa na kwashi kuɗin account duka?"zaro ido Sappa ta yi jin wani za'a yi ma Laila magani a take wani kishi da baƙin ciki ya turnuƙeta ta shiga tari.
"Eh tabbas kuma babu wanda isa ya hana dan haka ka fara shiri dan tare za mu tafi"wasu hawayen farin ciki ne suka shiga ambaliya a fuskar Nazifa ita sam ba ta zaci gaskiya Laila ke faɗa mata ba lokacin da ta shaida mata Maman tayi mata alƙawarin kaita asibitin waje.
Jasmine ce ta shiga tsale tana cewa "waiiii antyna za ta buɗe ido nima Maman sai a sayo min hannu"dariya Maman tayi tana mai jawo ta zuwa jikinta.

Tsananin baƙin ciki da hassada ya haifar ma da Sappa ciwon mara,a ƙarshe dai cikin jikinta ya fara zuba.
Tun da safe ta tafi asibiti,su na nan zaune jiran Dr ɗin abun ka da taron mata nan fa suka shiga hira kowa na faɗin abinda ke damun shi har aka zo kan Sappa wacce ke basu labarin za'a kashe maƙudan kuɗi saboda gyaran idon ɗiyar kishiyarta,ai kam suka shiga zuga ta kar ta yarda.Baki ta ja tayi ƙyaci tace "ina fah zan yarda ina nan ina tunanin matakin da zan ɗauka,ki na ga fah tashin hankalin da nake ciki ne ya haifar min da zubar jini"wata ɗaya daga cikin wadda tafi nuna damuwa akan abun tace "nima ciki ya taɓa min zuba amman ina shan wani maganin gargajiya ya ɗauke har sai da na haife ɗan cikina"Sappa tace "a ina kika same shi ni inda ki na da shi da kin bani dan dama ba kasau nake son namiji ya duba ni ba"
"No babu matsala in ki na so sai ki tashi mu tafi na kai ki har gun da ake saidawa" "ok tashi mu tafi"cewar Sappa.
Adaidaita suka samu suka nufi bakin asibiti ƙarama,wani ganye matar ta saye ta baiwa Sappa lokacin da suka ƙara tarar adaidaita da za ta mayar da su."Ka fara sauketa sai na ga gidanki,in ya so daga baya sai na kawo maki ziyara" "babu damuwa Maman Latif"cewar Sappa.
Hira suka tayi har aka kawo Sappa ƙofar gida ta biya duka kuɗin harda na Maman Latif,"nagode sosai Allah bar zumunci ki ban number dan in naje gida na kira naji maganin in ya so jikin ki" Sappa tace "ba damuwa"ta zaro number ta da ke jikin wata ƴar takarda ta baiwa Maman Latif.

Da zuwanta ta tafasa ganyen maganin ta tace ta fara sha,tun Sappa na jiran cikin ya bar zuba

har ta fidda rai.
Shirin barci ta yi ta tana tunanin ƙila maganin bai so jininta ba ne.
Sappa ba ta jima da kwanciya ba ta ji kamar ana dirowa cikin gidan,ji kake dif-dif-dif ƙatti na dirowa.Ta window ta leƙa nan ta ga zabga-zabga mazaje fiye da goma ko wane fuskar shi rufe da masque,ga manyan bindigogi a hannunsu.Da sauri Sappa ta saki labulen tana jin fitsari da ragowa cikin sun fara zuba.

Part ɗin Maman suka nufa,ba su wani ɗauki lokaci ba suka ɓalle ƙofar.Duka suka shigo aka bar biyu a bakin ƙofa,kamar a mafarki Maman ta ga mutane da baƙaken kaya sun yi ma gadonta ƙawanya.Wani gigitacen ihu ta ƙurma wanda ya sauka har cikin kunnen malam Nur da ke tsaye kan sallaya yana sallah.Kirjin shi ne ya buga da sauri-sauri ya sallamce ya nufi ƙofa.
"Ina kuɗin da kika ciro daga Bank?kar kiyi garma dan zan iya harbe ki"ɗaya daga ciki ya faɗa yana bugawa Maman kan bindiga ga hanci a take jini ya ɓarƙe,ta dafe wurin tana kuka wani ya kai mata naushi da ƙafa yace "ba tambayar ki ba a ke?"azabar da Maman taji ne yasa ta nuna masu drower,ba ɓata lokaci wani ya buɗe sai ga ƙatuwar bag.Zip ɗin ya buɗe ya ga ƴan goma-goma rasss kwance ciki da hannu yayi masu alama suka fice daga gidan.......

My book is only 500 via 2670215530
ZULFAU YAHAYA
Ecobank DM +22795045822 .DAGA WANNAN PAGE ƊIN BABU WATA DA ZA TA SAKE FITA DUK MAI SO YA BIYA.

Please share
[23/05 09:38] MRS SADAUKI: *SHAUKIN SO*💘

```LoVe story```💟

By
Chamsiya Laouali Rabo
{MRS SADAUKI💫✍️}

*FCWA*☀️

---

Littafin SHAUKIN SO labari ne akan kishiyoyi biyu ,ta farko sun yi auren soyayya da mijinta yana mugun sonta kamar zai mutu sai dai kash a haihuwar farko ta haifa masa Ƴa makauniya,wanda hakan yasa alaƙarsu yin rauni.Yayin da ta biyun kuma aka yi musu auren
```

zumunci bai sonta amma sai ta haifa masa ƴan biyu kuma duka maza wannan yasa ta ciri tuta a wurin mijin.

Shi me zai faru a gaba? Ku biyo ni a paid group only 300 via 2670215530
ZULFAU YAHAYA
 Ecobank DM +22789042227 ga waɗanda suke da lambata ta farko suna iya tura receip ɗinsu ta can ba dole sai wannan da na bayar ba.
[23/05 11:29] MRS SADAUKI: *BAƘIN RUHI*🧌🐲

```LoVe aNd HoRrOr story```👽

By
Chamsiya Laouali Rabo
 {MRS SADAUKI💫✍️}

*SADAUKARWA :* Ga dukkan iyayenmu MATA da suka tsaya tsayin daka don bamu kariya a kan dukkan wani da ke son cutar da mu.

*FCWA*☀️

___________________________

Happy sallah my dear fans, Allah karɓi ibadunmu Amen !!!

*Wannan labari da da kaso saba'in ya faru da gaske,don haka don Allah kar wacce ta ji haushina yayin ganin abin da ya saɓawa ra'ayi*

01

“Kowanne ahali da nasa sirrin,haka kowanne ahali da nasu tabo ko ƙaddara ko kuma dai wani al'amari wanda suke ɓoye wa.Motar tsautsayi ce ta ja ni na bankaɗe mayafin da ya luluɓe baƙin sirrin gidanmu wanda silar haka yasa na baro ahalina domin tseratar da da gajiyayen ruhina,wanda aka raunata shi ta sigogi da dama” na yi shuru saboda hawayen da suka cika min ido.Ita kuwa Lubna banda aukin kallona babu abin da take yi,da dukkan alamu ta ƙagu ta ji ainahin labarin nawa.

Na ɗan yi murmushi mai ciwo wanda ya bai wa ƙwallar da ta taru a idona sa'ar zubowa kan
```

kumatuna,na ci gaba da cewa " Gidanmu irin family house ne wanda za ki kaf yayyu da ƙannai a ciki,mu biyar ne mahaifiyarmu ta haifa,mu biyu ne mata ukun maza.Anty Aliya ce babba,sai Aliyu,sannan Fahad,sai ni sannan autanmu Haidar.Sannan akwai ƴaƴan kawunana su ma duk da matansu da ƴaƴansu,duk yawanmu a tukunya guda ake yi mana girki haka muka taso muka ga iyayenmu na yi.Sannan in za a ci abinci ma su iyayenmu maza a tare suke ci haka ma matan,mu kuma ana banbanta wa ƴan sa'inni ɗaya ake zuba mana a cikin faranti guda da wannan ne na yi sabo da cousin/cousine ɗita Hassana wacce ƴan biyu ne su ɗaya ta rasu a wani dare bayan mun gama cin abinci.Ni da Hassana akwai wani abu da ke faruwa cikin ahalinmu da yake mugun ɗaure mana kai yake kuma ci mamu tuwo a ƙwarya.Ba zan manta wata rana mun je ɗebo ruwa a ƙatuwar rijiyar da ke can bayan ɗakunanmu Hassana ta dube ni da kyau ta ce "Haule har yanzu mutuwar Husseina ta ƙi fita raina , kowane dare sai na yi mafarkinta tana kuka tana ce min na cece ta,amma jiya sai take ban shawara wai na gudu na bar gida ban san dalili ba"

"Kawai don kin san abin a rai ne shi yasa, sannan duba da cewa ku ƴan biyu ne ƙila shi yasa kika kasa fidda abin a kanki amma kusan shekara fa yanzu da ta rasu" shi ne abin da na faɗa mata a wancan lokacin amma sai ta girgiza kai ta ce "a'a na fi tunanin dai wani abun ne yasa take zuwar min a mafarki, sannan kar ki manta ko sau ɗaya ba ta take rana sai ta kawo min ziyara tana maimaita abu guda na cece ta,amma na jiya ya banbanta kawai ta ce na gudu" ban kai ga ce mata komai ba goggo Lami wacce ta kasance mahaifiyar Hassana ta iso bakin rijiyar,sam ba mu yi tunanin ta ji abin da muke cewa ba don ba ta nuna alamu ba kawai dai ta ɗauki bokitin da muka cika da ruwa ta tafi.To mu ma sai muka watsar da zancen muka ci gaba da aikinmu,bayan mun gama sai muka koma can cikin gida.

Wani irin kallo na ga Innarmu na bi na da shi,tun ban damu ba har na soma tsarguwa sai kawai na bar inda take don kaucewa kallon.Da dare bayan duk mun yi sallar isha'i muka fito cin abinci,tamkar wasu ƴan biki haka duk muka yi kashi-kashi muka kewaya kowa da faratinsu muna ci muna santin girkin iyayen namu har muka gama sai aka soma yin gatana har sai da dare ya tsala sannan duk muka rabu.

Ina shiga ɗakinmu har na kwanta na ji muryar Innarmu ta kira sunana cikin wani sauti "Haule?" sai da gabana ya faɗi amma na daure na ce "na'am Innarmu"

"Zo nan" ta faɗa ,sai na tashi na je kusa da gadon ƙarfenta mai rumfa na yi tsaye tare da sunne kai saboda har zuwa yanzu irin kallon nan ne na ga tana yi min.
"Kar na sake jin kin yi zancen nan ke da Hassana ,kin ji ko ba ki ji ba?"

"Wane zance Innarmu?" na tambaye ta don ni har ga Allah na manta.
"Na mutuwar Husseina,ki je ki kwanta" shi ne abin da ta ce,na je na kwanta ɗin sai dai fa sam ba baccin na yi ba kamar yadda na so yi tun farko.

Ido kawai na lumshe,ina jin lokacin da anty Aliya ta zo ta kwanta gefena bayan kuma Innarmu ta ce ta kashe ƙwan lantarki.Duhu na game ɗakin na buɗe idona,tunanin na shiga yi iri-iri yadda ake yawan yin mutuwa gidanmu kusan kuma duk date iri ɗaya ne.Na jima sosai cikin wannan tunanin,don gari yayi tsit kafin kuma na soma jin motsi a can babban falon ahali.Kamar munafuka haka na miƙe na fita,amma ban fita zuwa ƙaramin falo sai na laɓe,iyayenmu maza na gani kaf illahirinsu suna magana akan zancen da ban san ina ya dosa ba.

"Ibrahim yanzu ta ɓangarenka ya kamata mu fitar da alƙawari" Kawu Hamza ya faɗa wanda shi ne babba kaf cikinsu.

Kawu Laminu ya karɓe da cewa "hakan shi ne daidai,kuma dai kyautar namiji don ni ai mace na bayar wancan lokacin " wato mahaifin Hassana .

Ibrahim wanda ya kasance mahaifina yanayin fuskarsa ce ta ɗan canza kafin ya ce "zan yi shawara" sai kuma suka miƙe suka shiga wani ɗaki ƙwaya ɗaya tal wanda tun da na yi wayo ban taɓa ganin an buɗe shi ba sai yanzu.

Ba tare da na san mene ne meeting ɗin nasu ya ƙumsa ba sai na koma kan shimfiɗata na kwanta.Ina shirin rufe ido haske ya game ɗakin nan muka haɗa ido da Innarmu,"daga ina kike?" ta jefo min tambayar da kafin na bata amsa Haidar ya fashe da wani masifafen kuka wanda yasa Innarmu nufarsa da sauri.

Haidar ƙaramin yaro ne duka ba a yi wata biyu da yaye shi ba,ruwa Innarmu ta basa amma yadda take ɗura masa su to kamar haka ya maido su ta baki da hanci kafin kuma daga ƙarshe jini ya zubo masa ta hanci shi kenan bai ƙara motsi ba" ina kawowa nan na miƙe na bar Lubna zaune sake da baki da hanci.

"Haule ina kuma za ki je?" ta tambaye ni,ba tare da na juyo ba na ce "zan wanke kwanuka kafin Hajiya ta dawo".

Wurin da aka tanada don yin wanke-wanke na nufa na soma wanke plate ɗin da customa suka ci abinci.Ina tsaka da yi Lubna ta zo tana yi min ɗauraya,mun yi kamar minti biyar muna aikin kafin ta ce "fatan dai ba mutuwa Haidar ɗin yayi ba?"

Na san halin Lubna da mugun son jin labari,in ba ta gamsu ba to ƙila har gida tana iya bina don ta ji ƙarashe hakan yasa na ɗora daga inda na tsaya.

"Ina tsaye a gaban idona Innarmu ta soma yin hawaye tare da furici guda "don me sai Haidar?"

wannan kalmar ta daɗe tana yi min yawo cikin kwanya don nemo ma'anarta amma tsawon lokaci ban samu ba.Na durƙushe kan gwiwaina tare da tambayarta “Innarmu me ya samu Haidar ɗin?”

“Ya mutu Haule! Haidar ya mutu!” ta bani amsa tana ƙanƙame gawar Haidar,ban san lokacin da na yi kururuwa ba wacce kusan ita ta tashi kowa na gidan ciki kuwa har da anty Aliya.

Kan ki ce wani abu ɗakinmu ya cika da mutane,ana ta kuka goggo Lami ce ta je ta rungume Innarmu tana bata haƙuri.Yayin da Hassana ta yi tsaye kusa da ni ta ce “duba ki ga irin yadda Husseina ta yi ne yayin mutuwarta” cak hawayen da suke yi min zuba suka ɗauke,yayin da idona ya soma tariyo min gawar Husseina wacce har bayan an yi mata wanka jinin da ya fita ta hancinta yana nan bai goge na sai ma ƙari da aka samu wanda kafin safe har da idonta suke shatatar da kukan jini.Ban iya cewa Hassana komai ba a wannan lokacin sai dai mun ci gaba da kukan mutuwar Haidar,wanda har asubah babu uba namiji ko ɗaya da ya leƙo ɗakinmu sai da gari yayi haske shi ma ɗin karɓar gawar suka zo.

Bayan an yi wa Haidar wanka aka bai wa Innarmu damar yi masa ganin ƙarshe,haka don ƙwaƙuwa na mara mata baya har sai da ta buɗe likafanin nan na yi arba da idonsa su ma suna shatatar da jini.Kuka ne ya kubcewa Innarmu,kawai aka rufe gawar tare da fita shi nan gidan namu ya ƙara kancamewa da koke-koke ganin an fita da shi.

Ana cikin zaman makoki ne Hassana ta zo ta ja ni gefe,na ce “ke lafiya?”
Sai da ta waiwaiga sannan ta ce “jiya bayan mun kwanta na yi mafarkin Husseina ta ce na baki kayanta waɗannan wanda ta mutu da su ki saka a jikinki”

“Saboda me?” na tambaye ta ,ta ce “ke dai don Allah ki saka” nan na yi da ita zan saka ɗin kamar yadda ta buƙata” sai kuma na sake yin shuru na kalli Lubna wacce ta tsaya cak da yin aikin,na sakar mata murmushi na ce “ya dai kin tsorata ne? Ai ba ki ji komai ba nan duk shimfiɗa ce ke dai ki yi haƙuri da sannu duk za ki ji dukkan labarina”

Lubna ta ce “ai duk jikina yayi sanyi duk da dai ni ma da nawa labarin mai matuƙar firgici ”

Masifar Hajiya ce ta katse hirar tamu,da sauri na fita ina bata haƙuri ita kuwa kamar ƙara zuga ta nake sai ƙaimi take ƙarawa wurin faɗan.

“In ba ku canza ba wallahi sai duk na kore ku na kawo sabbin ma'aikata,dubi yadda har yanzu ba ku goge table ba”.

“Yi haƙuri Hajiya amma don Allah kar ki kore ni ba ni da kowa” na faɗa murya na ɗan rawa ,amma da yake Hajiya ƙarshe ce wurin rashin mutumci sai ta tsiro da wani zancen “yau ba za ki ci abincina ba sai da ki saya da kuɗinki,saboda kin ga ina tausayinki ne kike yi min iya shege” tana gama faɗar haka ta yi ƙuuu ta fice,ni kuma na yi baya na zauna kan kujera saboda kaina

da ke mugun sara min.....
[23/05 11:29] MRS SADAUKI: *BAƘIN RUHI*🧌🐲

```LoVe aNd HoRrOr story```👽

By
Chamsiya Laouali Rabo
{MRS SADAUKI💫✍️}

*SADAUKARWA :* Ga dukkan iyayenmu MATA da suka tsaya tsayin daka don bamu kariya a kan dukkan wani da ke son cutar da mu.

*FCWA*☀️

---

02

In akwai abin da ya fi ɗaga min hankali shine zancen kora ta da Hajiya ta ce tana iya yi,wanda kuma ya ɓata min rai shi ne yadda a kullum take wulaƙanta ni kawai don ina ƙarƙashinta.

Lubna ta fito wacce ita tun tuni ta gama aikinta,dama ita iya girki ne take yi.Ni kuma tarben baƙi da kawo musu abin da suka buƙata,sai kuma wanke kwanuka da share restaurant ɗin.

"Ki je ki yi wanke-wanken ni sai na goge wurin" ta faɗa cikin sanyin murya,ban ce mata komai ba na miƙe dakyar na je na ida aikin nawa.Sannan na dawo nan muka ƙarasa gugar,bayan mun gama na rufe ko ina kafin mu kama hanyar gidan Hajiya .Da ɗan nisa wannan yasa sai da muka yi sauri kafin mu isa,a falo muka tarar da ita ta ƙure ƙarshen ac amma duk da haka sai gumi take fitarwa.
Kallo ɗaya na yi mata na ɗauke kai,saɓanin Lubna da ta je tana cewa "hajiya ko jikin ne ya motsa?"

Cikin murya wacce kana ji ka san babu lafiya ta ce "olser ce ta yi min wuf sai ɗan kanoma,ki bani maganin nan na sha wanda kike bani"

Lubna ta ɗan dube ni kafin ta ce "ai Haule ce ke da shi dama ba ni ba"
```

“To ki karɓo min”
Ina jin haka na yi saurin wucewa can ɗakinmu da aka ware na ƴan aiki.Ina tsaka da rage kayan jikina Lubna ta shigo hannunta riƙe da kofi ta ce “ki zuba na kai mata”

Cikin ƙunar rai na ce “na ƙi na zuba ina ce dai yawuna ne”

Lubna ta tuntsire da dariya tare ɗan matsowa kusa da ni ta ce “ke ba abin alfaharinki ba ne a ce kamar Hajiya tana shan yawun ƴar aiki ? Kin san da ace ta san mene ne ainahin maganin da ba za ta sha ba Alkur'an yadda ta tsani talaka”

Wani ɗan murmushi na yi kafin na tofa yawuna cikin kofin ruwan,nan take suka soma tafasa suna motsi tare da canza kala.
Lubna ta ɗaga gira ta ce “ai ke ce Hajiyar,sannan don Allah ki yi haƙuri ki bar saka mana hajiyarmu cikin wancan halin kar ta je ta mutu mu shiga tara”

“Tafi dai ki kai mata kika tsaya surutu” na faɗa tare da shiga toilet na yi wanka,ko da na fito sai na tarar da Lubna ta kawo mana abinci.Nan ɗin ma wani murmushi na yi kafin na ce “cewa ta yi fa ba za ta ban abincinta ba”

“Tun da dai ta zuba miki sai ki yi haƙuri ki zo mu ci” cewar Lubna.

Sai da na canza kaya sannan na zauna muka ci shinkafa da miya muka hauda ruwa masu sanyi.Sai kuma muka hau yin hira kafin kuma ta miƙe ta ce “bari na je na gyara kayan miya na gobe,ki shirya don da na dawo za ki ɗora min labarinki” na yi murmushi kawai ba tare da na ce komai ba.

Ina shirin kwanciya Lubna ta shigo kamar an jefo ta,na ce “ke lafiya?”

Ta ce “uban ƴan tsamin rai ne ga shi can a falo tare da Hajiya yana juya kofin da na bata ruwa wai yana son ganin wane irin magani ne wannan da ta sha ta samu lafiya lokaci guda”

Na ce “to mene ne na ga duk kin tayar da hankali?”

Ta waro ido ta ce “hajiya ce ta basa amsa wai ke ce kike da maganin,kuma walla...”sauran maganar ce ta maƙale mata ganin an banko ƙofa da mugun ƙarfi har ni ma sai da na zabura yayin da haɗuwar idonmu ya saukar min da matsanancin faɗuwar gaba amma na aro mayafin jarumta na gaishe shi cike da ladabi kamar yadda uwarsa ta ce mu dinga yi.

“Ina wuni Alhaji ?” na furta cikin sanyin murya ina mai sauke idona ƙasa.

“Bani maganin da kika jiƙawa Mama ” shi ne abin da ya ce.

Na ce “ya ida ai dama guda ne ya rage”

“Bani kwalinsa ”
“Bai da kwali ”
“Ina aka taɓa sayar da magani babu kwali?”
“Wannan ɗin ba sayar da shi ake yi ba ai,na gargajiya ne”

“Ina son ganin ledar da aka ƙulla shi to” ya faɗa cikin son sai ya ƙure ni,na ɗago kai na kalle shi kafin na juyar da idona gefe na ce “na share ledar”

Bai ƙara cewa komai ba ya fice ƙuuu tare da banko ƙofa.

“Ina ga gida zan je zuwa an jima sai na dawo, wannan masifar ba ta ida ba wallahi sai ya sake dawowa kin san shi da zafin kai.Kuma ni ban son ganinsa cikin wannan halin duk sai na ji babu daɗi kuma gwiwaina su yi sanyi” Lubna ta faɗa tana yin wani kalar tausayi.

Na taɓe baki na ce “ni ban ga abin da kika gani a jikinsa ba da har kike wani sonsa haka,mutum a bushe kamar mai cutar  HIV sai shegun manyan ido kamar ƙuliƙuli dama-dama dai lips ɗin nasa su ne kawai masu kyau”

Lubna ta yi min dundun wasa ta ce “ke ban fa son rainin hankali,alhajin ne kike shammata haka? Haba dai! Kuma ni ba sonsa nake yi ba kawai dai yana burge ni” ta ƙarashe zancen tana wani murmushi mai tona asirin zuciyarta.

Canza zancen na yi na kamo wani,“ sai yaushe za ki dawowa nan da kwana? Allah na gaji da zama ni ɗaya cikin ɗaki kamar mayya”

Lubna ta ce “ke na manta ban faɗa miki ba,ɗazu bayan kin tafi restaurant an kawo wata ƴar aiki da alamu nan za ta zauna ita ma tun da ba ta da kowa kamar ke take”

“Ni babu ruwana da wata,ke nake magana yaushe za ki dawo nan? Na ga dai san ba za a hana ki ba duba da Umma ƙawar Hajiya ce ”

“In na je yau zan tambaye ta in ji in za ta bar ni,amma da wuya kam zan dai gwada.Na tafi sai zuwa yamma zan zo kamar kullum” cewar Lubna .Sai na saka hijabi domin yi mata rakiya duk da ba wani nisa ne ke da kwai da gidan Hajiya zuwa nasu .

Muna ratso falon muryarsa ta tarbe mu sai masifa yake duk a kan maganin da na bai wa

uwarsa ta sha ta warke.
Muna haɗa ido da shi ya ce “nan gaba duk ƴar iskar da ta sake bai wa Mamana maganin ƴan bori sai na kulle ta ,kar a sake shigo mana da kayan tsibo cikin gidan.Ke ma Mama ki rasa maganin da za ki sha sai na gargajiya? To mene ne amfanin karatun likitacin nawa?”

Ban kula shi ba don na fahimci tun ranar da na zo nan gidan ya tsane ni,wannan dalilin yasa ni ma yake ban haushi.Muna fitowa daga gidan Lubna ta ja wata ajiyar zuciya a bayyane kafin ta ce,“matar Maheee nada jan aiki,a yi mutum sai masifa kuma sam bai ma gajiya ”

Na ce “shi yasa yake ramewa ita ce duk ta cinye shi masifafe Allah ma ya raba ki da aurensa,don wannan ina ga har dukan mace sai yayi”

Lubna ta ƙyalƙyace da dariya ta ce “mutumniyata inda fa kike burge ni ke ɗin kamar yayen aljanu kike,to in faɗa miki jiya-jiyan nan ya ɗirka wa buduwarsa shegen duka saboda ya tarar da ita tana hira da wani ɗan ajinsu.Ina jin Hajiya na bai wa uwar budurwa haƙuri wai shegiyar zuciya ce da shi wannan yasa bai controling kansa”

Ban san me yasa na ji zuciyata ta yi min wani iri ba duk sai na ji babu daɗi,na ce “budurwa? Dama yana da budurwa ne?”

“Kin ji ki da wani zancen kuma,kamar Maheee ɗin ne zai rasa budurwa? Hum! To in faɗa miki shegen son mata ne da shi a yadda na ji Ummah na faɗa ƴan matan da yayi ba su da iyaka,in kin gansa da wannan yau to da an kwana biyu ya canza wata”

Cike da ɗacin rai na ce “amma kuma bai yi kama da mai son mata ba,duba da ko kallon su bai yi.In fa kin ga ya kalle ki to fitinarsa ce ta motsa kawai don ya tsorata ka da shegun idonsa kamar na jinjirin jinnu”

Lubna ta ce “ki shirya wata rana mu je asibitin da yake aiki ki ga yadda mata ke ɗaukar wanka saboda shi,kuma wallahi har da matan aure”

Ban ƙara ce mata komai ba na yi gaba don dama can tsaye muka yi muna ta zuba,sam ban ji wuyar tafiyar ba saboda yadda zuciyata ke azalzala tana wani irin zafi .Ban taɓa jin haushinsa sosai kamar irin na yau ba,kamar wasu kurame haka muka ci gaba da tafiya har muka isa gidansu Lubna.

A tsakar gida muka tarar da Ummah tana gyara wake,bayan mun gaishe ta sai muka shiga daga ciki.Kan katifar da ke shimfiɗe na yi wa kaina masauki na kwanta tare da yin lamo,maganganu Lubna ta kai wa junansu karo a cikin kwanyata.

“Bari na yi wanka,kin ga kunun tsamiya nan ki zuba ki sha” ta faɗa kafin ta fice,sai dai a yadda

ta bar ni haka ta same ni.Cike da mamaki take cewa “wai ba ki sha kunun ba?”

Na ɗan yamutsa fuska na ce “ban ra'ayi ne”

Ta taɓe baki kafin ta ce “ke ma ai jujun ce kamar Maheer ba a gane kanki wani sa'in ni dai ci gaba da bani labarin naki ”

Na ja ajiyar zuciya kafin na ce “zan baki har mu koma can gidan Hajiya ”

“Ni dai ki fara bani yanzu”

Na ce “a daren ranar muka faki idon Goggo Lami muka je ni da Hassana muka binciko kayan Husseina waɗanda suke ajiye ko tsinke ba a taɓa ba.Kayan da ta mutu da su wata doguwar rigar atamfa ce,tana mugun sonta wanda kusan tana yawan saka su wannan yasa har zuwa lokacin ba mu manta ta ba.A nan cikin ɗakinsu Hassana na saka rigar sannan na hauda tawa a sama,sai na mayar da hijabina.Waje muka fita kamar babu komai muka zauna cikin ƴan uwanmu muka ci abinci kafin duk a watse saboda yau babu wata hira mai daɗi da za mu yi in banda ta jajen mutuwar Haidar .
Ko da na je ɗakinmu sam ban cire hijabi ba da da shi na kwanta,babu jimawa kuwa bacci ya ɗauke ni.A cikin baccin na ji ana buga ƙofa tare da kiran sunana,na buɗe ido sai na yi tozali da Husseina sanye cikin kayan matattu wato likafani.Idonta na zubar da hawayen jini take kallona,kafin ta ɓace ba tare da ta ce min komai ba...” Lubna ta yi saurin katse ni “wai a zahiri kika gan ta?”

Na ɗan harare ta na ce “ke fa ba ki iya cin ƙwan makauniya ba,ki bari na baki labarin mana”

“To na bari” ta faɗa tana gyara zama.

Ni kuma na ci gaba da cewa “daidai nan na farka daga bacci sai na fahimci mafarkinta ne na yi,wanda kuma hakan ba ta taɓa faruwa da ni ba in ba yau da na saka kayanta ba.A lokacin wani irin tsoro ne ya kama ni sai na kasa yin bacci,don da zarar na rufe ido Husseina nake gani tsaye kusan ƙafafuna da fararen kayanta .Kwan lantarki na kunna saboda tsoro,ɗakin ya kawo haske sai na ga Innarmu zaune a tsakiyar gado ta yi tagumi da dukkan hannuwanta yayin da kuma hawaye ke yi mata shatata kamar an kunna pampo.Na matsa kusa da ita na ce “Innarmu kuka kike? Ki yi haƙuri don Allah ki bar kuka in kina yi hankalina tashi yake” ban san me ya ja ra'ayin Innarmu a wannan lokacin kawai dai na ji ta jawo ni tare da rungume ni tana mai cewa “Haule ina son nesanta ki daga gidan nan amma banda ƙarfi ko izzar yin haka,na sani ke ce ta gaba”

“Ta gaba kamar yaya? Innarmu wai mene ne kike son faɗa min?” na tambaye ta duk da a lokacin ba zan wuce shekara goma sha biyu ba amma na fahimci kamar da akwai wani sirri da

Innarmu ke ɓoye min" ina kawowa nan sai na yi shuru ina goge ƙwallar da ke yi min zuba saboda wata irin kewar mahaifiyata da ta tsirga min,na miƙe na ce "zan tafi sai kin iso"

"Jira na saka kaya mu koma tare" ta faɗa ita ma duk idonta sun yi ja,bayan ta kimtsa muka yi wa Ummah sallama muka dawo gidan Hajiya sai kuma muka tarar da wani sabon tashin hankali Maheer ne a kwance duk ya sandare kamar gawa ga kuma likita biyu kai gare shi.Ni da Lubna muka kalli juna don kuwa tuni muka san mene ne matsalar,da kuma maganin da zai warkar da shi.....
[23/05 11:29] MRS SADAUKI: *BAƘIN RUHI*🧌🐲

```LoVe aNd HoRrOr story```👽

By
Chamsiya Laouali Rabo
{MRS SADAUKI💫✍️}

*SADAUKARWA :* Ga dukkan iyayenmu MATA da suka tsaya tsayin daka don bamu kariya a kan dukkan wani da ke son cutar da mu.

*FCWA*☀️

---

03

Daga inda nake tsaye muke ƴar kallon-kallon ni da Maheer,kallo ne yake yi min wanda ke nuni da cewa eh ya san komai a kaina.A yadda yake juya idonsa tuni na fahimci abin da ke zuciyarsa,magana yake yi min ta ido wacce kuma sarai nake jin abin da yake cewa tamkar da bakinsa ne yake magana.

"Ki zo ki cire min ƙwayar kambun maitarki da kika jefa min ,in kuma mutuwata ce farin cikinki shi kenan sai ki ci gaba da riƙon inuwata da kika damƙe"

Ido na lumshe bayan na gama saurarar abin da ke fito wa daga idonsa,maimakon na basa amsa ko yi masa zancen abin da ya shafi maganin cutarsa sai tambaya da na jefo masa ni ma ta ido kamar yadda yayi min ,"wane ne kai ? " ƙin bani amsa yayi sai ya juyar da kansa gefe.
```

“Kar dai ki ce min zargina gaskiya ne ke ce kika jefa shi cikin wannan halin?” Lubna ta tambaye ni tana mai matso bakinta kusan kunnena.“Ki ɗauko kofin ruwa ki same ni a ɗaki” shi ne abin da na ce mata kafin na yi gaba abina,babu jimawa kuwa ta shigo kofin hannunta na karɓa na yi ta kallon ruwan na ƴan sakanni kafin na tofa yawuna a ciki suka fara tafasa suna canza kala a sannu-sannu,sai kuma na ƙara tofa wasu sannan na miƙa mata kofin ta fita.

Na ja wata ajiyar zuciya ina jin duk babu daɗi yadda ya wahala domin ni,duk da cewa ni kaina ban son hakan nake yi ba na cutar da mutanen da suka ɓata min rai.
Na saki ɗan murmushi a fili na ce “ko wane ne shi? Ta ya aka yi yake magana da ido?” ban kai ga samo amsa ba Lubna ta shigo tana yi min wani kallo kafin ta ce “sai ki je suna son yin magana da ke”

Na ce “su wa?”
“Likitocin da suka kasa yi masa magani mana,a gabansu na basa ruwan ya sha ya kuma tashi daram ya zauna kan ƙafafunsa shine suke son sanin sunan itaciyar maganin da kika yi amfani da ita”

Banda kallonta babu abin da nake yi,kafin ma na ce wani abu Hajiya ta shigo ɗakin tana washe baki tare da kamo hannuna ta ce “zo mu je yarinya kin zama cele ai ,manyan likitoci sun kasa maganin cutar Maheer amma maganinki na gargajiya ya warkar da shi garas.Kar ki so ki ga yadda na fita a guje neman taxi ni na manta ma da akwai mota a gidan,ina dawowa kuma aka ce ke ce kika basa maganin” tana maganar ne tana jan hannuna har muka iso falon.

Wani irin faɗuwa gabana yake yi,ga manyan likitocin da duniya ta san da su don har a tv ana nuno su.Duk sun gyara zama suna jiran amsa daga gare ni,shi kuma gogan ya wani haɗe rai kamar ba shi ne ya gama shan yawuna ba yanzu.

“Ga ta nan ita ce mai maganin” Hajiya ta faɗa tana wani murmushi kafin ta ɗan bangaje ni ta ce “ki gaishe su”

A ɗan rikice na ce “ina wuninku?” kusan duk a tare suka amsa kafin ɗayan ya ce “hajiya dama wannan ce ai kamar na sha ganinta restaurant ” yayi furucin yana wani sanyayyen murmushi yana ɗan ƙare min kallo.

“Eh ita ce, tana ɗaya daga cikin masu kula da restaurant ɗin ai” Hajiya ta faɗa .

“To likitar gargajiya muna son ganin maganin naki ” ya ƙara faɗa wannan karon cikin raha.
Da sauri na kalli Hajiya kafin kuma na maida dubana ga Maheer wanda nake jin idonsa a kaina tun ɗazu.

“Eh muna son gani Please ” shi ma ɗayan likitan ya faɗa.

Hannuna na ji yana jimƙewa da kansa,yayin da kuma nake jin muryar Maheer tana furta wasu harufa cikin Yaren da ba na Hausa ba,haka ma turanci.Kallonsa na tsaya yi yadda sam bai nuna alamar yana yin wani abu ba,amma tabbas amon muryarsa na fita wanda ina da tabbacin iya ni ɗaya ce kawai nake jinta.
Ba a ɗauki lokaci ba na ji wani abu jimƙe cikin tafin hannuna,sai na ɗago hannun tare da buɗe shi nan idona yayi tozali da wata koriyar flowers mai masifar haske.

“Waooo! ” likitan ya faɗa yana mai zuwa ya ɗauke flowers ɗin daga tafin hannuna kafin ya ce “wannan ai furen floris,Dr Muhamud ka tuna Dr Maheer ya taɓa nuna mana ita?”

“Eh sosai ya ce tana maganin komai amma a lokacin ba mu yarda ba,amma Umar ba ka ganin kamar abin nan camfi ne?”

“Ya isa haka don Allah,ku bata furenta ta tafi kun tsaya surutu sai ka ce yau ne kuka fara ganin abin almara” Maheer ya faɗa cikin ɗaga murya,duk suka tuntsire da dariya kafin su fara tsokanarsa can kuma shi Dr Muhamud ɗin ya zo ya miƙo min furen,sai da na saci kallon Maheer kafin na karɓa.Har tuntuɓe nake wurin barin falon,ina shiga ɗaki na ja wata doguwar ajiyar zuciya ban taɓa jin tsoron Maheer ba sai yanzu har wani ƙwarjini na ga ya ƙara min.

Ban tarar da Lubna ba, kitchen na wuce don na fi zaton tana can amma kafin nan sai da na ɓoye furen floris ɗin cikin kayana.Ai kuwa can na same ta tana ta aikin tuwon gobe,wuƙa na ɗauka na soma yanka mata albasa ba tare da na ce komai ba.Ita ma sai ta ƙi tanka ni sai ma waƙe-waƙe da ta tsira wanda kusan duk na habaici ne.

Na yi ɗan murmushi na ce “ko ki tambaye ni yadda muka yi”

Ba tare da ta dube ni ba ta ce “ai na san ba za ki kasa nemowa kanki mafita ba tun da kamar aljana haka kike ”

“A'a aljanar ce ba kama ba” na faɗa ina dariya .
Ta ce “to ƙila ɗin ma haka ne tun da babu wanda ya san abin da ke cikin duhu”

“Amma kin san da cewa na tsorata sosai?” na tambaye ta ina mai tsayawa da yankar albasar.
Ta ce “na san dai ba na Maheer ba sai dai ko abokansa”

“Wai ke duk komai kin sani game da shi? Ya aka yi kika san abokansa ne?” ba ta kai ga bani amsa ba Hajiya ta shigo kitchen ɗin,wata ƴar matashiyar budurwa na take mata baya.

“Lubna ga sabuwar ƙanwa na samo miki,za ta dinga taya ki aiki ki dinga nuna mata komai yadda ake yinsa,don ina sa ran ƙara sunayen jerin wasu sabbin abinci”

Cike da ladabi ta gaishe mu duk da dai ko na girme mata ba irin can ba,Lubna ta ce “me sunanki?”

“Aliya” ta bata amsa sai muka ɗan kalli juna,Hajiya ta ce “mene ne kuma?”

“Babu komai” muka amsa mata.
Har ta kai bakin ƙofar fita ta ce “Haule ki haɗa wa Alhaji tea ki kai masa ɗakinsa ki saka citta dayawa da lemun tsami”

“Wane alhajin ?” na tambaya da sauri har ina sakin wuƙar hannuna ban shirya ba,Hajiya ta juyo fuskar nan kicin-cikin kafin ta ce “alhaji nawa ke da kwai gidan nan?”

Sai da na haɗiye wasu yawu kafin na ce “ɗaya” sai kuma ta juya ta yi tafiyarta.Jikina na ɗan ɓari na ɗora tukunya kan gas na soma haɗa masa tea ɗin wanda dama can ni nake yi amma ban taɓa kai masa shi ɗakinsa ba ina dai jera su kan dianing.

Tsit kitchen ɗin ta yi sai Lubna da ke magana jefi-jefi tana kwatanta ma Aliya yadda ayyukan ke tafiya.Ni kuma ina gama dafuwar tea ɗin na juye shi cikin flask na ɗora kan tray da kuma kofukansa,sai da na dubi Lubna kafin na fita na yi tunanin za ta cece ni ta ce na kawo ta kai.

Tun da na fara taka step ɗin da za ta kai ni ɗakinsa jikina ya soma rawa,hakan ya bai wa kofukan yin ƙara suna fitar da wani sauti.
Bakin ƙofar na ja na tsaya,na fi minti biyu kafin na danna ƙarar rawar neman izinin shiga.Ƙofar ce ta buɗe da kanta,wani sanyi ya ratsa ni haɗi da wani dadaɗan ƙamshi.Murya can ƙasan maƙoshi na yi sallama,ba tare da kuma na ɗago kaina ba.

“In kika zuba min ruwan zafi mugun duka zan yi miki fiye da wanda aka baki labari” na tsinkayo muryarsa.Da sauri na ɗaga kai sai na ga ashe ina kusa da shi,hannuna na rawa na ajiye trayn kan table ɗin madubi da ke tsakiyar lafiyayyun kujerun ɗakin.Ina juyawa ƙofar ta rufe kanta,na juyo da sauri ina kallonsa murya na ɗan rawa na ce “hajiya ta ce na kawo ma tea ga shi nan,ni zan tafi”

Wani miskilin murmushi na ga yayi kafin ya ɗauki kofi ɗaya ya soma haɗa tea,bayan ya gama

ya ƙara ɗaukar wani kofin shi ma ya zuba a ciki duk ina tsaye ina kallonsa.

Ya ɗauki kofin ya soma kurɓa kafin ya ɗago ya dube ni ya ce “ki ɗauka ki sha” ko motsawa ban yi ba,sai da ya ƙara cewa “in ba ki sha shayin nan to a nan za ki kwana” ko ida rufe bakinsa bai yi ba na ɗauki kofin na soma sha da sauri duk da kuwa yana da zafi.Ina gama shanye wa kuwa na ji ƙofar ta buɗe da kanta,da wani irin sauri na juya har da ɗan guduna don gani nake in na tsaya wasa ƙofar za ta sake rufewa.

Da na fito ji na yi tamkar na baro wuta ne na shigo aljanna, kitchen na koma na taya su aikin sai da aka kira sallah na fita.
Ko da na gama sallar ma ban koma ba,ɗaki na yi zamana don gobe ni ma a tsaye zan wuni aikin kai wa mutane abinci.Har sai da aka yi sallar isha'i sannan na fita zuwa ɗayar kitchen wacce ita kuma iya girkin gida kawai ake yi a cikinsa.Kuloilin da ta zuba abinci na soma ɗauka ina kai wa can kan table ɗin cin abinci,bayan na gama sai na ɗauki kwanon abincinmu wanda aka sauya mai girma ƙila saboda zuwan Aliya ne.Ko da na koma ɗaki sai na tarar da su duk sun shigo,Lubna ta fara shiga wanka sannan ita ma ta yi daga nan sai na juye abincin cikin babban faranti muka muka soma ci amma sai na lura Aliya babu abin da take sai satar kallona,tun ban damu ba har na tsargu na ce “Lubna ƙanwarki sai kallona take ki tambaye ta halan na yi mata kyau ne”

Lubna ta yi ɗan murmushi kafin ta ce “to ke kin ji Aliya wai kina kallonta”

Maimakon ta kawar da dubanta a'a sai ma ta ƙara ƙure ni da ido kafin ta ce “na ga ba ta lafiya ne”
Da mamaki na ce “wa ya faɗa miki banda lafiya?”

Sai da ta saki wani murmushin kafin ta ce “ga gubar maciji nan tana yawo a jikinki”
Kasa ci gaba na yi da cin abincin,ban ce komai ba sai Lubna ce ta yi magana “wace irin magana ce wannan? Ya za ki ce guba na yi mata yawo a jiki? Ke ta ya aka yi kika sani? Ke ki bar ma wannan maganar don in wani ya ji sai ya ce mayya ce ke,Ah to in ba maye ba wane ne zai iya ganin abin da ke cikin ɓargon jikin mutum” Lubna ta ƙarashe cikin faɗa yayin da ita kuma Aliya ta kai hannunta kan goshina ,nan take wani baƙin ruwa suka soma zubo min ta baki da hanci.Kamar zan mutuwa haka na ji yayin fitar abin,can kuma ta janye hannunta wanda yake ta kunno koren haske daga can tsakiya tamkar an kunna lantarki.
Lubna ta zabura ta tashi tsaye tare yin baya tana “Ya Rasulullahi! Manzon Allah!”

Ni kuwa ido na zuba wa Aliya ko kafin na ce wani abu an turo ƙofa,Maheer ne.Da sauri ta ɓoye hannunta mai hasken a bayanta,shi kuma ni ya kafe da ido kafin ya saki murmushi ya ce “kar ma ki ɓata lokacinki ko kin yi yunƙurin fitar da shi ba zai fito ba”maganar ido ce yayi min ya fice,sai kuma na fahimci cewa ba wai iya ni ɗaya ce wannan karon na ji shi ba har da Aliya wacce jikinta ya ɗauki kyarma tun lokacin da ta ga Maheer ɗin.

“Wace ce ke?” na jefo mata tambayar,ba ta bani amsa ba sai tashi da ta yi a guje za ta gudu amma tamkar wata ɓarauniya haka na yi saurin cabko ta na riƙe ta gam ina mai ce mata “wallahi babu inda za ki sai kin faɗa min wace ce ke”........
[23/05 11:29] MRS SADAUKI: *BAƘIN RUHI*🧌🐲

```LoVe aNd HoRrOr story```👽

By
Chamsiya Laouali Rabo
{MRS SADAUKI💫✍️}

*SADAUKARWA :* Ga dukkan iyayenmu MATA da suka tsaya tsayin daka don bamu kariya a kan dukkan wani da ke son cutar da mu.

*FCWA*☀️

________________________

04

Jikin Aliya ne ya soma yin rawa kamar mazari kafin ta ce,“don Allah anty Haule ki bar ni na tafi wallahi in ya gano ni ce nan na yi masa kutse zai iya hallaka ni ”

Cikin ɗaga murya na ce “ba fa zan bar ki ba ,gwara ma ki bani labarinki kuma muddin ina tare da ke to babu abin da zai iya yi miki.Hatta ita gubar da ya bani na sha ba wai don ya cutar da ni ba ne a'a don ya dinga controling tunanina ne”

Lubna da ke can tsaye a raɓe ta ce “wato kenan kin san da gubar ma a jikinki? Innalillahi wa'inna ileyhi raji'un! Allah ka tausaya wa rayuwata kar ka ƙara jefa ni cikin wani cakwalkwalin uƙubar da na tsira a baya”

Na dube ta kafin na ce “don Allah Malama ki zo ki zauna kika wani tayar da hankalinki sai ka ce baƙuwar ganin abubuwan nan na siddabaru”
```

Wata muguwar harara ta jefo min kafin ta kalli Aliya wacce har zuwa yanzu hannunta na fitar da wannan hasken.

“Wace ce ke Aliya?” na sake jefo mata tambayar a karo na biyu.
Kai tsaye ta bani amsa da cewa “ni ɗin almajira ce,na taso cikin Bara na kuma girma cikinta.Ni ɗin ba muguwa ba ce kamar yadda kika yi tunani,duk da kuwa ina ɗauke da BAƘIN RUHI a gangar jikina amma ban taɓa cutar da wani ba sai dai na bai wa kaina kariya ga masu son cutar da ni”

Na ja wata ajiyar zuciya kafin na ce “amma me yasa kike jin tsoron Alhaji?”

“Saboda shi ne babba a gare ni,powersa ta fi tawa ƙarfi sannan a tsarin zubin halitta protector ɗinsa ya fi nawa tasiri”

Ina jin abin da ta ce sai na dubi Lubna wacce goshinta ke tsatsafo da zufa.Na saki ɗan murmushi kafin na ce,“na ga powerki irin wacce ake iya sharing nata ne ,ko za ki taimaka ki gutsurawa Lubna ko da ɗigo biyu ne?”

Aliya ta jinjina kai kafin ta dubi Lubna wacce ke shirin artawa a guje amma na harɗe ƙafafunta ta hanyar kallo kawai,don ina juya idona ta kasa motsi na riƙe su gam.
Na miƙe tsaye ina riƙe da Aliya har zuwa yanzu,ita ma tashin ta yi da taimakona ta samu ta dafa goshin Lubana koren hasken ya fita shuuu kamar yadda ake zuba man fetur a babur,yana fara shiga kuma ta yi saurin janye hannunta.

Na saki murmushi na ce “yanzu dukkan tsoronki zai fice,shi kenan ke ma kin dawo tsagenmu”
Da idonta da suka kaɗa suka yi jawur lokaci guda take kallona amma ta kasa magana,ban damu ba don na san ƙarfin ikon sarrafa wani yankin power Aliya ne ke ratsa jininta.

An ɗauki kamar minti goma kafin Lubna ta dawo normal,ta ja wata ajiyar zuciya kafin ta ce “Haule kin kyauta kin mayar da ni mai ido uku,sai dai ki sani yau ba zan bari ki rumtsa ba sai kin bani labarinki duka”

Na yi ƴar dariya kafin na ce “labarina nada tsayi sosai Lubana amma ke ki fara bamu naki,in kin gama sai Aliya ta ɗora daga ƙarshe ni kuma  sai na dinga baku nawa lokaci zuwa lokaci”

Da sauri Aliya ta ce “eh hakan yayi gaskiya” sai duk muka samu wuri muka zauna.

Yanayin fuskar Lubna ya canza kafin ta ce “ban ma san daga ina zan fara ba,farko dai zan iya cewa na yarda da karin maganar nan da Hausawa ke yi ' ba duka ƙyalƙyali ne gwal ba' tabbas na yarda da hakan bayan shekaru biyu da suka gabata na rayuwata.Kamar dai kowacce ƴar

talakawa haka na tashi da burin samun aiki mai tsoka , wannan yasa na kashe kaina wurin yin karatu tuƙuru.Na bi duk wani matakin ilimi da kika sani,na yi digiri har da digirgir sai dai fa samun aiki ne ya zama jan aiki.Tun ina ajiye takarduna har na gaji na bari,cikin haka ne Umma ta sama min gurbin aiki nan wurin Hajiya can farko iya zuwa can restaurant ne aikina ina kai wa costumer abinci .Kamar yadda kika sani iya wannan aikin kawai ba wani kuɗi ne masu yawa ba,amma haka nake yi don gujewa zaman banza.Sama da wata biyar ina wannan aikin ,daidai ɗaya rana ban taɓa cire burina na samu babbar kujera akan karatun da na yi ba.Sau tari ina jin haushi in na ga masu kuɗi suna shigowa nan su ci abinci na kuɗaɗe dayawa har su bar ragowa nan.Masu zuwa da ƴan mata kuwa haka zan zauna ina ta kallon yadda maza ke tattalinsu,duk abin da kika duba a jikin ƴan matan kuɗi kawai ke magana.Sai fa rayuwarsu ta soma burge ni ina sha'awar cewa ina ma ni ce,zan iya ce muku ma har hassadarsu ke tsarga min musamman in na ga mace wacce ba ta yi wani dogon karatu ba amma tana da kuɗi sosai nake jin haushi.Sai kuma ƙarfin imanina yayi ƙasa ina ganin Allah ya azurta kowa amma ni ya bar ni cikin ƙuncin talauci ni iyayena waɗanda kusan ma a lokacin ni ce ke kula da su saboda Abbana da ya samu karaya bai aikin komai.

Kusan da wannan burin yin kuɗi nake kwana nake kuma tashi da shi har Allah ya jefo min wata ƙawata da muka yi makaranta da ita.Ba zan manta ba wata baƙar rana ce wacce ta shiga lissafin ƙaddarata,ina kwashe plate ɗin da aka ci abinci na ji muryar wata da na sani ta kira suna “oh Lubna ? Ke ce?” ni ma cike irin zumuɗin nan irin ka jima ba ka ga mutum ba na nufe ta zan rungume ta amma don wulaƙanci ta yi saurin ja baya tana yamutsa fuska kamar ta ga kashi kafin ta ce “wai ƴar aiki kika zama bayan duk uban karatun da kika yi? Ki rasa abin da za ki yi sai tarben customer ?”

Duk da na ji babu daɗi haka na danne zuciyata na ce “to ya zan yi tun da ban samu aikin gwamnati ba,faɗa min Zulaihat ina kike aiki?”

Ba ta bani amsa ba sai wuri da ta samu ta zauna kan ɗaya daga cikin kujerun da ke wurin,“me ke da kwai marar nauyi ? Don yunwa nake ji shi yasa ma na tsaya da motata cikin rana na ci abinci na wuce” ni kuwa gwiwaina ne suka yi sanyi jin Zulaihat ce wai da mota duk da ban yi mamaki ba duba da suturar jikinta iya jakarta ma tana iya ciyar da ƴan gidanmu na tsawon wata biyu,uwa uba kuma wayarta iphone wacce kusan duk masu zuwa restaurant ɗin nan ina ganinsu da ita.
Jiki na yi min ɓari na ce “jira na je na kawo miki” sai na koma can ciki na haɗo mata abincin da na san ƴan gayu irinta na so har da lemun kwalba,da na kawo mata  sai ta bani damar zama kan kujerar da ke kallon tata.A kunyace na zauna, Allah yayi min sa'a ma babu kowa.Cike da yanga take juya cokali cikin plate ɗin kafin ta soma ci tana latsa waya,message ne na WhatsApp ta soma kunna wa ina saurare kusan duk akan manyan kuɗi ne da kuma kayan da mutane suka yi oder ko kuma suka saya suka yaba,can kuma ta soma mayar wa na ji tana zancen za ta tura miliyoyin kuɗaɗe.Ni kuwa ina zaune sake da baki ina kallonta,kuma kar ku ji zancen wasa wallahi burge ni ta yi yadda take abu na ƴan gayu.Hummm! Faɗar mintinan da na share a zaune kafin Zulaihat ta dube ni ƙaramin misali an fi goma sha,can ta ɗago ta dube ni da

idanunta da suka sha gashin zamani ta ce “Lubna gaskiya ba zan ɓoye miki ba na ji takaicin ganinki a wulaƙance kina boyi-boyi,da kyawunki da iliminki.Amma dai komai ya wuce tun da Allah yasa mun haɗu zan duba na gani”

Ba tare da na san wane aiki ne za ta samo min ba na shiga yi mata godiya,nan ta shiga nuna min hotunanta da ta yi ƙasashen duniya .Ni kuma sokuwa girman burina sai ƙara farashi yake ina jin cewa ni ma nan gaba kaɗan zan koma kamar Zulaihat,da za mu rabu sai ta bani lambata da ke jikin wani ɗan ƙaramin kati mai ɗauke da dukkan address ɗinta da kuma kantinta na business.Ba ta bar ni haka ba,sai da ta ware dubu goma ta bani shi ma wai don ba ta da canji ne kuɗinta duk daloli ne.

Da na isa gida kasa bacci na yi,haka na yi ta juyi kan shimfiɗa .Saƙo kuwa na rubuta shi ya fi cikon casbi kuma sai na goge a ganina sam ba ta cancanci in yi mata text ba.Can na daure na kira ta, lokacin ƙarfe goma saura kwata na dare,har zan yanke kiran sai kuma na ji ta ɗauka tana cewa “Lub baby ƴar halak kin ƙi ambato yanzu na gama maganarki wurin oga ”

Na washe baki na ce “na zata ma kin yi bacci,na gode sosai da wannan ƙoƙari me ogan ya ce ?”

“Ki zo gobe nan babban kamfani yana son ganin ki,sannan ki haɗo da takardun karatunki sai takardar shaidar ɗan ƙasa da kuma hotonki kala biyu ”

Tamkar na yi hauka haka na ji lokacin ba tare da na san ƙaddara ce da rabon a yi ke ja na ba.Tun a daren na jawo ambalof na shiga haɗa takarduna don dama kusan ina da komai da ake buƙata in aka fidda hoto.Bacci ɓarawo ne ya ɗauke ni a wannan daren,shi ma rabi da rabi ne.Tun bayan sallar asubah na shaidawa Umma zancen aikin sosai ita ma ta yi murna.Zuwa ƙarfe takwas na je gidan hoto aka yi min guda biyu,a nan take kuma aka bani su.Daga nan na kira Zulaihat sai ta ce na jira za ta zo ta ɗauke ni,ina nan tsaye ina jiran zuwanta sai wata tsohuwa ta tsaya kusa da ni tana mai neman sadaka .Murnar na samu aiki yasa na zuge jaka na bata sadaka,tana karɓar kuɗin sai ta soma juya su haɗi da kallona tsakiyar ido ta ce “ƴata ki koma gida inda za ki je ɗin nan babu alkhairi ” wani irin haushin ta bani kafin ma na kai ga yin magana Zulaihat ta parker motarta tana yi min horne,da sauri na zagaya na buɗe na shige ina jin tsohuwar nan na sake jaddada min maganarta amma na yi kunnen uwar shegu da ita .

Fuska a sake muka gaisa kafin ta ce “ke ma dai kin kusa ki faso gari ki huta da yawon raba abinci a restorant”

Na yi murmushi na ce “ai kuwa dai kin ga ban ma shaida wa Hajiyar na samu aiki ba”

“In an gama miki interview ai sai ki je ki sanar da ita”

Haka muka ta yin hira har muka isa wani katafaren kamfani,duk da ina cikin garin amma ni ban taɓa ganinsa ba da idona ina dai jin labarinsa.Tun da muka fito daga cikin mota ake gaishe da Zulaihat,sai na fahimci tana da babban matsayi a wurin .
Jikina ne ya soma yin rawa lokacin da muka shiga ofis ɗin ogan,komai na wurin ja ne tun daga labulaye capet da kuma kujeru.Hatta kalandar da ke ɗauke da jerin sunayen watanni ita ma ja ce,haka ma book ɗin nan da mutane ke ɗauke abu mai muhimmanci shi ma ja ne.

Wuri ta nuna min na zauna kafin ta ce “jira yanzu zai fito” sai na sakar mata murmushi kawai ina mai ci gaba da sauraren bugun zuciyata.Kamar minti biyar haka wani babban mutum ya fito,baƙi ne wulul kuma gajere yana da ƙiba sosai ga kuma ƙaton tumbi kamar mai cikin wata tara .

Cike da girmamawa na sauka na gaishe shi har ƙasa,ya amsa cikin sakewar fuska kafin ya bani umarnin na koma inda nake.Zulaihat ce karɓi takarduna ta miƙa masa,a nutsu ya shiga duba su kafin ya soma yi min tambayoyi ina basa amsa daidai da abin da na sani.

Ya yi wani murmushi da ya ƙara bayyana muninsa kafin ya ce “Zuly ƙawarki nada kaifin basira kam,ina ga ita ya kamata mu baiwa kujerar mai kula da baƙinmu na waje ko ya kika ce?”

Ta yi wani murmushi tana mai cewa “ai kuwa ko a makaranta ita ce ta ɗaya,sannan ta saba jagorantar duk wani abu da ya shafi jagoranci ina ga babu matsala in dai ta yarda za ta yi”

Sai duk suka maido dubansu gare ni,wata irin rikicewar na yi da kuma mamakin ƙarshen furucin Zulaihat wai in na yarda.To me zai hana na yarda ? Abin da na jima ina nema ɗin shekara da shekaru.

“Ba ki ce komai Luby” Zulaihat ta faɗa .
Muryata har rawa take na ce “na yarda mana ina so,in dai maganar turanci ce ai kin san nan na fi ƙwarewa babu wata matsala” ina gama faɗar haka sai ogan ya miƙo min wata takarda haɗi da jar biro ya ce na saka hannu a ƙasa wanda ke bada tabbacin na yarda da dukkan sharuɗan zan yi aiki a kamfanin .
Hum! Haule kin san dayawa mutanenmu ƴan Afirka muna yin babban kuskure shi ne saka hannu a takardar da ba ka karanta jawaban da ta ƙumsa ba,to ni ma a lokacin haka na rabbata hannu na miƙa masa.A tare suka saki wata ajiyar zuciya mai bayyanar da tsantsar farin ciki.

Sai a lokacin kuma ogan ya buɗe ƴar takardar da ke ɗauke da hotunana biyu,ɗaya ya ɗauka sannan ya buɗe wani fayil mai ɗauke da hotunan mutane dayawa sannan ya maƙala nawa tare da yi masa wani rubutu can ƙasa.
Bayan ya gama sai ya dubi Zulaihat ya ce “ki kai ta wurin shopping ki tabbatar kin zaɓa mata kayan da za su fi dacewa da aikinta,sannan inda buƙata har gyaran jiki a yi mata .Kin dai fi ni

yadda ya kamata na bar miki komai a hannunki,sannan zuwa gobe za ta soma aikin kuna iya tafiya”

Ba mu ƙara cewa komai ba muka fito,cikin yanayin tsarguwa na ce “Zulaihat mene ne kuma na yin gyaran jiki? Halan datti gare ni irin sosai?”

Ta tuntsire da dariya ta ce “in ba abinki ba ke da za ki tarben turawa in ba ki kama kanki ba kina ganin za su yarda su zuba hannun jari a kamfaninmu?”
Murmushi kawai na yi na basar,daga nan gidan gyaran jiki ta kai ni cikin wata ƙatuwar inji na shiga iya kaina kawai ke waje shi ma bayan an gama wannan ɗin sai da aka saka min relax aka sa ni a tukunyar busar da gashi.Bayan mun gama komai sai ta saya min wata doguwar abaya wajen matar mai gyaran jikin,na saka sai na dawo tamkar wata balarabiya na yi kyau sosai.Daga nan gidan cin abinci muka je bayan mun cika tumbinanmu sai muka wuce mall,yadda na ga Zulaihat na jido riga da wando yasa na yi mata magana don ba zan iya saka su ba amma sai na ta saurare ni.Bayan su kuma ta saya min har da after dress da kuma sari ,wasu kayan ma ban san da irinsu ba.

Na yi tunanin gida za ta kai ni amma sai ta wuce da ni gidanta,a falo muka zube ta sa masu aikinta suka kwaso tulin kayan da ta sayo min kowanne da takalminsa.
Sai da aka kawo mana kayan maƙulashe muka taɓa tare da jus sannan na soma duba kayan,sai dai ban ɗauki lokaci ba bacci yayi awon gaba da ni a nan take kuma na soma yin wani mafarki marar kan gado.....
[23/05 11:29] MRS SADAUKI: *BAKIN RUHI*🧌🐲

```LoVe aNd HoRrOr story```👽

By
Chamsiya Laouali Rabo
{MRS SADAUKI💫✍️}

*SADAUKARWA :* Ga dukkan iyayenmu MATA da suka tsaya tsayin daka don bamu kariya a kan dukkan wani da ke son cutar da mu.

*FCWA*☀️

---

05
```

Mafarki ne wanda sam rabon da na yi sa ina jin tun lokacin isar min da saƙon balaga.Sai da wannan ya sha banban da wancan,don wannan sarai ina ganin wanda ke tarayya da ni.Ba kowa ba ne ba sai oganmu wanda yanzu ya gama yi min interview,abin mamaki kuma a cikin mafarkin bai fi yadda yake yabona ba yana cewa “ashe Zuly ta yi gaskiya kina da taurari masu kyau masu haske,ke ɗin maƙurar ilimi ce” ban farka ba har sai bayan komai ya kammala.A hankali na buɗe idona da suka yi min nauyi,sam ni na manta ma a inda nake sai bayan na watsake ne na tuna gidan Zuly ne nake.

A hankali na tashi zaune ina jin duk jikina na yi min ciwo kamar wacce aka yi wa shegen duka.Ta zo da murmushinta ta ce “ashe kin tashi? Bari na sa a haɗa miki ruwan wanka in kin gama sai ki ci abinci”

Ɗan murmushin yaƙe na yi na ce “to” sai ta ƙwala kiran ƴar aikinta bayan  ta zo ta faɗa mata aikin da za ta yi sai kuma ta dube ni kamar mai son tantance wani abu kafin ta ce “kayanki suna ɗakinki an jera a drower”

Abun mamaki kasa yi mata muso na yi ko kuma na tambaye ta yaya na samu ɗaki a nan gidan.Ita ce ta yi min jagora na isa can ɗakin wanda tuni an haɗa min ruwan wanka a baho,kar ku ji zancen wasa a ranar nan Zuly ce ta yi min wanka tamkar wata ƴarta ni kuma na kasa yin wani kataɓus.Duk da ina tune na yi mafarki amma sam tunanina bai bani na tsarkake jikina ba,saboda controling nasa ake yi.Bayan na fito ita ce ta bani kayan da na saka,sannan aka kawo min abinci kamar yadda ta shaida min tun farko.A cikin abincin nan Allah kaɗai ya san irin kalar maganin da aka saka min amma a haka na ci,kar ku tambaye ni maganar sallah don dama can farko ni ɗin na kasance mai wasa da ita ba kullum nake cika biyar ba sai in Umma ta yi min faɗa wannan yasa ko kaɗan ban samu ƙarfin zuciyar yunƙurin yinta ba.
Ina cin abinci Zuly na yi min hirar yadda aikina zai kasance a gobe da kuma yadda tsarin yake,sai kuma ta soma nuna min yadda ake yin aiki da wata ƙatuwar waya bayan nan kuma ta kira ƴan aiki biyu suka yi min tausa da wani man da aka tanada don yin tausa sai dai shi sun garwaya shi da gubar tsafinsu.
Har cikin ɓargon jikina nake jin yana ratsa min ,a sannu a hankali kuma bacci ya ɗauke ni nan ɗin ma mafarki na yi gani nan a wani ɗakin taro duk turawa ne ciki ni ɗaya ce baƙar fata.Masayar turanci kawai muke yi kowanne na yaba kamfanin da yake yin aiki,bayan mun gama meeting kuma sai muka je muka yi wanka cikin swimming pool maza da mata haka duk muka shiga ciki babu wata suturar kirki.Ina farkawa wannan karon babu kowa a ɗakin sai ni ɗaya,sannan babu wani haske sosai shuru na yi ina daidaita tafiyar numfashina.Daga nan kwance na ga lokacin da wata baƙar inuwa ta fita amma ban iya tantance ta mace ce ko ta namiji.
Kamar minti biyu sai ga Zuly ta shigo tare da kunna ƙwan lantarki,na lumshe ido tare kuma da buɗe su.
“Ki tashi ki shirya ƙarfe bakwai saura ”shine abin da ta ce min.
Da mamakin jin wai har dare yayi gari ya waye na ce “kina nufin yanzu safiya ce?” wani irin kallo ta yi min kafin kuma ta fita,na sauke ajiyar zuciya na tashi na shiga toilet sai a lokacin kuma na lura da an canza min kayan jikina zuwa na bacci.

Cikin bahon wankan na shige,ina tunanin kaina a can ƙasan zuciyata sai dai fa na kasa tuna wace ce ni daga ina nake abu guda kawai ke cikin ƙwaƙwalwata shi ne aikina da kuma Zuly sai oganmu wanda nake jin mugun tsoronsa ya samu wuri a zuciyata ya zauna daram.

Bayan na gama wankan sai na fito,da taimakon wasu turawan masu aikinta na kimtsa cikin wasu arnan kaya riga da wando waɗanda suka ɗame ni sosai suka fitar da shap ɗina.Tamkar wata ƴar tsanar roba haka na koma na yi kyau sosai,gashin kaina kuwa an dunƙule min shi tsakiya sai aka ƙara min da ribbob na gashin doki ta yadda ya sauka har gadon bayana.

Zuly ta shigo ita ma cikin shiga mai kyau sai dai na fi ta haɗuwa kasancewar na fita kyawun fuska da na jiki.Jaka ta miƙa min da sabuwar waya irin ƙatuwar nan wacce ake aikin ofis,kafin ta ce "mu je" ta kamo hannuna,dakyar nake tafiya saboda yadda ban saba hawan takalmi masu tsini ba.

Da muka fito harabar gidan nan na ga ikon Allah don kuwa ba gidan da muka zo ba ne ni da Zuly,wannan tamkar aljannar duniya haka yake.Hatta motocin da ke wurin sun sha banban da waɗancan,cike da girmamawa aka buɗe mana gidan baya muka shiga abun mamaki har da masu take mana baya.Sai da muka hau babban titi ne sannan na gane nan ɗin fa Turai ce ba Afirka ba,wani kamfani ne muka je tun a bakin ƙofa Zuly ta tsaya kafin ta ce "ki nutsu ki aiwatar da aikinki kar ki wani damu jin cewa ke ce baƙar fata a cikinsu" kai na jinjina mata kafin Bodyguard biyu su take min baya har zuwa ɗakin da za a yi meeting ɗin.

Direct kujerar da ke ɗauke da sunana na je na zauna,suna ne wanda ba wanda uba mahaifina ya saka min ba a'a Oga ne ya canza min shi ba tare da na san ta ya aka yi kuma na gane nawa ne ba.Leena shine sunan da ke jikin ɗan ƙaramin allon gabana,sai da na yi gyaran murya sannan na danna wayar hannuna wacce ke ɗauke da dukkan bayanan da za mu tattauna a kai.

"Sunana Leena daga ƙasar Kamaru,wakiliyar kamfanin El Mansoor a yau mun kawo muku wata babbar haja wacce muke fatan za ku ji daɗinta sosai fiye da sauran business namu na baya" ina kawowa nan sai na yi shuru ina yi musu murmushi su kuma duk fuskokinsu sun nuna zaƙuwar jin abin da zan ce ɗin.

Na ci gaba da cewa "a ƙididdiga ta malamanmu na spirituality sun gano cewa dayawan mutane a yayin yin bahaya mutum na zubar da kaso hamsin cikin na abin da ya shafi taurarinsa marar kyawu,yayin da kuma zubar da yawu a lokacin da mutum ke tsugunne kan salanga yake ɗauke ɗigo biyu na sinadarin tauraronsa mai haske.In muka haɗa hamsin da biyu sun tashi ɗari cicif.Na san dayawanku za su tambaya ta ya aka yi aka samu ɗari? To amsar mai sauƙi ce duk tauraro mai haske ɗaya yana daidai da kaso hamsin na baƙin tauraro,da za a saka su a injin markaɗe a garwaya su to tasirin farin tauraro ne zai ƙwace kaso mafi rinjaye.Kun ga shi kenan mun samu tauro ɗari kenan" duk shiru suka yi suna nazari amma babu wanda ya iya cankar

ainahin gamsashiyar amsar kawai sai suka fara yi min tambayoyin yadda za su yi su zuba hannun jarin wanda dama ni shi nake jira.Sai na soma yi musu bayani dalla-dalla “iya adadin kuɗin da mutum ya zuba iya adadin taurarin da zai samu,kenan kowa sai ya aiko min da saƙon abin da ya yanke ta adreshing email namu”
Ina kawowa nan sai Zuly ta shigo ita da wasu masu aiki su biyu suna ɗauke da tray,amma ita Zulyn ce ta ajiyewa kowa kofin shayi a gabansa tana ajiye min na ɗauka na soma kurɓa ina kallon yadda suke shawara a tsakaninsu.

Ba a kuma ɗauki lokaci ba kowa ya soma faɗin abin da zai zuba na hannun jari,bayan nan duk sai aka watse aka bar ni daga ni sai Zuly wacce ta danna wa oga video call tana murmushi tare da yi masa congratulations akan aikin da na yi nasara ba tare ni na san muhimmancin meeting ɗin ba ko kuma ina jawaban da na kawo suka dosa ba.

Yadda suke murna yasa ni ma na ji sanyi a raina,ina jin oga na cewa “ku tawo gida mu yi shagalin murnar a nan”

Yanayin fuskar Zuly ya ɗan canza ina ganin lokacin da ta saci kallona ta wutsiyar ido kafin ta ce “oga kana ganin lokaci yayi da Luby za ta ga zahiriya da idonta?”

“Eh mana! Ai ba zama za mu yi muna kashe kuɗi wurin controling memorynta ba kawai ku dawo yanzu,sai ku same ni a can filin hutawana ”

Da ƴar damuwa a fuskarta ta ce “oga ko dai ka tarbe mu a can ɗin,don ina gudun Luby ta yi min tirjiya ko borin hauka”

“Ki yi yadda na ce” yana gama faɗa ya kashe,sai a lokacin ne ni kuma na jefo mata tambayar da ta ɗaure min kai “Zuly wace ƙasa ce nan? Ta ya aka yi muka zo nan?”

“Ki taso mu je,yanzu kin samu amsar tambayarki in mun koma Kamaru” ta faɗa tare da nufar ƙofa,sai na take mata baya ina mai ci gaba da yi mata wata tambayar “amma ina ne nan?” ba ta bani amsa ba har muka shiga mota muka isa gida.
Da umarninta kuma na bi bayanta zuwa wani ɗaki wanda babu komai a cikinsa sai wani madubi da aka rufe da jan ƙyalle.A gabana ta buɗe shi tare da ɗaukar wuƙa ta tsaga yatsanta jini ya soma ɗiga sai ta shafi madubin nan take yayi ƙara ƙiiiii tare da buɗewa ya fitar da hoton ƙofa amma fa ba ƙofar ba ce don ba ka ganin komai sai wani farin abu kamar gajimare.

Jikina ya ɗauki rawa na ce “ina ne nan kuma Zulaihat?” na yi tambayar ne jin tamkar tunanina ya dawo normal,iya ni ɗaya kawai ke sarrafa shi.
“Ba mu da saurin lokaci Lubna ki zo mu tafi” ta faɗa tana kamo hannuna da niyyar shigar da mu cikin madubin,a tsorace na ce “mu je ina? Wai cikin madubin? Zulaihat wannan ai tsafi ne.Ina kika kawo ni? ” ba ta bani amsa ba ta wani fizgo ni muka ratsa mirror ɗin sai gamu muna yawo cikin wani iska kafin kuma ƙyaftawar ido na gan ni a cikin ɗakin Zulaihat a cikin falo.Tuni zaren

carbin tunanina ya tsinke,dukkan jikina rawa yake yi min ina son yi mata tambayoyi amma ina tsoron jin amsoshinsu don ban so a ce abin da nake zargi gaskiya ne.

Ita kuwa Zulaihat sai ta yi fuska tare da haɗe rai ta ce “ki tashi mu je Malama oga na jiranmu”

Cike da masifa na ce mata “babu inda zan je! Gidanmu zan tafi”

Nan ta yi wata dariya kafin ta ce “au haba? Kenan? To wuce ai ga ƙofa nan sai ki tafi”

Sam ban damu da gyatsen da ta yi min ba sai na fita daga ɗakin na fito harabar gidan,babu kowa a bakin get sai na je na buɗe ƙofa da zumar fita nan na yi arba da wata lukutar masifa don kuwa ruwa ne maƙil a wurin tamkar za su taɓo sararin samaniya,babu shiri na koma can cikin falon sai na tarar da ita tana shan ayaba cike da shaƙiyanci ta ce “har an dawo daga gidan ko kuwa an fasa zuwa?”

Idona ne suka kawo ruwa shaaa,ina kallon Zulaihat wacce da dukkan alamu babu ɗigon imani a ƙirjinta.Miƙewa ta yi tare da ɗaukar key ɗin mota ta ce “mu je” dole dangi na ƙi yasa na take mata baya muka shiga motar .Mai gadi ya buɗe mata gate yana wani murmushin da ya tabbatar min bakinsu ɗaya shi da Zuly duk munafukai ne,gudu sosai ta yi har muka isa gidan Ogan.Muna shiga ana kiran sallar magrib,a zaune muka tarar da shi kan kujeru na alfarma ya saka ɗan madaidaicin table a gaba mai ɗauke da cake wanda aka yi wa kwalliya kamar ba ci za a yi ba.

Tsoron Ogan ne ya ƙara ratsa ni,amma duk da haka ita ɗaya kawai ta gaishe shi.Ya amsa yana kallona kafin ya fara jawabinsa “Luby na san zuwa yanzu kin fara gane aikinki, sannan kin san cikin me kika shiga,da kuma su wa kike tare da su.Sai dai ki sani a tafiyarmu ba gudu ba ja da baya,kamar yadda kika saka hannu a yarjejeniyar tsarin aikinmu za ki yi komai da family suka buƙata wato ƙungiya,to ya zama dole ki yi shi.Sam family ba mu da matsala,ba kamar sauran ƙungiyoyin da kika sani ba ne,mu sam ba mu da buƙatar jini sai in dai mutum ne ya kawo taurin kai muke ɗaukar mataki mai tsauri a kansa.Abin da muke so ba komai ne ba sai abin da bai da amfani wurin al'umma,kamar dai abin da kika gabatar a yau wato kashi/bahaya sai kuma sperm ko yawu ko kuma audugar mata da suka riga suka yi amfani da ita shi kenan fa.Mene ne matsala a nan?” ya ƙarashe tambayar yana mai kafe ni da idonsa masu mugun dafi.

Wasu sabbin hawaye suka zubo min kafin na zube a gabansa na ce “don Allah ka yi haƙuri ka goge sunana daga ciki, wallahi na yi ma alƙawari babu wanda zan faɗa wa wannan labarin ko da kuwa iyayena ne”

Yayi wani murmushi ya ce “tuni ai iyayenki sun san da aikinki,don yanzu haka mahaifinki na asibiti an yi masa gyaran ƙafa sannan mun aika saƙon cewa yau ke ce za ki yi gadi a babbar pharmacie ɗinmu ta saida magunguna.Ko ba ki yarda ba?” yayi tambayar yana mai jawo wayarsa ya kunna min video duk abin da ya faru tun daga lokacin da aka ɗauko Abbana har

izuwa lokacin da suke asibiti an yi masa aiki ga Ummah nan zaune kusa da shi fuskarta cike da farin ciki.

Wani irin tausayin kanmu ne ya kama ni,tabbas sun yi min dabaibayin da ban isa na warware ta sauƙi ba.

“In kuma kika ce za ki bijire minti biyu yayi yawa zan aika mahaifinki barzahu” oga ya faɗa . Cikin razani na dube shi,sai ya gaskata maganar ta hanyar cewa “ƙwaran gaske ,kamar yadda kai ki ƙasar Turai bai yi min wahala ba haka zan katse igiyar numfashin mahaifinki don haka kar ki kawo min wasa ki zo ki yanka cake ɗin nan kafin ya sha iska”

Yana gama faɗar haka sai Zuly ta miƙa min wuƙa,ba don na so ba na yanka cake ɗin wanda yayi daidai da jin wani mashi ya caki zuciyata tamkar ma zuciyar tawa ce na yanka.
Mu uku muka cinye cake ɗin duka,kafin Zuly ta ja ni mu koma can gidanta.....

Ga masu son fara yin payment 500 via 2670215530
ZULFAU YAHAYA
Ecobank DM +22795045822
[23/05 11:29] MRS SADAUKI: *BAƘIN RUHI*🧌🐲

```LoVe aNd HoRrOr story```👽

By
Chamsiya Laouali Rabo
{MRS SADAUKI💫✍️}

*SADAUKARWA :* Ga dukkan iyayenmu MATA da suka tsaya tsayin daka don bamu kariya a kan dukkan wani da ke son cutar da mu.

*FCWA*☀️

---

06

Da muka isa gidanta dakyar na samu na yi sallar isha'i,ita kuwa magrib kamar yadda lokacinta
```

ya wuce to haka ta wuce ni don ba zan ranka ta ba.
Gida nake son tafiya,amma da dukkan alamu ba zan samu wannan alfarmar ba.Haka na yi shuru cikin ɗaki ina tunani iri-iri da kuma mamakin yadda Zulaihat ta koma muguwar sheɗaniyar marar imani.Na goge hawaye masu ɗumi da suka zubo min lokacin da tunanin yadda na ga iyayena suna farin ciki ya faɗo a kwanyata.

“Luby sai fa in kin so ne za ki damu,kamar yadda oga ya faɗa miki mu family sam ba mu da wata matsala.Kin ga fa babu wani abu da za a nema wurinki in kika cire lokacinki,ni ban ga abin damuwa ba a aikin da babu kashe mutane ciki sannan ko jinin ɗan tsako ba mu buƙata”

A lokacin da ta yi min wannan magana sai kuma na ga fa kusan tana da gaskiya,duk da cewa su ɗin matsafa ne amma dai fa ba su kashe mutane.Amma abin da ya fi bani mamaki bai fi ta yadda suke son abubuwan shirme ba,cikin son sanin dalilin haka na jefo mata tambayar “Amma Zulaihat me za ku yi da kashin mutane?”

“Don Allah ki bar ce min Zulaihat ɗin nan,ki kira ni da Zuly sannan maganar me za mu yi da kashin mutane ke ce a ba ki san amfaninsa ba shi yasa amma da shine ai ake yin takin zamani ana kaiwa gona don yin noma”

Na ja ajiyar zuciya da yake ni sokuwa ce sai na yarda da maganarta,kuma in faɗa muku gaskiya sosai kalamanta suka yi tasiri a raina don sai na ji na kuma yarda zan yi aiki da su.Ban taɓa sanin illa ne ba sai da na haɗu da ke Haule na ga irin abubuwan da kike yi na ban mamaki.

Jin na samu ƴar nutsuwar ruhi sai na je na yi wanka da ruwa masu ɗumi,da na fito na sha salade na fruit sai kuma a lokacin ne Zuly ta bani wayata wacce take sabuwa dal.Wani irin daɗi na ji ganin ta canza min waya amma layina ne a ciki,ta yi wani murmushi tare da zama kusa da ni ta ce “kwaɗayin na gan ki cikin daula yasa na kawo ki cikin family,dubi yadda jikinki yayi kyau cikin ƙanƙanen lokaci ”

Na ɗan yi murmushin farin ciki kafin na ce “ni dai ki koya min yadda ake aiki da ita” ta yi ƴar dariya kafin ta soma nuna min,muna yi muna taɓa hirar makaranta da kuma ƙawayenmu wanda muka yi aji guda.Duk wani wanda nake da labarinsa sai na faɗawa Zuly aikin da ya samu ko kuma halin da yake ciki.Ban taɓa tunanin cewa rahoto ne take haɗawa ba don farmakarsu sai a ranar da ni ma tawa mission ɗin ta zo,zan faɗa muku yadda komai ya wakana sannu-sannu.

A daren nan sosai muka jima muna hira kafin duk mu kwanta, washegari Zuly ce ta tashe ni sai kuma ta hana ni na yi wanka sallah kawai na yi na saka kayana waɗanda na fito da su daga gida sai jakata.

Fita muka yi muka shiga mota ta kai ni asibiti da tambaya muka samu ɗakin da su Ummah suke.
Ina ganinta na je na rungume ta ina tambayar jikin Abba wanda ke bacci.
“Da sauƙi sosai yanzu likita ya shigo ya duba shi tare da yi masa allura,ya aikin Lubna? wannan fa?” Ummah ta faɗa tana nuna min Zuly .

“Ah na manta ban gabatar miki da ita ba,Zulahait abokiyar aikina ce” na bata amsa.

Umma ta ɗan yi murmushi kafin ta ce “ma sha Allah! Allah ya taimaka ya baku sa'a ya kuma baku cimma nasarar aikinku,ki ƙara yi wa oganku godiya don Allah Lubna .Mutum mai kirki jiya bai bar wurin nan ba har sai da ya ga an shiga an kuma fito da Abbanki”

Wani irin sanyi ya ratsa ni jin wani abin farin ciki,na so in zauna da iyayena amma Zuly ta ƙi bani damar yin haka ta hanyar cewa “ki dai tashi mu je gida ki yi wanka ki canza kaya sai ki dawo ko?”

Da wannan tasa ta ci galaba kaina muka fito,“Zuly mene ne haka? Na ga kamar ba ki son na zauna tare da iyayena” na faɗa ina kafe ta da ido.

Ta ce “ke ba fa komai ne ba,ina so dai ki yi wanka ki canza kaya ko kin ji  sanyi”

“Amma daga nan fa?”
“Za mu wuce kamfani” ta bani amsa.Kafin mu shiga mota mu koma can gidanta,da isarmu kuwa wankan na shiga bayan na fito na shirya cikin ɗaya daga cikin abayar da muka siyo jiya.Ina tsaka da fesa turare ta shigo sanye cikin kayan atamfa har da luluɓa uban mayafi kamar ta ƙwarai,ina shirin yi mata tambayar ya na ga ta yi shiga ta kamala daga can falo na ji muryar wani gardi yana kiran sunanta cikin tsawa “Zulaihat?” murya na rawa ta amsa kafin ta kama hannuna ta ce “in ya tambaye ki wace ce ke sai ki ce ƴar uwata ce ke kun zo nan ne domin jinyar mahaifinki” ba ta bani damar cewa komai ba kuma ta ja ni muka fita can falo.

Yadda duk ta nutsu cike da tsoro yasa ni ma na kama kaina tare da gaishe shi cike da ladabi,dakyar ya amsa kafin ya ce “wace ce ke?”

Sai da na saci kallon Zuly kafin na ce “ƴar uwarta ce,jiya muka zo nan garin domin jinyar mahaifina da ke asibiti”

“Ita kuma ta ce min yau ne kika zo”

“Eh nan gidan ba,amma ai tun jiya muka zo ni da iyayena suna can asibiti”

“Wace asibiti?”

“Private asibitin nan da ke kusa da babbar kasuwa” na basa amsa,bai ƙara cewa komai ba sai ya je ya zauna kan kujera yayin da ita kuma Zuly ta je jikinta na ɗan rawa ta fara zuba masa abinci tana gamawa ta zo ta kama hannuna tare da jana muka koma can ɗakina.Bayan ta rufe ƙofa sai ta ja ajiyar zuciya,ni kuma na ce “wane ne kuma wannan?”

Cikin ƙasa da murya ta ce “mijina ne,ki bari daga baya zan yi miki bayani” tana gama faɗar haka sai ta fice ta bar ni sake da baki ina mamakin kenan Zuly tana da aure amma ta rasa wanda za ta aura sai babban mutum kuma irin mai zafin kai.

Bakin bed na zauna ina tunanin ni ma ai lokaci yayi da zan bai wa maza dama ,saboda can baya gani nake in ba aiki na samu ba to fa ba zan taɓa kula namiji ba.
Tsawon lokaci ina wasiƙar jaki kafin Zuly ta shigo ,“ taso mu ci abinci” ta faɗa .Tashin na yi na mara mata baya,ita ce ta zuba mana sai da muka fara ci sannan ta soma bani labarinta.

“Lubna kamar yadda kika sani ba duk abin da mutum yake so yake samu ba,to ni ma hakan ce ta faru da ni.Bayan mun kammala karatu na fara neman aiki ,duk inda na je babu nasara sai na samowa kaina mafita wato ita ce ta auren miji mai kuɗi shine fa na auri Alhaji ” tana kawowa nan ta yi shuru ban matsa mata da sai ta ƙara cewa wani abu ba lura da yadda take bani labarin a takure.Bayan mun gama cin abinci daga nan kuma kamfani muka wuce,kafin nan bisa hanya sai da ta ƙara gutsura min labarin nata.

“Akwai wani group mai suna sugar Daddy ,a can muka haɗu da Alhaji ta hanyar wata ƙawata na samun link ɗin.Tun da na tura hotona na gabatar da kaina ya biyo ni pc ya ce na yi masa ban kuma ja aji ba muka fara soyayya kar ki so ki ga yadda yake yi min batal ɗin kuɗi.Ba a ɗauki lokaci ba kuma ya zo gidanmu suka yi magana da iyayena waɗanda kafin auren sai da suka tambaye ni ai dai ina sonsa ko ? Na kuwa ce eh.Amma a zahiri ba haka abin yake ba,kawai saboda in samu gidan hutu ne yasa na amince da aurensa.Muna yin aure hannunsa ya koma na jariri hahaha! Ya bar bani kuɗi sai dai fa duk abin buƙata yana zuba min su a store kuma bai damu ba don na ɗiba na yi kyauta  da su,ana haka sai na fara haɗuwa da manyan mata .In an je biki su yi ta liƙen kuɗi,wata don ta ɓarar da 200k ba wani abu ba ne ,to abin sai ya fara damuna har na soma tunanin ko rabuwa zan yi da Alhaji .Da na kai wa waccan ƙawata da ta bani link kokena sai ta haɗa ni da oga” tana kawo wa nan da labarin ta yi parking duk muka fito,duk da a lokacin na so jin yadda ta kaya amma na yi shiru muka shiga ciki.

Cike da girmamawa aka dinga gaishe ta,direct kuma ofis ɗin oga muka wuce.Yana ganinmu yayi saurin tasowa ya shayar da ni giyar mamaki don kuwa rungume Zuly yayi ƙyam a ƙirjinsa tare da feso wasu kalamai waɗanda suka sa na zauna ban shirya ba.

“Ya haka Baby? Na ji an ce mijinki yau yayi saukar asubah,shine ba ki faɗa min ba.Me ya kawo haka ko yayi miki wani abu ne?”

Ita kuwa ƙoƙarin fizge wa take,tana satar kallona da sauri na kawar da kai.
Ina jin lokacin da oga ke ci gaba da cewa “faɗa min kun yi wani abu da shi ne?”

“A'a ! Please ka sake ni mana ” ta faɗa.

“Luby ki ɗan fita ina son yin magana da Oga” ko kallonsu ban ƙara yi ba na fita,direct kuma ofis ɗinta na shiga wanda ke kusan na oga.Kaina na ji yana sara min a fili nake tambayar kaina “wai da aurenta take kula wani? Da aurenta take zina? Innalillahi wa'inna ileyhi raji'un! Ya Rabb ka tsare ni daga sharrin zina Allah kar ka jarabce ni da ita,kar ka kuma nuna min ranar da zan yi ta Ya Rabb kafin ranar nan ta zo Allah ka aiko tirela ta markaɗe ni na huta” haka kawai na ji hankalina ya ƙi kwanciya da wannan aikin,sai nake jin kamar na je na shaida musu ban so.

Bayan wajen minti talatin ina zaune sai ga Zuly ta shigo ,kallo ɗaya na yi mata na ɗauke kai. Ta zauna tare da soma magana ba tare da na tambaye ta ba,“sai haƙuri Luby,ni ma na fara gajiya sai dai ba a komawa baya.Kin ga a ranar da ƙawata ta haɗa ni da oga da farko iya aikin yi masa lissafi kawai ne nawa,amma sannu-sannu sai ya fara bijiro min da ainahin zuwan nawa.Cike da tako yayi nasarar kai ni kan shimfiɗarsa har sai bayan komai ya kammala ne na fahimci kuskurena,don da soyayya ya ɓullo min .Amma yana bani kuɗaɗe masu mugun yawa sai ya girgiza tunanina,sai kawai na biye masa kusan kullum in na zo aiki muna keɓewa yayin da shi kuma yake cika min jakata da ƴaƴan banki”

“Ita kuma alaƙar tsafi?” na jefo mata tambayar.
“Shi ne ya bani power ya kuma nuna min yadda ake yin komai”
“To amma me yasa ba ki rabuwa da Alhaji ki auri oga ? Ai hakan ya fi nake gani tunda da dukkan alamu shi oga kina sonsa”

Wani kallo ta yi min kafin ta ce “ki shirya za mu fita zuwa yawon ƙauyukan da za a soma aiki”

“Aikin me fa?”

“Na gina banɗakunan kan titi mana” ta bani amsa.

Ko da muka fito tuni motar da za ta yi yawo da mu ta zo,haka muka shiga mu da wasu sauran ma'aikata.Yawo sosai muka yi muna duba wuraren da za a gina banɗakuna,wasu cikin kasuwa wasu kuma kan titi.Sai bayan sallar azahar muka dawo,Zuly ce ta yi wa oga bayanin komai kafin ta sauke ni asibiti.
Ina shiga daidai nan Abba ya rufe idonsa ya soma bacci,bayan na gaishe da Ummah sai na zauna na tambaye ta jikinsa ta amsa ana ta samun ci gaba.

Nan na wuni,har dare amma Abba bai tashi ba har ƙikitocin sai da suka yi mamakin irin baccin nan da yake alhalin ba a yi masa allura ko magani mai sa haka ba.Saƙon Zuly na samu kan ina iya tafiya gidanmu ba sai na je can gidanta ba,da wannan na yi wa su Ummah sallama na je can gidan.A daren ne kuma na yi wani mafarki mai matuƙar firgitarwa,ga Abba nan yana kuka yana kiran sunana yayin da kuma wasu mutane masu baƙaƙen kaya sun ɗora shi kan garwashin wuta suna gasa shi tamkar wani tsire.

A firgice na farka wanda yayi daidai da kiran Zuly,"ki fito ina ƙofar gidanku" shine abin da ta faɗa min ta kashe wayar.

Cike da mamaki na duba lokaci,ƙarfe biyun dare ne.Amma haka na fita na same ta cikin mota,ina shiga ta fizge ta kuwa ta soma yin gudu kamar za ta tashi sama tambayar duniya kuma ta ƙi bani amsar abin da ke faruwa .
Gidanta muka wuce,tana yin parking duk muka fito hankali tashe take jan hannuna zuwa ciki.Wannan dai ɗakin muka shiga wanda na yi laƙabi da ɗakin sirrinta,ko da muka shiga sai ta buɗe madubinta ta tsaga yatsanta jini ya soma zuba ta kamo nawa da niyyar tsaga shi kenan mijinta Alhaji ya shigo ɗakin yana salati tare da jefo mata tambaya "Zulaihat tsafi cikin gidana? Dama ke MATSAFIYA (Mrs SADAUKI) ce ban sani ba? Ai kuwa yau..." bai ƙarasa kai ƙarshen maganarsa ba Zuly ta jefa wuƙar hannunta tare da furta furucin tsafi nan take wuƙar ta sauka daidai tsakiyar ƙirjin Alhaji a nan take ya faɗi jini na yi masa malala......

My book is only 500 via 2670215530
ZULFAU YAHAYA
Ecobank DM +22795045822
[23/05 11:29] MRS SADAUKI: *BAƘIN RUHI*🧌🐲

```LoVe aNd HoRrOr story```👽

By
Chamsiya Laouali Rabo
{MRS SADAUKI💫✍️}

*SADAUKARWA :* Ga dukkan iyayenmu MATA da suka tsaya tsayin daka don bamu kariya a kan dukkan wani da ke son cutar da mu.

*FCWA*☀️
```

07

Ban taɓa shiga tashin hankali irin na yau ba,kisan kai ne aka yi a gabana ga gawa kwance cikin jini.Tsabar ruɗewa da na yi yasa na soma zagayen ɗakin ina ihu,yayin da ita kuma Zuly ta soma tsafe gawar tana barbaɗa mata wata hodar tsafi kafin ƙyaftawar ido gawar ta ɓata ko kumfan jini babu,a wannan lokacin ne na ƙara ganin bala'in da na tsoma kaina a cikinsa.Zuly ta nufo ni da niyyar kama ni amma na yi tsalle na koma can gefe ,idonta ta juye tamkar wata zakanya kafin ta soma yi min magana cikin wata irin murya “Luby ki zo mu wuce ba mu da sauran lokaci,in kuma kika jinkirta duk abin da ya biyo baya babu ruwana”

Ina kuka ina ƙari na ce “amma Zuly kisan kai fa kika yi,mutum ne fa kika kashe kuma mijinki”

“Babu ruwanki da wannan matsalar ki zo mu wuce” ta yi furucin tare da yin tsalle ta zo ta cabko ni muka tashi cikin iska kafin mu ratsa ƙofar da ke cikin mirror.

A wani ɗaki muka bayyana,da na duba da kyau sai na ga wancan dai ne na ƙasar waje.Duk yadda na so na bijiro da zancen kisan kan da ta yi ta hana,a gaggauce ta tirsasa ni na shirya cikin kayan arna kafin mu fito.Yanzu ma buɗe mana mota aka yi muka shiga ,muna tafe ina duban hanya sai na ga wata ce aka ɗauka ba waccan ba.Mun yi tafiya mai ɗan nisa kafin mu isa, wannan karon a tare muka shiga ɗakin taron mai ɗauke da ɗumbin jama'a daga ƙasashe daban-daban.Ciki kuwa har da oga shi ma ya haɗe cikin wasu baƙaƙen suit kamar sauran mazan,wuri muka samu muka zauna oga ya dubo inda muke zaune fuskarsa ta nuna alamun damuwa.

Can kamar minti biyu wani zabaya ya fito sanye cikin jajayen kaya kansa ya ɗora wata hulla kamar ta sheɗan,gashin kansa da idonsa duk wasu iri ne kamar wani makaho haka ya ƙanƙance su yana ƙarewa kowa kallo ,da ya zo kaina sai ya tsayar da dubansa gare ni.Gabana ne yayi wani irin mugun faɗuwa ,so nake na kauce idona amma tamkar wacce aka yi wa dabaibaye na kasa.

“Mansoor fatan ka yi wa ɗalibarka bayani?” shi ne abin da ya faɗa .

Muryar oga na ɗan rawa ya ce “a'a tukuna dai Boss ”

Bai ce komai ba sai ya zauna kan kujerar ya soma yin wasu maganganu da ban gane su ba saboda kogin tunani da na abka,ban farga ba sai da na ji Zuly ta zungure ni sai na dawo hayyacina nan  kuma na ƙara jin wani zancen banza wanda kuwa hankalina ya kasa ɗauka.

Oga ne ke bayani kamar haka "Luby a family muna da wata ƙa'ida,babu virgine a tsarin tafiyarmu in ma ta shigo to dole a yi amfani da ita don kawar da budurcinta.In irin wannan damar ta samu to Boss ne yake yin wannan aiki ,kamar yadda tsarin yake zai yi amfani da ke a gaban dukkan family bayan nan kuma sai ki karɓi zoben ƙarfin iko da kuma madubinki wanda zai sauƙaƙa miki yin balaguro zuwa ƙasashen duniya da kuma in an tsara meeting"

Wata irin bazawarar dariya na yi,don abin jin shi na yi kamar wasar kwaikwayo sai na miƙe tsaye kamar mahaukaciya ina mai ci gaba da yin dariya kafin na ce "wato na basa budurcina? Akan wane dalili kenan? To ba zan yi ba,sai dai ku cire ni daga cikin family ɗin amma ba zan taɓa aikata zina ba"

Da wani mugun sauri oga ya zagayo ya zo inda nake ya kama kafaɗuna ya ce " Luby wannan dolenki ne! Kin ga ki ajiye hankalinki babu fa wata matsala sau ɗaya tak ne zai yi shi kenan "

Hawaye suka zubo min masu ɗumi,ji nake kamar na shaƙe wuyan oga har sai ya mutu na sake shi .

"Na bata nan da sati ɗaya,ta je ta yi shawara don ina da ayyuka masu muhimmanci a gabana kowa zai iya tafiya" Boss ya faɗa tare da miƙewa ya koma hanyar da ya fito.
Nan kowa duk ya watse,Zuly ta kama hannuna muka fito muka bar oga can.Har muka isa gida tana yi min nasiha haɗi da shawarwarin banza wanda in sun shiga kunnena sai su fita ta ɗayan kunnen,sam ban ji zan iya yin abin da suka ce ba.

Na yi tunanin da zarar mun je za mu koma can Kamaru ne,amma sai na ji wata sabuwa wai zan sake yin wani zama da mutanen da na tallata musu hajarmu.

Cikin bahon wanka na shiga na lumshe ido,tunanin iyayena da kuma abubuwan da suka faru suke ta min yawo a kwanya.Har sai da ruwan suka huce na zuba wasu sannan na yi wanka na fito,cikin kayan bacci na shirya sannan na kwanta sai dai fa na kasa yin baccin haka na yi ta yin juyi bisa gado.Can sai ga Zuly ta shigo hannunta riƙe da ƙaramin tray ,tashi na yi zaune ita ma ta zauna bakin gado tare da miƙo min kofi ɗaya na madara ita ma ta fara shan guda.

"Wacce shawara kika yanke ?" ta jefo min tambayar.

"Game da me fa?" ni ma na tambaye ta.

Da ɗan mamaki ta dube ni kafin ta ce,"maganar Boss ɗin ce kika manta?"

"Shi wane ne?" ban ida rufe bakina ba kofin da ke riƙe da hannuna ya tarwatse har sai da

kwalba ta shige min hannu nan take jini ya soma zuba.
Jikin Zuly ya ɗauki rawa,sai ta dubi madubin da ke a ɗakin kafin kuma ta taimaka min ta tsayar da jinin ta naɗe min shi da bandeji.

Sosai na tsorata ban taɓa tunanin Boss nada power har haka ba,don babu tantama shi ne ya tarwatsa kofin.A tsorace nake kallon Zuly kafin na ce “don Allah ki mayar da ni gida”

Muryar Boss ta fito ɓaro-ɓaro ta cika ɗakin “duk inda za ki je ba za ki taɓa boyewa ganina ba,na soma bibiyarki kenan”

Da sauri na rungume Zuly ,sai aka ƙwanƙwasa ƙofa ita ce ta bada damar shigowa.Ƴar aiki ce,cikin Yaren turanci ta ce “oga na falo yana jiran ku ” tana gama faɗa ta fice.

After dress na ɗauko na ɗora a sama kafin mu fita falon,Oga na zaune ya hakimce fuskar nan kicin-cikin kamar za ta tsage.
Na sunne kai tare da samun wuri na ja na tsaya ganin irin mugun kallon da yake jefo min.

“Zuly kin ga saboda ke ina shirin samun matsala da Boss ? Ta ya za ki kawo wacce kika san za ta kawo mana cikas? Faɗa min wace shawara kuka yanke yanzu?”

“So take mu koma Kamaru,kuma ni ma na ga kamar hakan zai fi.In mun je can za ta fi samun damar yin tunani in tana ganin Abbanta ” Zuly ta faɗa ,ban san dalilin da yasa ta kawo Abbana a cikin wannan lamari ba.

Oga ya ce “babu matsala za ku iya komawa,amma ki bari har zuwa gobe don yanzu haka an tsinci gawar mijinki ƴan sanda sun soma yin bincike.Kin ga in suka biyo ta kanki za su samu ba ki ma ƙasar,kuma in kin je ki nuna cewa labarin mutuwar ne ya maido da ke”

“Kenan in haka ne sai dai mu bi jirgi ba ta madubi ba?” Zulyn ta faɗa sam babu wata damuwa a tattare da ita.

Oga ya miƙe tsaye ya ce “eh hakan za a yi,na riga da na tsara komai” yana gama faɗa ya murza zobensa nan take ya ɓace ɓat.

A ɗakin Zuly na kwana, washegari kuma tun da safe muka shirya tsaf zuwa aeroport,jirgi ne na musamman wanda bai da buƙatar sai mun nuna wasu takardu.Tamkar zan fita daga wuta haka nake ji,don na lashi takobin da zarar mun sauka Kamaru ko ƙasa da sama za su haɗe ba zan ƙara shiga sabgar Zuly ba na fita daga family kenan.

Jirginmu na sauka ƴan sanda suka tarbe mu,nan na ga ikon Allah yadda Zuly ke kuka idonta duk sun yi ja sai wani rangaji take kamar za ta faɗi sai na taro ta .Daga nan police station muka wuce aka yi mata tambayoyi kafin ta nemi tana son ganin gawar mijinta.

Duk yadda ta so mu je tare zillewa na yi na tafi can asibiti,a zaune na tarar da Ummah tana kuka.Tana ganina ta taso ta ce "ina kika shiga tun jiya muna nemanki a waya ba mu samu ba? Auta kuma ta ce min kuna kwance tsakar dare kika fita kika bar gidan,ina ne kika je?"

"Wurin aiki mana Ummah,amma ai gani na zo.Ya jikin Abba?"

Hawaye ta goge da mayafinta kafin ta ce "ɗazun nan aka kawo masa kwara-kwara wacce zai dinga yin tafiya kawai sai kwacaaa na ji ya faɗi.Likitoci sun ce aikin da aka yi masa a ƙafa ya lalace sannan ya samu shanyewar ɓarin jikiii " ta fashe da wani kuka mai tsuma rai ,nan take jikina ya ɗau rawa.Ban ida rikicewa ba sai da na je na ga yadda Abba ya koma ,kukan ni ma na dinga taya Ummah ga likitoci sai rubuta sabbin magani suke.

Cikin wuni guda suka rikita mana lissafi don kuwa an kai gaɓar da kuɗin hannun Ummah sun ida dama oga ne ya bata su.
Wuraren sallar magarib kuma babban likitan ya fito da wani zance,"kuɗin gadonku sun ida ku je ku zuba wasu kafin nan da ƙarfe goma na dare "

Ummah ta dube ni ta ce " Lubna ki je ki biya,ko har yanzu ba a baki ko dala ba sai aikin?" a cikin kalamanta sai nake jin kamar har da ɓacin rai,wato gani take na ɓoye kuɗin ne musamman suturar da ke jikina da ke tsadadiya babu wanda zai yarda kan cewa banda kuɗi.

"Bari na je na dawo" shi ne kawai abin da na faɗa kafin na fito,tafiyar ƙasa na soma yi ina tafe ina tunani har na isa gidan Zuly .A falo na tarar da ita,muka gaisa sama-sama kafin na shiga ɗaki na ɗauko wayata iphone wacce zuciyata da ruhina suka yarda da na sayar da ita na yi wa Abbana magani.

Har na kai bakin ƙofar fita na ji muryar Zuly na cewa"kina tunanin kuɗin sayen magani su ne za su warkar da mahaifinki? To in dai haka ne kin makaro "

Da sauri na juya ina kallonta,ta sakar min wani murmushi tana mai kankare akaifarta.
"Me kike nufi a nan?" na samu dakyar na tambaye ta zuciyata na ɗan dokawa.

Ta miƙe tare da zuwa dab da ni sannan ta ce "ina nufin ko duniya za ku yawace babu asibitin da za ta iya warkar da cutar mahaifinki,ke ce maganinsa in kina so ya warke dole ki bai wa Boss haɗin kai" tana gama faɗa ta bar ni nan tsaye.Na jima cikin shock kafin na fice,wajen wani mai sayar da wayoyi na je na karɓi kuɗi tare da bar masa wayata jingina.
Ko da na isa asibiti na tarar ana yi wa Ummah tijara,haka dai na biya kuɗin gado da kuma na

sauran maganin da ba a siya ba.

Na yi tunanin na kawo ƙarshen matsalar duk da kuwa furucin Zuly bai bar kwanyata ba,ashe nan duk shimfiɗa ce aka yi min mamakin na gaba.
Ƙanwata auta ita ce ta kawo mana abincin dare mun ɗan taɓa hira kafin ta koma gida ni kuma na yanke shawara zan zauna tare da Ummah.

Dare ya tsala bayan duk kowa ya kwanta,na ji motsin buɗe ƙofa wanda yayi daidai da farkawata daga bacci sai dai tamkar gawa haka na sandare na kasa motsi.A gabana oga da Zuly suka shigo ɗakin suka yi tsaye kai ga Abba,can kuma Boss ya bayyana su biyu suka danne Abba yayin da shi kuma yayi masa wata allura wacce ta sa shi soma yin ihu da kururuwa yana kiran zai mutu su tausaya masa su bar cutar da shi,cikin ɗacin rai Boss ya ce “ƴarka ce duk ta ja maka masifa ba za mu taɓa barinka ƙalau ba sai ranar da ta amince da ƙudirina”

Ina jin lokacin da Abba ya soma magana cikin azaba,“Lubnata ba za ta taɓa aikata abin da kuke so ba,na gwammaci na dawwama cikin wannan masifar kan na ga ta gurɓata rayuwart...” Zuly ce ta ɗauke Abbana da wani mari wanda hakan yasa sauran maganar ta maƙale masa,suna gamawa suka fice sai kuma a lokacin kawai jijiyoyin jikina suka ci gaba da yin aiki.

Dakyar na iya tashi na je na yi tsaye gaban Abba ,idonsa ya zuba min yana kuka.Bakinsa ya juye ba zai iya yin magana ba,amma a haka ina fahimtar abin da yake son sanar da ni.Na faɗa jikinsa na saki wani irin kuka mai cin rai wanda yayi sanadiyar tashin Ummah ita ma sai ta soma yin kukan don ta yi tunanin mutuwa yayi.

Sai da likitoci ne suka shigo suka tabbatar mata da ransa,allura bacci suka yi masa saboda wani irin abu da ya soma yi kamar mai cutar hauka.

Jikin Ummah na je na ƙanƙame ta ina mai ci gaba da yin kuka yayin da ita kuma ta soma rarrashina tare da kwantar min da hankali Abba zai samu lafiya.

Da gari yayi haske suka sake shigowa suka duba Abba,suka ce jikinsa ya ƙara mutuwa da buƙatar a yi masa gashin ƙashi .Haka suka tura gadonsa aka shiga da shi wani ɗaki,ni da Ummah iya bakin ƙofa kawai muka tsaya.Daga nan muna jin yadda Abba ke ƙwallowa yana ihu da ransa.

Sosai kururuwarsa ke taɓa min zuciya ,sai nake ganin duk laifina ne.A haka dai na fita don zuwa mu yi cinikin wayata da na baro jiya,nan ɗin ma wata masifar na tarar shagon wayoyi ya ƙone ƙurmus sai gawawarkin wayoyin ga su nan jere ringis duk sun ƙone.Yana ganina ya ƙara ƙaimin kuka,ni ce na basa haƙuri don da ace ya san ta dalilina ne yayi asarar nan ƙila kotu ce za ta raba mu.

Idona sun rufe,babu komai cikinsu sai ɓacin rai.Gidan Zuly na nufa don so nake a yita ta ƙare,ko da na isa na tarar da ita a zaune tana karɓar ta'aziyar mijinta ga mutane duk sun cika falon.Ɗakin da aka ware domin ni na shiga bayan na yi mata alama da ido ina son ganinta,sai dai ina shiga na tarar da Boss a hakimce kan gado yana murmushi...

My book is only 500 via 2670215530
ZULFAU YAHAYA
Ecobank
DM +22795045822
[23/05 11:29] MRS SADAUKI: *BAƘIN RUHI*🧌🐲

```LoVe aNd HoRrOr story```👽

By
Chamsiya Laouali Rabo
{MRS SADAUKI💫✍️}

*SADAUKARWA :* Ga dukkan iyayenmu MATA da suka tsaya tsayin daka don bamu kariya a kan dukkan wani da ke son cutar da mu.

*FCWA*☀️

---

08

A lokacin da na ga Boss kwance kan bed sam babu sutura a jikinsa,wani irin bugawa zuciyata ta yi sai dai na kasa ɗaga ƙafata ballantana na koma baya na fita daga ɗakin.

Cike da shaƙiyanci yake cewa "ki gama gujegujenki ni ɗin nan ne zan raba ki da budurcinki,in kuma kin fi ƙaunarsa kan mahaifinki ai shi kenan" yana gama faɗar haka ya ɓata kamar walƙiya.Na ja ajiyar zuciya,abin da na fahimta a family su komai nasu ba su yinsa dole sai ta daɗin rai wannan dalilin yasa ko da wasa ba su saka ƙarfi ba wurin baiwa Boss ni ba.

Ina nan tsaye ina saka wasiƙar jaki Zuly ta turo ƙofa ta shigo,kallo ɗaya ta yi min ta ɗauke kai tare da yin gaba.Ni kuma na take mata baya ina mai kiran sunanta,sai da ta cire zumbulen
```

hijabinta sannan ta juyo ta fuskance ni ta ce “Luby ban san wace irin zuciya ce da ke ba marar tausayi,duk halin da Abbanki yake ciki kin kasa haƙura ki bada kai bori ya hau.Me za ki yi da shi budurcin? Ina ce duk don da dai ki kai shi ne gidan mijinki,to ki sani a family ba a auren bare.Duk wanda ko wacce ta shigo babu aure to dole ne ya zaɓi abokin rayuwa cikin ƴan ƙungiya,kuma ina ce ai a gabansu za a yi komai ba za ki samu matsala da mijinki ba tun da ya san komai”

Tamkar mai cutar dundumi haka na ji a lokacin,sai kuma na fahimci ba ƙaramar ƙungiyar asiri ce wannan ba wacce ta ɓoye sirrika masu yawa sai a sannu ne za ka dinga ganinsu suna fitowa. Ban kai ga cewa komai ba Zuly ta ƙara da “kawai ki amince ita ce shawara da zan baki”
Idona wani irin raɗaɗi na ji suna yi min kamar an watsa barkono ciki,maƙoshina ya bushe ƙamas dakyar na iya tattaro yawu na haɗiye kafin na ce “ban gane ba zan iya auren wani ba? Zulaihat wai wannan ɗin duk mene ne? Wane irin dokoki ne wannan? To ki tsaya ki ji in faɗa miki daga yau a yanzu da nake faɗa miki na fita daga family har abada,ku je can ku yi tsafinku kuɗi ne dai to ban so ku riƙe abinku.Kuma wallahi kika yi ƙoƙarin ɓullo min da wani sharri to sai na je har ofishin ƴansanda na shaida musu ke ce kika kashe mijinki” ina gama faɗar haka ban tsaya ɓata wani lokacina ba na fita na bar ta cike da shock.

Duk a tunanina shikenan na huta na jefar da ɗan mangoro na huta da ƙuda sai dai ina isa asibiti na tarar da tashin hankalin da ban taɓa zato ba.
Jikin Abba ya rikice sai aman jini yake dunƙule-dunƙule,likitoci sun duƙufa wajen bincike amma result bai nuna alamun wata cuta ba ga jinin Abba sai ƙasa yake yi ga shi banda kuɗi,jinin kuma sai an saya.

Duk da yana cikin firgici da gushewar hankali bai hana shi isar min saƙon kar na saki na bayar da mutumcina ba.Banda kuka babu abin da nake yi,ji nake kamar na je na cewa Zuly na amince sai dai fa duk shaƙiyancina na tsani zina ban ƙaunarta ko kaɗan.Ko da ace saurayina ne wanda nake so ban ji zan iya basa kaina ba ballantana sindiƙin ƙato mashuriki matsafi.

A lokacin da zuciyata ta yi rauni sosai,shine ganin yadda jini ya soma yi wa Abba zuba ta hanci da kuma ido daga ƙarshe yayi shaƙuwa shikenan ashe ta fitar rai ce.Wuaren ƙarfe bakwai ne na yamma likito suka tabbatar mana da hakan,tsabar tashin hankali yasa na suma aka bani gado.Ban san abubuwan da suka faru ba sai a washegari na farka tuni kuma an kawar da gawar Abba an kai shi mankwancinsa na gaskiya.Sai a lokacin na yi kukan mutuwarsa kamar raina zai fita,kafin a sallame ni daga asibiti Allah ya ƙulla alaƙa tsakanina da wani Dr David shine ma ya ɗauki nauyin biyan kuɗin maganina har na ji ɗan sauki.

Bayan na koma gida ma haka yake zuwa yana kula da ni,kusan ma in ce shi ya ɗauki nauyin gidanmu tun da babu wanda ya tallafa mana daga dangi.

Cikin abin da bai wuce wata ɗaya ba wata irin shaƙuwa ta shiga tsakanina da Dr David ,sonsa ya samu matsuguni a zuciyata duk da hankalina bai kwanta ba saboda shirun da Zuly ta yi sam ban yarda da shi ba,don na sha jin yadda ƴan ƙungiyar asiri ke da mugun naci.Ashe kuwa ban saɓa lamba ba,a wani yammacin Laraba mun ajiye magana Dr David zai zo ya ɗauke ni mu je gaishe da mahaifiyarsa .Mun yi waya da shi kenan ya shaida min ya ga shi nan zuwa,bayan kamar mitin goma aka kira ni aka shaida min yayi hatsari yana can asibiti .
Cike da tashin hankali na fita ko Ummah ban shaida ma ba,ina fitowa nan cikin layinmu wani mai mashin ya kaɗe ni sai da na yi sama na faɗo duk kayan jikina suka ɓace da ruwan dauɗa,dole na koma gida na yi wanka ina ƙoƙarin sake fita kuma ita ma Ummah ta soma nata ciwon abu kamar wasa sai ga mu har da zuwa asibiti.

Bayan mun dawo gida na yi ta gwada kiran Dr David amma layin bai shiga,amma ban haƙura ba a cikin haka na samu ya shiga sai dai ba shi ne ya ɗaga ba mahaifiyarsa ce wacce nan take ta hau ni da masifa akan na rabu da ɗanta kar abin da nake ciki ya shafi ɗanta na je can na ƙarata da matsalata.To a nan ne fa na gane zama bai same ni ba,sam kasa bacci na yi .Tsakar dare kuma ciwon Ummah ya ƙara tashi ta soma numfashi kamar za ta mutu,a lokacin tuni na soma yin kuka na ɗauki wayata tsabar ruɗewa wai da Dr David zan kira nan ne na ci karo da saƙon Zuly tana yi min hannunka mai sanda tare da barazanar cewa in ban yarda na dawo bakin aiki ba to zan rasa Ummah tamkar yadda Abba ya tafi.

Ina matuƙar son Ummana wannan yasa na aika mata saƙon zan koma a gobe,hum in faɗa muku wani abin mamaki kamar cirar ƙaya haka Ummah ta warke ta samu bacci.Sai na ji na ɗan samu nutsuwa,ni kam ban yi bacci ba har sai da na yi sallar asuba wacce zuwa yanzu ina yin sallolina.

Sai wuraren ƙarfe tara na farka,na yi wanka na shirya sai kuma na shaidawa Ummah zan koma a bakin aikina.
“Ni kam Lubna tun da Abbanku ya rasu ban ga wani daga cikin ƴan wurin aikinku ya zo ba,har shi ogan naki” shine abin da Ummah ta ce.

Na ce “kin san na rasa wayata,kuma oga ba ya ƙasar ita kuma Zulaihat faɗa muka yi lokacin da na ce ta ara min kuɗi ta ƙiya ƙila shi yasa ba ta zo ba ko kuma ba ta samu labari ba”

“To Allah kyauta,ki je Allah ya tsare ki ya kuma kare ki da sharrin dukkan mai sharri”

Cike da jin daɗin addu'arta na amsa da “amen” kafin na fita.Ina zuwa bakin titi motar Zuly ta parker a gabana,zuciyata cike da ƙunci na je na zagaya na buɗe na zauna ta saki murmushi mai sauti kafin ta ce “barka da safiya” ban amsa ma ta ba har muka isa gidanta na canza kaya muka wuce.

Sosai na yi mamakin yadda aka shirya min tarba ta musamman,har da yi min wankan fure aka yi min kafin kuma na yanka cake aka shiga taɓi.Bayan wannan sai muka wuce ofis ɗin oga ni da

Zuly,bayan mun zauna ne ya soma yin magana “Luby duk da dai ban so kika rasa damarki ta farko ba,amma mun rarrashi Boss kan ya janye wannan dokar duba da yadda kike da ƙoƙarin aiki dakyar ya yarda amma da sharaɗin za ki kawo sperm ɗin wani wanda kika sani mai ilimi”

Na ɗan yi saƙo kafin na ce “a ina kuma zan samu sperm oga?”

Zuly ta yi karaf ta ce “ saurayinki David mana ,ai kin ga yana da ilimi sosai kuma ma ai kin ga ba musulmi ne ba ballantana ki sha wuya wurin shawo kansa”

Shiru kawai na yi,duk da na ga sharaɗin ba wani mai tsauri ne ba amma tabbas na san da haɗari a ƙasa.
“Ko kuwa dai kin fi so a dinga yi wa ahalinki ɗauki ɗaiɗaya suna mutuwa ɗaya bayan ɗaya?” Zuly ta jefo min tambayar da na ji tamkar na shaƙe mata wuya,kuma sai yanzu ma ne raɗaɗin mutuwar Abba ya fi yi min ciwo fiye da can farko.

A hassale na ce “ kar ki yi kuskuren taɓa Ummana don wallahi zan shayar da ke mamaki,kun faɗi sharaɗinku ai sai ku jira in ban yi ba sai ku bijiro min ta nan”

Oga ya ce “ Zuly ke ma ya kike yi mata magana haka? Ki yi haƙuri Luby ki je ki fara shirye-shiryen taron da za ki gabatar yau da dare,Zuly ki bata sanadaran da kuka fitar na taurari”cewar oga kafin ya miƙe ya shiga toilet,ita kuwa jakarta ta zuge ta miƙo min wasu kwalabe biyu ɗaya mai baƙin murfi yayin da ɗayar kuma ke da farin murfi.Na karɓa ina juya su yadda kowacce kwalba ke fitar da bata kalar hasken.

“Baƙin tauraro yana da matuƙar muhimmanci ga waɗanda suka san amfaninsa,shi kuma farin yana ƙara ƙarfin power ne kawai” Zuly ta faɗa kafin ita ma ta tashi ta take wa oga baya.Ba a ɗauki lokaci ba yanayin sautinsu ya fara farmakar kunnena babu shiri na fita na bar ofis ɗin amma sam sautin ya ƙi fita da kwayanta hakan ya haifar min da zuwan wani hatsabibin feeling wanda ya fi kama da na haddasawar sheɗanu.Ido kawai na lumshe tare da ƙanƙame jikina,a inda nake zaune nake a cikin ofis ɗin Zuly nake jin wasu idon sharri na ankare da ni amma da na duba ban ga kowa ba.

Ina zaune cikin wannan hali Zuly ta shigo,jan bakin da ta saka duk babu shi a leɓenta sannan zaman rigarta ma haka.Ba tare da wata damuwa ba ta ce “kafin mu isa Japan ya kamata ki aiwatar da aikinki na kawo sperm ɗin David,ki tabbatar komai ya tafi kan tsari”

“Ta ya za a yi na samu sperm ɗinsa ba tare da mun yi sex ba?”

“Ki yi tunani Luby,yin sex da masoyi ai bai da wata illa ya fi ki yi da wanda ba ki so”

“Ba ki da hankali,sai na je na yi zina? Allah ya tsare ni” na faɗa tare da miƙewa,ina shirin fita wani abun al'ajabi kiran Dr David ya shigo wayata cak na tsaya kafin na juyo na ce “shi ne ke kirana ” sai ta saki murmushi ta ce “ki ɗauka mana”

Kiran na ɗaga,bayan mun gaisa ya tambaye ni yana son mu yi magana amma don Allah ba ta waya ba mu haɗu ko da wani restaurant ne.A ranar nan rabon na rabu da alaƙaƙai ne yasa na yarda da gayyatar Dr David,wani abun mamaki kuma shine a restaurant ɗin Hajiya ne muka haɗu a nan ne na fara ganinki Haule haka kawai na ji kin yi min sai kuma na ga kina yawan kallona a duk lokacin da za ki kai abinci a wani teburin da aka buƙata.A tattare da ke na ga wasu abubuwan na daban sai dai ban san ya zan yi na yi miki magana ba,a nan ne kuma hankalina ya rabu biyu na yadda zan yi na samo sperm ɗin Dr David da kuma na mamakin yadda kike yin abu kamar siddabaru.

Dakyar na iya tattaro jarumtar tunkarar Dr David kan cewa ina son sperme ɗinsa saboda an ce yana gyara fuska,bai wani musa min ba don dama ya kira ni izuwa nan ne don bani haƙuri da kuma neman alfarmar mu koma soyayya.Mun yi da shi zai kawo min sperm ɗin zuwa dare,da wannan muka rabu ya sauke ni gida.Duk yadda muka yi da shi na kwashe na shaidawa Zuly ta yi murna sosai har ta kasa ɓoye farin cikinta,sai kuma na yi mamakin haka amma na ɓoye shi har lokacin da Dr David ya zo ya kawo min abin da na buƙata cikin wata ƴar kwalba.

Bayan na karɓa ya jefo min wata tambayar da ta hautsana hanjin cikina,“Lubna kin tabbata a fuskarki za ki shafa shi?” duk da a lokacin na firgita amma haka na mayar da abin tsokana na ce a'a cikin mahaifata zan ɗura shi don na samo baby mai kama da kai,nan yayi dariya muka taɓa ƴar hira kafin ya tafi.

Yana gusawa motar Zuly ta parker na shiga muka lula can gidanta,cike da zumuɗi take cewa “meeting ɗinki na Japan an ɗaga shi,yau za mu je ɗakin sirrin Boss domin gabatar da sacrifice ɗinki na farko” sam ban fahimci abin da take cewa ba,sannan kuma ban tambaya ba.

Yau ma ta cikin madubinta muka bi muka isa a ɗakin taron,abun mamaki kowa ya haɗu har da shi kansa Boss ɗin wanda idonsa ke jifana da kallon sha'awa.Ba a ɓata lokaci ba muka dugunzuma wani ɗaki mai shegen duhu ,babu abu mai haske ko ɗaya in kuka cire wani mirror .

Cikin wata irin busashiyar murya Boss ya kira sunana,hakan yasa na ɗan matsa ba tare da na amsa ba.Hannu ya miƙo min,na san za ku ce ta yaya na ga haka duk da na ce akwai duhu a ɗakin.To abin shine da zarar mutum ya kai wani lavel yana samun wani ido a tsakiyar goshinsa mai gane masa komai da ido normal ba zai gani ba.

Yana karɓar robar sperm ɗin ya buɗe ta,sannan ya dangwalo da yatsansa ya shiga yin rubutu a jikin madubin *BAƘIN RUHI* shi ne abin da ya rubuta nan take wata irin guguwa da iska mai ƙarfi suka cika ɗakin na yi tunanin duk za su yi murna sai dai fa akasin haka ne ya faru saboda kururuwa da suka soma,kafin ƙyaftawar ido wani jan maciji ya bayyana a mirror ɗin yana feshin wuta kafin kuma madubin ya tarwatse wanda turnuƙin fashewarsa ta haifar min da gushewar hankali ko da na farka a kwance na same ni kan shimfiɗa Ummah na yi min fifita.Ina ware idona sosai nan na yi arba da Alhaji wato Maheer,wani irin mugun kallo ne yake watso min yana

hararena.

Ummah ta ce “kin farka Lubna?” ban amsa ba sai dai na yunƙura zan tashi sai dai na kasa saboda yadda jikina ke yi min mugun ciwo.
“Ki kwanta ki huta” cewar Ummah.
Shi kuwa cike da mugunta ya ce “barta za ta iya tashi,ke miƙe ”

Maganarsa tamkar umarni ne a gare ni,haka na ji ba zan iya yi masa muso ba na miƙe na tashi zaune duk da kuwa uwar azabar da nake ji.Wani magani ya fiddo cikin aljihu ya miƙo min,“komai za ki ci ki dinga zuba wannan a ciki,in kuma kika kuskure daidai ɗaya rana za ki koma hannun waɗanda kika fito”

A lokacin da na ji Ummah na yi masa godiya sai na fahimci tuni ya shaida mata komai,ban yi mamakin yadda aka yi ya san komai ba don na fahimci yana da power.Sannan a cikin coma ɗin da na shiga haka aka yi min wahayin komai ta yadda aka yi ya tarwatsa komai,ashe lokacin da muke yin magana da Dr David Maheer ya shigo restaurant ɗin kuma ya ji abin da nake cewa.Sannan kuma abin da ba ki sani ba Haule sarai Maheer ya san cewa ke ma ba normal mutum ba ce,kamar yadda na dinga kallon abubuwan da kike na siddabaru to shi ma idonsa suna iya ganin duk abin da kike yi” Lubna na kawowa nan da dogon labarinta da take bamu ni da Aliya sai ta yi shiru,ni kuma numfashi na ja kafin na ce “amma ta ya aka yi ni ban san da cewa shi ma yana da power ba sai yau? ”

“Saboda ƙarfinsa ya wuce yadda duk kike tunani,kin ga fa shi ne ya kuɓutar da ni daga komarsu tun lokacin ba su sake waiwayata ba.Haka ita ma Ummah ba ta yi sake kan kula da lamurrana ba kullum cikin yi min addu'o'i take,duk asubah in ta gama sallah kamar wata ƴar baby haka take dafa goshina tana yi min addu'o'i ” cewar Lubna.

Na dubi Aliya wacce duk yanayinta ya canza kafin na ce “ya dai?”

“Babu komai! Amma dai a yadda na fahimta ita ma Lubna ta shiga komar BAƘIN RUHI ne kamar yadda na saba ganin gawarwakin waɗanda suka mutu ta silarsa,su ma jini yana fita ta idonsu”

Furucin Aliya ya tuno min da gawar Haidar,murya na ɗan rawa na ce “Lubna bayan an yi wa mahaifinki wanka shin jinin da ya fita ta idonsa ya wanku?”

Ta ce “wallahi ban sani ba saboda lokacin ai na faɗa muku ban cikin hayyacina kuma ko da na farka tuni an kawar da shi”

Na ce “da buƙatar mu samo amsa,babu kuma wanda zai bamu tabbacin haka sai Ummah.In dai hakan ta kasance to tabbas BAKIN RUHI nada ƙarfi sosai ta yadda ya bazu a duniyar nan to

amma wane ne shi?” na yi tambayar da ni da su babu wanda ya san amsarta.....

My book is only 500 via

2670215530
ZULFAU YAHAYA
Ecobank

DM +22795045822

🔞Don Allah masu zuwa suce min complet suke so ku yi haƙuri Ni ma banda shi,yanzu nake typing in kina so ki biya na saka ki group.
[23/05 11:29] MRS SADAUKI: *BAƘIN RUHI*🧌🐲

```LoVe aNd HoRrOr story```👽

By
Chamsiya Laouali Rabo
{MRS SADAUKI💫✍️}

*SADAUKARWA :* Ga dukkan iyayenmu MATA da suka tsaya tsayin daka don bamu kariya a kan dukkan wani da ke son cutar da mu.

*FCWA*☀️

---

BONUS na book ɗin *BAƘIN RUHI* mai so ya tura 300 kafin na saki last free page 10 gobe in sha Allah ki tura kai tsaye ta wannan account ɗin 2670215530
ZULFAU YAHAYA
ECOBABK sai ki turo min shaidar biya ta WhatsApp +22795045822 .Da zarar na saki last free page discount ɗin ya ƙare.

Masu sha'awar karanta tsofin Books ɗina ku zo na yi muku discount,ga wacce ta shirya ta tuntuɓe Ni kai tsaye ta WhatsApp +22795045822

09
```

Dare yayi sosai wannan yasa muka jingine bayar da labarin,duk da na san akwai abubuwan da Lubna ta ɓoye wanda ba ta faɗa ba amma haka na yi shiru na samu wuri na kwanta.Ido na lumshe nan take Maheer ya bayyana cikin tunanina,zaune yake a ɗakinsa ya sha wata doguwar rigar bacci ta maza fara sol da ita.Gabanta a buɗe yake,hakan ya bani damar ganin fafaɗen ƙirjinsa mai ɗauke da suma baƙa silik ta kwanta sai sheƙi take.Duk da ban taɓa saurayi ba,amma gargasar ƙirji na ɗaya da abin da nake fatan samu a wurin mijin aurena hakan yasa na kafe gurin da ido ko ƙyaftawa ban yi.

Har sai da na ji muryarsa yana cewa ,"kin ga dama kin zo" da wani mugun sauri na buɗe idona sai kuma na tashi zaune na dafe saitin zuciyata da take bugawa,sam na kasa gane shin tunaninsa ne na yi? Ko kuwa dai ban sani ba bacci ne ya ɗauke ni sai na soma mafarkinsa? Amma dai tabbas na gansa da idona sai dai irin wannan tunanin bai taɓa zuwar min ba.

Cike da tsoro na ƙara kwanciya na lumshe idona zuciyata na ci gaba da matsanancin bugawa.Wannan karon jinsa na yi dab da ni har muna jin hucin juna kai kace hatta gangar jikinmu na tare da juna ne,nan kuwa iya esprit ne.A hankali na ɗaga idona na kalle shi,yadda yayi wani tsaye ƙiƙam a gabana duk ya kere ni kamar Giwa da ɗan tsako.

"Yanzu kuma wannan mene ne da ka jawo ni cikin tunaninka?" na tambaye shi.
Cike da shaƙiyanci yasa hannunsa mai sanyi ya wani matse haɓata tare da ɗago ta ya ce,"ni kike yi wa magana haka? Sa'anki ne ni? Wato ni ne ma na shiga tunaninki? Kin zata ban gane ba? Ke ce kika shigo tunanina,na lura tun da kika zo gidan nan idonki na kaina duk kin bi kin takura ni kin hana ni saƙat,faɗa min wa ya aiko ki?"

Cike da jin haushi na sa dukkan hannuwana na tura ƙirjinsa sai dai ko gezau bai yi ba,shi ma tuni ya hassala sai ya kama hannuna ya murɗe har sai da na saki ƴar ƙara na soma fizge-fizge amma ya ƙi saki na.

"Duk shegen kinibibinki ne ya jawo miki halin da kike ciki amma ko kaɗan ba ki cancanci samu wannan power ba,sam ban ga ma dalilin da yasa ƴar aike ta mallaka miki mahaɗin ƙarfin ikona b..." ban bari ya kai ƙarshen aya ba na gantsara masa cizo a ƙirji da wani mugun sauri ya sake ni tare da ja baya ,daidai nan ni kuma na tashi zaune tare da buɗe idona fayau.

Saitin hannuna na duba inda ya murɗe sai na ga yayi ja sosai tamkar a zahiri ne ya riƙe ni ɗin,ƙin komawa na yi na kwanta sai na ci gaba da zama tsakiyar su Lubna da tuni sun yi bacci.

Ina nan zaune na ji handle na motsi ,kafin kuma ƙofar ta buɗe kanta ƙiiiii sai dai ban ga kowa

wanda ya shigo ba.Wani irin tsoro ne ya kama ni ,sai nake ganin kamar Maheer ɗin ne zai shigo a zahiri.

“Haule!” na ji muryar da har na koma ga Allah ba zan taɓa mantawa da ita ba ta kira sunana cikin wani irin yanayi.
Na soma waige-waige kafin na ce “Husseina? Husseina ke ce? ” ba ta bani amsa ba,sai jin wani abu na yi cikin iska ya kama hannuna yana jana sai kawai na sauko daga shimfiɗar na soma take mata baya duk da kuwa idona bai ganinta.

Da muka ratso falo haka ƙofarsa ita ma ta buɗe kanta,haka ma ta ƙofar gida.
Muna fitowa sai Husseina ta bayyana a gare ni,tana sanye cikin farin likafaninta har izuwa yanzu kuma kukan jinin take.

Kan dakali ta ja ni muka zauna kafin ta ce “Haule sai yaushe za ki kuɓutar da mu daga cikin ƙangin da muke ? Har yanzu ba ki samo mahaɗin sirrin tarwatsa BAƘIN RUHI ba?”

Jikina banda rawa babu abin da yake yi,na ce “ta ya aka yi kika zo nan? Kuma me yasa kika fito da ni waje? Ai sai ki yi min magana a can ɗakinmu”

Ta ce “in muna cikin gidan nan idonki ba za su taɓa gani ba Haule,amma na tambaye ki wane ne kike so har haka wanda ya mantar da ke dalilin zuwanki ƙasar nan?”

“So kuma? A'a ni ban son kowa” ban ida rufe bakina ba Husseina ta ɓace ɓat,cike da mamakin ta ya za ta tafi ba ta yi min sallama ba na miƙe da niyyar shiga gida sai dai kuma na tsaya cak sakamakon ganin mutum tsaye a gabana fuskar nan tamau fiye da kullum.Wani irin mugun tsoronsa da shakkarsa ne suka yi min dirar mikiya musamman da na gansa da kayan jikin nan irin na tunanina.

“Da wa kike magana?” ya jefo min tambayar cikin tsawa kamar wani ubana.

Mayafin jarumta na aro na yafawa kaina na ce “da kai mana”

Ya waro ido kafin ya ce “ke kar ki raina min hankali da ni kuma?”

“Eh to wa ka gani a nan bayan mu biyu?”

“Me kika fito yi to?”

“Abin da ka fito yi” na basa amsa kai tsaye tare da yin gaba sai dai ƙofar a rufe take ruf.Na juyo

na dube shi,sai na ga yana wani miskilin murmushi kafin ya ce “ina ce dai fatalwa ce ta fito da ke waje? To ki ce ta mayar da ke in tana da izzar zama a inda nake” yana gama faɗar haka sai ya zo yana tsayuwa ƙofar ta buɗe kanta na yi wuf zan shige amma tuni ta rufe shi kuma ya shiga ciki.

Tsoro ne ya kama ni,cikin magiya na ce “don Allah Alhaji ka buɗe min ”

Banza yayi da ni duk da kuwa da ina jin alamun tsayuwarsa bai tafi ba.Hadari ne ya soma haɗa kansa haɗi da tsawa da walƙiya,nan tsorona ya ninku don kuwa duk jarumtata ban son ruwan sama su dake ni.

“Ki faɗa min da wa kike magana sai na buɗe miki ” na tsinkayo muryarsa.

Cikin kukan da ya fara zuwar min na ce “ka buɗe min na yi ma alƙawari zan sanar da kai” ai kuwa ya buɗe ƙofar ina shiga na baza a guje na nufi can ƙofar da za ta sada ni da babban falo.

Cak na tsaya ina waro ido saboda wani jaririn maciji da ya sarkaye handle ɗin ƙofa,ina juyawa kuma sai na hangi Maheer yana takowa izuwa inda nake.Timmm na ji ƙarar faɗowar macijin kafin ya fara yin silululu yana tawowa,a mugun firgice na yi baya tare da rugawa na tarbo Maheer ɗin na koma bayansa tare da ƙanƙanme shi ina kuka ashe gudun gara na yi na faɗa gidan zanzaro shine mamallakin macijin.

“Sahut!” shine furucin da yayi kafin macijin yayi tsalle ya ɗale kafaɗarsa hakan ya baiwa bindinsa bugun fuskata nan take na yi luuu zan faɗi da sauri ya juyo tare da taro ni sai dai muna haɗa ido da macijin igiyar saita numfashina ta katse ban ƙara sanin abin da ke faruwa ba sai da na ji muryar Hajiya a kaina tana cewa “ka ƙi faɗin abin da ya same ta,sannan ma wai me ya kawo ta ɗakinka? Maheer me ka yi wa ƴar mutane?”

Wani irin sarawa kaina yayi jin wani batu wai ɗakin Maheer ,ban shirya ba na buɗe idona tarau ai kuwa a ɗakin nasa nake kwance kan bed ɗinsa abin da ya fi ɗaga min hankali bai fi yadda na ji duk ƙamshin jikinsa ya dabaibaye ni ba.

Muna haɗa ido da Hajiya ta yi saurin matsowa “Haule me kike yi ɗakin Alhaji?”

Shiru na yi don kuwa sam na kasa tuna komai da ya faru ciki kuwa har da zuwan Husseina,abin da na sani dai shi ne ina kwance a ɗakinmu Lubna ta gama bamu labari.

Maheer ɗin na kalla wanda shi ma ni yake kallo da idonsa da suka kaɗa suka yi ja kamar tsohon maye.
Hajiya ta mangare ni cike da masifa ta ce “don ubanki ba za ki faɗa min abin da kika zo yi

ɗakinsa ba?”

Shaaa hawaye suka fara yi min zuba,don sai yanzu ma ne nake ganin illar wanzuwata a nan uwa uba kuma ni kaina ban san ta ya aka yi na tsinci kaina a nan ɗin ba.

A karo na biyu na juya na dubi Maheer,Hajiya ta buɗe baki da niyyar yin wata masifar iya sunana kawai ta furta Maheer yayi wata irin busa mai ratsa dodon kunne sai ta yi shiru tana mai cewa “In Haule ta gama gyara maka ɗakin ta je ta shirya don Allah kafin su Lubna su gama saka kaya a mota” sai kuma ta fice.

Ya juyar da kai gefe ya ce “ki tashi ki koma ɓangarenku”

“Amma Alhaji me ya kawo ni nan?” na yi tambayar wasu sabbin hawaye na ƙara zubo min. “Dalla Malama saukar min daga gado,ban sani ba ki je ki tambayi fatalwar da ta kawo miki ziyara” ya faɗa a hassale.

“Fatalwa kuma?” na yi tambayar,ya zo da ƙarfi ya wani fizgo ni na faɗo daga gadon amma sai na yi saurin miƙewa ina jin tsanarsa na ƙara ninkuwa a raina.Idona har wani rufewa suke na nufi ƙofar fita,da na ratsa falonsa ne idona ya sauka da duwatsun awarwarona nan ma mamaki na yi,na duƙa zan kwashe su amma tamkar yadda iska ke ɗaga leda haka duk suka tashi sama suka yi bayana,sai na juya nan na ga ashe shi ne yayi amfani da siddabarunsa ya janye su.

Hannuna na duba na ga yayi ja alamun an yi wa wurin mugun riƙo,ban tanka shi ba na fita.Ina fara taka step na ga Lubna a tsaye tana kallon benen wanda yake ɓangaren Maheer ne,a cikin idonta nake hango wasu abubuwa da suka haɗa da zargi da kuma mugun kishi amma ban kula ta ba na wuce part ɗinmu.

Sai da zan shiga toilet ne na lura doguwar rigar baccinsa a jikina,na kwance ɗaurin na jefar da rigar amma abin mamaki sai ta ƙi taɓo ƙasa.

Ban san lokacin da na furta “matsafi kawai” sai kuma na ɗauki rigar na ajiye ta cikin jakar kayana.Bayan na shiga toilet na cire kayan jikina,ina wanka amma ƙamshinsa ne ke tashi.Bayan na gama wanka na zo na gabatar da sallar asubah wacce ta wuce ni don tuni ƙarfe bakwai ta buga.

A gaggauce na kimtsa cikin kaya masu kyau sannan na ɗauki rigar da nake ɗorawa a sama mai sunan Hajiya da kuma restaurant ɗinta.

Ko da na fito tuni an jera komai a mota,cike da ladabi na gaishe da Hajiya .Yadda na ga Lubna na kauce min yasa ban takura ta ba akan sai mun yi magana,a yau tare da Aliya za mu je a nisa umarnin Hajiya hakan yasa muka shiga mota muka wuce can.

Bayan an gama jera komai a wurinsa sai kuma na fito nan inda ke teburan cin abinci na ƙara gyarawa,babu jimawa kuwa mutane suka fara zuwa Aliya ta dinga taya ni aikin har muka samu ƙafa ta ɗan tsana sai na zuba abincin da za mu ci,sai kuma a lokacin na dube ta da kyau na ce "Aliya don Allah me ya faru a jiya a gidan Hajiya na kasa tuna komai,kawai dai na tashi na tsinci kaina a ɗakin Alhaji "

Dama tun tuni na lura ita ma da magana a bakinta,kawai dai ta yi shiru ne.
Aliya ta ce "to mu dai mun tashi ba mu gan ki ba,shine Anty Lubna ta je ta sanar da Hajiya ita kuma tana shiga ɗakin Maheer don sanar da shi ta tarar da ke a gadonsa kina bacci sai ta yi kururuwa duk muka haura sama kafin kuma mu iya cewa wani abu shi Alhajin ya fito daga wanka dole muka fita waje saboda mugun kallon da watso mana.Amma ni ma ban san me ya faru ba,na dai ji Anty Lubna na cewa kin ci amanarta kin je ɗakin Alhaji alhalin kin san tana sonsa,kuma wai don kawai ta yarda da ke ne shi yasa jiya ta bamu labarin cewa sperm ɗinsa ne ta kai a madadin na Dr David "

Kaina ne na ji yayi wata irin sarawa,ɓacin rai ya ƙara dirar min.Tsakanin jin sperm ɗin Maheer ne Lubna ta yi amfani da shi,da kuma jin zargin da take min sai na rasa wane ne ya fi yi min ciwo.

Abincin na ji ya fita raina,na miƙe na wanke hannuna.Kuka nake son yi don samu salamar zuci sai dai ina fitowa idona yayi tozali da wata mai ciki tana aman jini duk ya ɓata teburin da ke gaban kujerar da take zaune,hankali tashe na nufe ta sai dai tana ɗago idonta na tsaya cak sakamakon abin da ya gigita ji da ganina.....

My book is only 500 amma na yi discount daga yanzu zuwa kafin na saki page 10 ta ƙarshen free.ki tura 300 ta wannan account 2670215530
ZULFAU YAHAYA
ECOBABK sai ki turo min da shaida biya +22795045822

Wacce ba ta shirya ba don Allah kar ta yi min magana
[23/05 11:29] MRS SADAUKI: *BAƘIN RUHI*🧌🐲

```LoVe aNd HoRrOr story```👽
```

By
Chamsiya Laouali Rabo
{MRS SADAUKI💫✍️}

*SADAUKARWA :* Ga dukkan iyayenmu MATA da suka tsaya tsayin daka don bamu kariya a kan dukkan wani da ke son cutar da mu.

*FCWA*☀️

---

Last free page 10

Fuskarta ta yi wani irin ja kamar za ta tsage jini ya zubo,ga idonta da suke baƙi ƙirin sam babu hasken nan.Bakinta kuma jini ne shaɓe-shaɓe yana mai ci gaba da ɓulɓulo mata.A kallon tsanaken da na yi mata duk ta yi gudu ba za ta haura shekara ashirin da biyar ba,sam kasa cira ƙafata na yi daga inda nake sai ita ce ta yunƙura ta taso ta zo tare da zubewa gabana.Yatsun hannunta na taɓa ƙafata na ji wani irin yanayi ya ratsa ni,yanayi ne wanda na taɓa shiga irinsa lokacin baya shi ma ba zan taɓa mata wannan mummunar ranar ba.

Yawun bakina ne na ji sun fara taruwa da kansu kafin su soma ɗiga suna sauka kanta tamkar ana zubar da ruwan pampo ko kuma ana yayyafi.Zafin hucinta da fitar numfashinta shi ya cika wurin tamkar wacce ake zarar ranta,ƙila shi ya jawo hankalin Aliya ta fito daga can ɓangaren ta zo nan.

“Ƙwayar cutar BAƘIN RUHI,Haule ki ja baya mana contact da ke yana iya haifar da tsayawar numfashinta” Aliya ta faɗa tana mai jawo ni baya,sai a lokacin na ji wani irin raɗaɗi a ƙafata daidai wurin da ta ɗora yatsun hannunta da na kai duba wurin sai na ga tamkar an zuba min acid ne tuni ya wani kumburo ga wata uwar azaba da nake ji.

Na yi baya na samu kujera na zauna,yayin da Aliya kuma ta soma juya hannunta mai ɗauke da ƙarfin iko na power nan take ya kawo haske tare da bayyanar da wani dunƙulalen haske sai ta cillawa wannan mai cikin shi sai ya zagaye ta  sai a lokacin ta nufo ni ta tsuguna ta kamo ƙafata.

Hankalinta na ga duk ya tashi,ni kuma na ce “kar ki damu zan warke hakan ya taɓa faruwa da ni ai.Amma me yasa kika jefa mata wannan hasken?”

“Ɗaure ta ne na yi ta yadda ba za ta iya motsawa ba,haka shi ma dafin jikinta zai tsaya da aiki don yana dab da raba ta da rayuwarta.Yanzu dai bari na naɗe miki ƙafarki,sai mu tattauna yadda za a warkar da wannan baiwar Allah ”

Wani tissu ta samu ta ɗaure min ƙafa,na tashi tsaye kan ƙafafuna ina kallon mai cikin wacce ta zama kamar gumki ta kasa motsi.

“Mene ne ke damunta Aliya?”

“Ya za a yi mu samo maganin cutarta ita ce tambayar da ya dace ki yi Haule,kar ki bari kuskuren da kika yi baya ya sake maimatuwa ” ina jin furucin da Aliya ta yi sai na yi saurin dubanta,ta jinjina kai kafin ta ce “na san antynki ai,kar kuma ki tambaye ni ta yaya yanzu mafita za mu nemo kuma ke ce za ki jagoranci tafiyar”

Na ja wani gwabron numfashi kafin na ce,“dole sai na samu labarin mafarin abin da ya haifar mata da wannan cutar”

Shiru Aliya ta yi kafin ta ce “in haka ne muna da buƙatar madubi ko da ɗan guntu ne”

Ban kai ga yin magana ba aka shigo,Lubna ce da sauri na nufe ta sanin kullum tana yawo da madubi a jaka.

“Yawwa don Allah ki bamu aron madubinki” na faɗa .

Inda mai cikin take a durƙushe ta duba kafin ta zuge zip ɗin jakarta ta miƙo min,sai na je  kusan Aliya na tambaye ta “ya za a yi yanzu?”

“Ki je saitin idonta ki haska madubin za ta yi magana sai mu ji” cewar Aliya .
Dukka mu ukun muka yi tsaye,suka saka ni a tsakiya yayin da na daidaita madubin ita kuma Aliya ta yi amfani do powerta ta ɗago kanta sai a lokacin na yi mata magana “Wace ce ke? Mene ne dalilin shigarki wannan halin?”

“Sunana Meelat,ƴa ga masu matsakaicin hali,ba mu da kuɗi amma muna da rufin asiri.Na yi karatuna a makarantun gwamnati har Allah yasa na kai matakin University,ina shekara ta biyu yanzu haka.Tun zuwana can na ga yadda rayuwar jami'a take yadda ake challenge ɗin sutura da kuma wayoyi.To dama tun can farko ina sha'awar rayuwar luxery,ina da babban burin shiga mota ,zuwa gidajen cin abinci na manyan mutane da sauransu.Kwatsam wata rana na fito daga

jami'a zan je wurin gyaran gashi wata rantsatsar mota ta parker a gabana,a hankali ya sauke madubin motarsa wanda yake baƙi ƙirin ɗin nan.Wani babban mutum ne na gani cikin shiga ta alfarma,fari ne shi tasss mai kyau mai gayu wannan yasa ban wani ja aji ba da ya nemi ya rage min hanya.Sam ban yi duba da ya haife ni ba ko kuma kusan yin jika da ni ba,abin da ke gabana kawai kuɗi.Shi ya biya kuɗin da aka gyara min gashi da aka gama min kuma na kira shi ya zo ya ɗauke ni kamar yadda ya buƙata ya bani lambar wayarsa.Kafin ya mayar da ni can jami'a sai da yayi min shopping kuma ya faɗa min ƙudirinsa na sona yake,nan fa muka fara soyayya ko sau ɗaya bai taɓa kai hannunsa jikina ba tsawon watanni uku muna tare kuma komai nake so yana yi min.Ni da ƙawayena mun mayar da shi atm ɗinmu,a takaice dai sai da muka kwashe wata biyar kafin ya gayyace ni gidansa ya ce yana yin birthday na zo mu yanka cake sai na koma sannan kuma sai na duba gidan in yayi min nan zai ajiye ni in mun yi aure .Haka na je can gidan nasa mai kamar aljannar duniya inda ake parker motoci ma kawai abin kallo sannan akwai motoci iri-,kamar baƙauya haka na yi ta kallon har muka wuce can falonsa ashe ban ga komai ba don cikin ya fi haɗuwa.Ya nuna min kujera ya ce na zauna zai yi sallah ya dawo.Duk da a lokacin bai wuce ƙarfe biyar na yamma ba amma ban tambaye shi sallar mece ce zai yi ba kawai abin da na ɗauka mutum ne mai addini.

Daga inda nake a zaune ina ɗan jin sautin muryarsa yana karatu,amma dai ba na Alkur'ani ba ne cikin wani yare ne yake yinsa.Kamar minti goma haka sai ya fito jikinsa sharkaf da gumi har goshinsa na ɗigar da zufa,hankali a ɗan tashe yake cewa “babyna zo! Taso zuwa gare ni, please ina son ki yi min wani taimako ni kuma na yi miki alƙawari zan mallaka miki key ɗin mota da gida da duk abin da kike so.Lokacin da yayi wannan furucin na yi tunanin sex ne zai nema wurina sai duk ban damu ba don na taɓa yin aure ballantana na ji tsoron rasa budurci kuma a shirye nake na biya masa buƙatarsa duba da hidimar da yake yi min,nan take na ce masa na amince in dai gaske zai ban motar.Sai ya kama hannuna muka shiga ɗakin nan da ya fito,babu komai a ciki sai wani ƙaton akwati a tsakiya yana buɗe shi na yi tsalle na ja da baya .

Ba komai ne cikin akwatin nan ba sai gawar wata mata har ta bushe da alamu ta jima da mutuwa.Jikina ya ɗau kyarma,sai ya soma kwantar min da hankali yana cewa “kar ki wani damu baby kawai ciki za ki shiga kwanta na tsawon minti ɗaya kacal sai ki fito.

Soyayyata da abun duniya yasa na yarda na kwanta a tsorace,kamar yadda ya faɗa ɗin kuwa babu jimawa na fito sai ya bani maƙudan kuɗi waɗanda ni kaina ban san yawansu ba kuma ya mallaka min ɗaya daga cikin motocinsa da kuma gida.Tun bayan da na koma can in na kira shi wayarsa ba ta shiga,da farko ban damu ba sai satin da ya wuce da na soma ganin cikina na kumbura yana zama ƙato in kuma na yi tari sai jini yayi ta ɓulɓulowa na yi yawan asibiti har na gaji amma likitoci ba su gano abin da ke damuna ba.Har gidansa na je amma yana rufe da ɗan kwaɗo ,maƙwabtansa kuma sun ce yayi tafiya.Yanzu ma daga can nake saboda na ji labarin yau zai dawo amma kuma bai zo ba,da zan wuce ne na tsaya don in ci abinci saboda yunwar da nake ji sai kuma na soma yin tari hadi da aman jini” tana kawowa nan na tashi daga gabanta.

Ina mai kallonsu,Aliya ce ta soma magana “ina ga yayi amfani da jininta ne don bunƙasa arzikinsa ”

Lubna ta karɓe da cewa “a'a bana tunanin domin kuɗi yayi hakan,don in don su ne to zai nemi yayi sex da ita ne ko kuma ya nemi ta basa jinin period ɗinta tabbas sai dai don wata manufar”

Bayan duk na saurari jawabansu sai na ce “in dai ba don kuɗi ne ba to tabbas da buƙatar mu je can gidan nasa”

“A'a zuwa gidansa ba shi ne mafita ba,neman taimakon ƴar aike dai ya kamata mu yi” cewar Aliya tana dube-dube.
Na ce “wace ce kuma haka ?” ba ita ta bani amsa ba,Lubna ce ta ce “duk wata power ko ƙungiya akwai shugabanta Haule ”

“Ina za mu samu tukunyar laka?” Aliya ta tambaya.

“Ko a kasuwa za a samu,me za a yi da ita?” na tambaya.

“Ku fito mu je kafin wasu costumer su zo .Haule rufe ko ina,mu tafi” Aliya ta faɗa ,duk yadda na so yin tambaya kuma Lubna ta hana haka muka rufe restaurant muka nufi kasuwa tukunyar lakar muka saya kafin kuma Aliya ta ja mu can wani guri mai ƙazanta.

“Ku rufe idonku ” ta bamu umarnin da na so yin gardama amma tuna halin matar da muka baro yasa na yi yadda ta ce.
Wani irin hayaƙi na ji ya turnuƙe min hanci yayin da Aliya kuma ke karanto wasu abubuwa maras kan gado.Yanayin yadda iskan shaƙata ya canza yasa na buɗe ido,cikin wani ƙasurgumin daji ne muke duba da labarin da Lubna ta bamu sam ban yi mamakin hakan ba.

“Wannan shi ne ƙasurgumin dajin AOKIGAHARA,ana yi masa laƙabi da dajin fatale da dodanni.Duk wani da ke son kafa ƙungiyar asiri to dole sai ya biyo ta nan domin samun albarka aljanai da kuma tabarakin manya-manyan mashahuran matsafa waɗanda suka taka rawar gani wurin zalunci.Kamar yadda kuke gani dajin ya rabu biyu, wannan shi ne tafarkin haske masu kula da fararen ruhika kuma masu kyautar ƙarfin iko na power,to mu can ne za mu je” Aliya ce ta yi jawabin tana mai nuna mana wata ƙofa wacce wani ƙaton icce mai kan mutum ya raba tsakanin hanyoyin biyu ta sharri da kuma ta khairan.

“Kina nufin BAƘIN RUHI ya samo asali ne daga wannan hanyar kenan?” na tambaye ta ina mai nuna ƙofar wacce ke cike da tarnaƙin hayaƙi da duhu.

“Wannan amsar ai ke za ki bamu ita Haule saboda maɗaukakiyar ceto da ke a jikinki” Aliyar ta

faɗa tare da yin gaba,muka take mata baya ina mai juya kalmar ni ce ke ɗauke da maɗaukakiyar ceto a jikina.

Can cikin muka lula kafin mu samu wani keɓaɓen wuri mu zauna,ni ce a tsakiyarsu kamar yadda Aliya ta ce na yi.Bayan duk mun zauna sai muka ajiye tukunyar lakar a tsakiyarmu,yawun bakina na tofa a ciki sai wani irin haske ya soma bayyana daga can ƙasan tukunyar .Gaba na ɗan yi  da fuskata na leƙa ciki,da wani mugun sauri na dawo baya sakamakon fuskata da na ga ta rabu biyu.Ɓangaren hagu fuskar Maheer ce yayin da bangaren dama kuma yake tawa,ban san me hakan ke nufi ba sannan kuma ban tambayi Aliya ba wacce tuni ta soma kiran sunaye barkatai sam ban aje hankalina sosai ba tunanin Maheer ne ke yi min yawo a zuciya.

“Ban san mene ne matsalar ba ƴar aike ta ƙi bayyana a gare mu,Haule ko da wani saƙo da aka isar miki zuwanmu?” tambayar nan da Aliya ta yi min ya katse min tunanina,na girgiza mata kai na ce “a'a babu wani saƙo da aka isar min”

Yanayin fuskar Aliya ya nuna rashin jin daɗi,sai ta miƙe ta ce “ku tashi mu tafi ba za ta zo ba,ban san kuma me yasa ba” haka muka fito daga ɓangaren ba tare da na yi tunanin cewa hoton da aka nuna min na fuskata ta tsage gida biyu sannan ta haɗe da ta Maheer shi ne makullin nasarar da muke tunkara ba.

Da muka fito Lubna ta ce “ amma Aliya ita wannan hanyar fa? An hana a shiga ne ko da haɗari?”

“A'a ko ɗaya,sai dai ita tana da sharuɗa ne masu tsauri shi yasa ba kowa ke son shiga ba.Kin ga muddin mutum ya shiga to ko ya ga abin tsoro bai da ikon yin ihu ko ƙara,sannan duk abin da za ka gani iya kallo ɗaya ne kacal za ka yi masa ka ɗauke idonka a kai,sannan ko ƙasar cikin wurin ba a yarda ka ɗebo ba ballantana furanni ko wani abu da ke ciki” Aliya ta faɗa .

“Haule zo mu je mu shiga mu gani ko ba komai za mu ƙara ilimi”Lubna ta faɗa tana wani kamo hannuna,haka kawai na ji gabana na dokawa amma na daure na yarda muka shiga .

Tun a bakin ƙofa wani irin iska mai zafi ya dake min,kuma tamkar an zuƙo mu ne ba tafiya muka yi da ƙafafuwanmu ba haka na ga mun yi saurin shiga tsakiyar wurin.Wuri ne mai cike da furanni masu tsantsar kyawu wanda ya ɓoye sharrinsu da kuma gubar da ke ɗauke da shi.Muna tsaka da tafiya muka dinga jin kukan jarirai,Aliya ce ta yi mana bayanin dalilin kukan.

“Dayawan matan da suka rasa rayukansu suna ɗauke da ciki su ne in sun shigo nan suke haife

cikin,wani sa'in jariran na rasa madarar da za su sha ne to in sun ji ƙamshin bil'adama ne sai su fara kuka.In da mace mai shayarwa to haka za ki ga madara na ta ɗiga daga mamanta tana shigewa ƙarƙashin ƙasa" ina gama jin bayanin nan sai wani tsoro ya kama ni,duk gani nake ni ma hakan na iya faruwa da ni duk da kuwa ni budurwa ce.

Wajen wani koren fure muka ratsa sai ya soma yin rangaji yana motsi tamkar wani mai rai,Lubna ta kai hannu za ta tsinko amma Aliya ta buge hannun tare da cewa " ba ki ji na ce ba a taɓa komai ba?"

"Na manta" ta faɗa tana dariya.

Sai da muka yi yawo sosai kafin mu kamo hanyar fita,nan ne na ji tamkar na taka wani abu mai motsin rai.Ina ɗaga ƙafata sai na ga wata sarƙar diamond mai shegen kyawu sai ƙyalli take,kallo ɗaya na yi mata ina shirin kawar da idona amma wani abu ya ja hankalina a tsakiyar sarƙar harafin H ne aka zana sannan ga wasu duwatsu masu kaloli da aka ƙawata harafin.

Na duƙa na kai hannu na ɗauki sarƙar,ko da na ɗago sai na ga tuni su Lubna sun kai bakin ƙofa.Kamar wacce aka yi wa dole haka na saka sarƙar a wuyana tare da gyara ɗan ƙaramin hijabina sannan na ɗan ruga na cimmar musu.

Ko da muka fito waje sai Aliya ta ƙara mayar da mu can wurin nan mai datti.
"Yanzu ya za a yi kenan?" Lubna ta tambaya.

Aliya ta ce "mafita guda gare mu a yanzu shi ne mu je can gidansa"

Kamar wacce aka tsikara na ce "na san gidan" duk suka kalle ni da mamaki,amma tun da abin da suke so ne kawai ba su tambaye ni ta yaya ba sai muka ɗau taxi ni ce na dinga nuna masa hanya har muka isa gidan.

Bayan mun sallami mai taxi muka fito muka yi cirko-cirko,unguwar tsit take sosai ma na yi mamakin ta yadda aka yi Meelat har ta iya ganin maƙwabtan Alhajin.

Aliya ce ta soma juya hannunta mai power ta ɓalle kwaɗon da aka rufe gidan da shi,su biyun duk suka shige ciki yayin da ni kuma na tsaya ina kallon wata matashiyar budurwa wacce ke zabaya tana leƙena ta wata can saman benen ɗaki.

'Wace ce ita kuma waccan mai farar fata kamar fulawa?' na tambayi kaina a zuci,ban kai ga samo amsa ba na ji kururuwar su Lubna daga can cikin gidan.A guje na nufi ciki sai na tarar suna gurmuzu su da wani gogon Biri duk yadda Aliya ke da power ta kasa tsayar da shi domin shi ma an tsafe shi.Abun mamaki ina shigowa sai ya tsaya cak tare da zubewa ƙasa yana wani irin abu kamar yana gaishe ni,ƴar kallon-kallon muka fara yi mu ukun .

“Haule ke ma irin wannan protector ɗin gare ki? Na ga duk jikinsa yayi sanyi” Aliya ta yi min tambayar da sam ban ma gane mene take nufi ba hakan yasa na share ta na ce “ga ɗakin akwatin gawar nan” na nuna musu shi da yatsa sai suka nufi ƙofar yanzu ma Aliya ce ta buɗe ta.
Sai bayan sun shiga na take musu baya ina mai waiwayen Birin da har zuwa yanzu yana a yadda yake.

Kiciniyar buɗe akwatin suke amma sun kasa,don power Aliya ma ta ƙi yin aiki.Sai na zo na kama musu amma ta ƙi buɗuwa,Lubna ta ce “ina ga akwatin nan jini ne makullin buɗe shi”

Duk sai muka kalle ta,kai ta jinjina ta ce “wannan tambarin Family ne” ta nuna wani logo da ke jikin akwatin.

“To jinin wa za a tsaga?” na yi tambayar.

Aliya ta ce “in dai haka ne da na Lubna za a yi amfani duba da ta taɓa zama cikin ƙungiyar,na san har zuwa yanzu zanen hannunta bai goge a rubutun da suka yi ba” sam ba mu yi tunanin wannan babban kuskure ne za mu tabka ba,haka Lubna ta tsaga yatsanta ɗigon jininta ya ɗiga sau uku a jikin tambarin nan take akwatin ya soma buɗe kansa a hankali wari da ɗoyi yasa suka ja baya,yayin da ni kuma na toshe hancina tare da matsawa ina leƙen akwatin.Yana gama buɗewa na ji an tunkuɗa ni ciki na faɗa yayin da kuma akwatin ya rufe ruf da ni a ciki.Cike da tashin hankali na soma kiciniyar buɗe shi amma ya ƙi yi,ina jin muryar Aliya kuma na cewa Lubna “don me kika yi haka? Yanz...” ban ji ƙarashin maganar ba sakamakon ƙanƙame ni da gawar ta yi tana yi min maganar da ta birkita lissafina.Daidai nan free page ya ida in kina son ci gaba sai ki tura 500 via2670215530
ZULFAU YAHAYA
ECOBABK sai ki turo min da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822

🔞Yanzu nake rubuta shi Ni ma banda complete in kin biya group ne zan saka ki
06.Apr.25